## دار السلام ← Darassalamu :

Allah ya sake tara mu a Darassalamu.

اللهم أجمعنا مرة أخرى في دار السلام .



www.alkottob.com

Allah ya ƙaddara saduwarmu a Darassalamu.

قدر الله أن يجمعنا في دار السلام .

## : Daraji ← درجة

Allah ya ɗaukaka darajarsu a cikin aljanna. رفع الله درجتهم في الجنة .

Bayi zasu ƙetare shi da gwargwadon darajar ayyukansu.

العباد يجتازونه بقدر درجة أعمالهم .

Kada a faɗi darajar sai kuwa ya ƙare bayyana.

لا تقل الدرجة حتى ينتهي الكل من الشرح .

Mutum ya kamata ya kula da abinci mai daraja a jikinsa.

يجب على الإنسان أن يهتم بالطعام المفيد لجسمه .

Daga nan daraja sarkin fada ta ragu wajen sarki.

من هنا نقصت منزلة رئيس القصر لدي الأمير .

Ina roƙo a cikin darajar mulkinka ka bar ni in yi 'yan kwanaki, kaɗan a nan. أسألك بعظمة ملكك أن تتركني أمكث أياما قليلة هنا .

Ya karya mini daraja. أنقص قيمتي .

Ya duba kayan ɗaki , ta ga duk an kwashe masu daraja.

نظرت إلى أثاث الحجرة ، فرأت أن كل ما أخذوه قيّم .

## : Darasi ← درس

Jatau ya koyi darasi. جاتو تعّلم درساً .

Kullum darasi ya faɗo a kan dabarun da ya kamata su yi.

دائما الدرس يكون على الحيل التي يجب أن يفعلوها .

Musa ya karanta darasi mai wahala. موسى قرأ درسا صعباً .

A ranar alhamis babu darasi a makarantu.

في يوم الخميس لا توجد دراسة في المدرس .

Kullum Isa ba ya makara a wajen darasi.

دائما عيسى لا يتأخر عن الدرس .



www.alkottob.com

## درع ← **Dir'i** :

القميص هو ما يُقال له الدرع .

Abin da ake ce wa dir'i shi ne riga.

## درهم ← **Dirhami** :

Ba yin zakka ga azurfa da yawanta bai kai dirhami dari ba.

لا يُزكي عن الفضة التي لم تبلغ مائة درهم .

Dirhami ɗari kuwa shi ne aukiya biyar. المائة درهم تساوي خمس أوقيات .

Ba ni ke dirhami. ليس عندي ولا درهم .

## دروة ← **Durwa** :

تأتي بمعني سترة

Mace ba ta durwa sai da dalili. لاتضع المرأة السترة إلا لسبب .

Amfanin da auduga ya hana mata yin durwa da tsumma.

فائدة القطن جعلت النساء لايتحفضن بالخرقة .

Musa ya yi durwa a bakin kogi. موسى عمل دروة على شاطيء النهر .

## دعاء ← **Addu'a** :

Zaka yi addu'a cikin sujjada in ka ga dama.

ادع في سجودك إن وجدت الفرصة .

Da ya yi sallama ya yi addu'a. عندما سلّم دعا .

Aka yi mana addu'a don kada shaidan ya sake wasa da zukatammu.

دُعِيَ لنا لكيلا يلعب الشيطان مرة أخرى بقلوبنا .

Ya yi masa kyakkyawar addu'a. دعا له دعاءً حسناً .



www.alkottob.com

## : Da’awa ← دعوى

Mun ji da’awa tasa yanzu mu ji taka. سمعنا دعواة الآن نسمع دعواك .

Wanda ake da da’awa a kansa ya ƙi rantsuwa.

من ادُّعِيَ عليه رفض القسم .

Na gyara masa da’awa tasa. غيّرت له دعواة .

Za’a yi da’awar kisan kai a kan wata jama’a.

ستقام دعوى القتل على جماعة من الناس .

## : Daftari ← دفتر

Na ga wani gyara a daftari. رأيت تغييراً في الدفتر .

Alkali ya yi rubuta a daftarin shari’a. القاضي كتب في دفتر القضاء .

Daftarin hukuma ba mai wasa da shi. دفتر الحكومة لا يُلعب به .

Na sayi sabon daftari. اشتريت دفترا جديدا .

## : Daƙiƙa ← دقيقة

Daƙiƙa sittin shi ne awa ɗaya. الستون دقيقة ساعة واحدة .

In na yi nutsu a cikin kogi na kan sami daƙiƙa uku kafin na ɗago.

إذا غطست في النهر أحتاج إلى ثلاث دقائق لأطفو .

Dayan ya fita da daƙiƙa biyu ka zo. جئتَ بعد أن خرج بدقيقتين .

## : Dala’ilu ← دلائل

Yana karatun dala’ilu. يقرأ في كتاب الدلائل ــ الخيرات .

’Yan aji biyu sun karanta dala’ilu bayan an tashi.

طالبان قرآ الدلائل بعد الانصراف .

Hamisu ya hardace dala’ilu. خامس يحفظ الدلائل .



www.alkottob.com

## : Dalili ← دليل

تأتي بمعنى سبب أو أثر

Ya kira shi ya tambaye shi dalili. ناداه وسأله عن السبب .

Yana so yana kashe ni , amma ya rasa dalilin da zai bayar.

يريد أن يقتلني ، ولكن عجز عن السبب الذي يتذرع به .

Ba su kula da tsabta ba , babu kuwa wani dalili sai jahilci.

لا يهتمون بالنظافة ، ولا يوجد سبب إلا الجهل .

Suka duba sai suka ga ba ayari ba dalilinsa.

نظروا فلم يروا القافلة ولا أثرها .

Da mijin ya shigo , ya ganta ta himmatu cikin saƙa amma ba zare ba dalilinsa. عندما دخل الزوج ، رآها همّت في النسج ، ولكن لا خيط ولا أثر له .

## : Dillali ← دلاَّل

التاجر المتجول

Im bai sami kuɗi ya yanka ba , sai ya zare turmi kan dillali.

إذا لم يجد مالا يسرق يسحب ثوب من فوق رأس الدلال .

Da gari ya waye sai ga dillalan doki sun zo karɓar kuɗi.

عندما طلع النهار جاء تجار الخيل لأخذ الثمن .

Ya ajiye rigunan da yake dillanci bisa teburin malam.

وضعوا الثياب التي يتاجرون فيها على مائدة المعلم .

## : Addini ← دِينٌ

Su ƙara lura da al'amarin addini. اهتموا كثيرا بأمر الدين .

Wannan niyya da ka yi , ita ce ake so ga addinimmu.

هذه النية التي نويتها ، هي المطلوبة في ديننا .



www.alkottob.com

Wannan babban zunubi ne ga addininsu. هذا ذنب عظيم في دينهم .

## دنيا ← Duniya :

Ba ni da kome a duniya sai warkin nan.

لا أملك في هذه الدنيا سوي هذا القميص .

Im ba ka yi hankali a duniya ba , sai ka wahala wata rana.

إن لك تتعقل في هذه الدنيا ستتعب يوما ما .

Yau kyanwa ta mutu , duniya ta yi daɗi.

اليوم ماتت القطة والدنيا صارت حلوة .

Na shiga duniya na sha ko wace azaba.

هِمْتُ على وجههي في الدنيا وذقت العذاب .

Daga nan sai a yi shirin kalaci , sa'an nan a shiga harkar duniya.

من هذا الوقت استعد بالطعام ثم بدأ عمله في الحياة .

Suna zaune kamar wata uku tare cikin jin daɗin duniya.

مكثوا حوالي ثلاثة أشهر معا يتمتعون بالحياة الدنيا .

Wannan ɗan duniya yau ya zo ya gama mu husuma.

هذا الشرير جاء وأوقع بيننا الخصومة .

Daga yau ba ka ƙara kukan abu sai fa in ka yi hankali na 'yan duniya.

من اليوم لن تبكي شيئا ، إذا اتقيت الأشرار .

## دولة ← Daula :

### تعني السلطة

Wannan littafi ya ƙunsa duk ayyukan zaruntaka da shiga daular sarauta. هذا الكتاب يشتمل على أعمال الشجاعة ، والدخول في سلطة الدولة .

Sarkin nan da uwarsa su dawo birni , tun da yake Allah ya ba shi daula haka. هذا الأمير وأمه عادا إلى المدنية ، طالما وهبهم الله الملك هكذا .

Suka riƙa yi masa ba'a har suka laƙaba wa yaron nan suna ɗandaula.

أخذوا يسخرون منهم حتى لقبوا هذا الصبي صاحب السلطة أو ابن الدولة .



www.alkottob.com

## : **Dawwami** ← دوَّم

Ya rabbi ka dawwami sarkimmu. اللهم أدم أميرنا .
Allah ya dawwami mulkinka. أدام الله ملكك .
Haske ya dawwami mulkinta , na tuba. أدام الله النور على ملكك ، تبت .
An hore ka da dawwamad da ƙasad da kai. أُمِرْتَ بمداومة الخشوع .
Allah shi ne ya halicci aljanna ya tanade ta gidan dawwama ne ga waliyyansa. الله هو ـ الذي ـ خلق الجنةِ وأعدها دار خلود لأوليائه .

## : **Diyya** ← دية

Arne kuma diyyarsa dirhami ɗari takwas ne. المجوسي ديته ثمانمائة درهم .
Aka biya masa diyya. دُفِعت له الدية .
Na biya diyyar waɗanda suka kashe duke. دفعت دية الذين قتلوا كلَّهم .
Suka halarci wajen yin rantsuwa game da diyyar kuskure.
حضروا حلف يمين الدية الخطأ .

## : **Dinari** ← دينار

Ta kawo dunari dubu ta ba shi. أحضرت الف دينار واعطته .
Ba'a fid da zaka ga dinarin da yawansa ya kasa ashirin.
لا تخرج الزكاة عن الدنانير التي لا تبلغ العشرين .
Abin da za'a ba ta , shi ne rubu'in dinari. ما ستُعطَى هو ، ربع دينار .

★★★



www.alkottob.com

# الـذال

## : Zati ← ذات

ذات الله سبحانه وتعالى

Suna lura a cikin hakikanin Zatinsa. يتفكرون في حقيقة ذاته .
Shi ya rinjayi al'arshinsa mai girma da zatinsa.
هو يعتلي عرشه المجيد بذاته .
Ya zantad da Musa da zancensa wannan da shi ke , shi ne sifar zatinsa. كلم موسى بكلامه الذي ، هو صفة ذاته .
Shi ne mai ƙaddarawar al'amurra da zatinsa. هو مقدر الأمور بذاته

## : Zarra أو Zarratin ← ذرّة

Ba ku kula da sha'anin Umma da na ɗanta ba ko misƙala zarratin.
لم تهتموا بشئون أمه وابنها ولو مثقال ذرة .
Wanda ya aikata aikin alheri ko da misƙala zarra ce zai gani.
من عَمِلَ عَمَلَ الخير ولو مثقال ذرة سيراه

## : Zira'i ← ذراع

Mustahabban taimama ambaton sunan Allah da gabatar da bayan zira'i kafin cikinsa. مستحبات التيمم ذكر اسم الله وتقديم ظاهر الذراع على باطنه .
Tsawonsa zira'i saba'in kaɗai. طوله سبعون ذراعا فقط .
Ya shafo zira'ar hannunsa na dama. مسح ذراع يده اليمني .



www.alkottob.com

## : Zuriya ← ذرّية

Bai bar zuriya ko guda ba. — لم يترك ذرية ولو واحد .

Har wa yau kuwa zuriyar bayin nan suke yin wannan hidima.

حتى اليوم وذرية هذا الخادم تقوم بهذه الخدمة .

Haka sunayen zuriyarku suke ? — هكذا تكون أسماء ذريتكم ؟

Ya zama tare da zuriyarsa. — يقيم مع ذريته .

## : Azzakari أو Zakari ← ذَكَرٌ

العضو التناسلي للرجل

Daga abubuwan da ke warware alwalla shafan zakari.

من الأمور التي تنقض الوضوء مس الذكر .

Farawa da wanke najasa sa'an nan azzakari.

البداية بغسل النجاسة ثم الذكر .

Boyan kan azzakari cikin farji yana wajabta wanka.

مغيب رأس الذكر في الفرج يستوجب الغسل .

## : Zikiri ← ذِكْر

Ana son zikiri bayan salloli. — يُستَحب الذكر بعد الصلوات .

Mai tafiya masallacin idi zai yi ta yin zikiri a sarari.

الذاهب إلى مصلي العيد يذكر الله كثيرا في الخلاء .

Zasu daina zikirin yayin da liman ya shiga salla.

يتركون الذكر عندما يبدأ الأمام الصلاة .

## : Zilla ← ذِلّة

تأتي بمعنى الذل أو الأذي

Karama bayan zilla. — العز بعد الذلة .



www.alkottob.com

In da kwaɗayi da wulakanci in kuwa ka haɗiye shi ba ka ganin zilla.

إذا وجد الطمع والاحتقار وتغلبت عليهما لاترى ذلة .

Kar ka dinga yi wa 'yan waɗansu zilla don kada a yi wa naka.

لا تؤذي أبناء غيرك حتى لا يؤذي أبناؤك .

In kana yi wa yaro zilla ba zai yarda ka ɗauke shi ba.

إذا كنت تؤذي الولد لا يرضى أن تحمله .

## ذَمٌّ ← Zambo :

Su sa maroka da makaɗa su yi mini zambo.

جعلوا المتسولين والطبالين يذمونني .

Shata yana cikin mawaƙan da suke iya zambo.

شاتا من الشعراء القادرين على الذم .

Idan mawaƙi ya tsane ka ba abin da zai yi maka . wanda ya fi zambo.

إذا كرهك الشاعر لا يستطيع أن يفعل لك شيئا أكثر من الذم .

## ذِمِّيٌّ ← Zimmiyi :

Ya yi sallama ga zimmiyi. سلَّم على ذِمِّيّ .

Wajibi ne ga musulmai su kare hakkin zimmiyi.

يجب على المسلمين حماية حق الذمي .

Shari'a ta yarda ka zauna da zimmiyi. الشريعة ترضى بأن تعيش مع الذمي .

## ذنب ← Zunubi أو Zamba :

Wannan babban zunubi ne ga addinimmu. هذا ذنب عظيم في ديننا .

Shi zai sha uƙuba sakamakon zunubinsa. سينال عقوبة جزاء ذنبه .

Ya tuna wani zunubi ne da ya yi mai girma shi ya sa shi kuka.

تذكر ذنبا عظيما عمله ، هو الذي جعله يبكي .

Ya aika Galma a shaida wa ubansa ga dansa an kama shi ya yi zamba.

أرسل إلى جَلْما فقيل لأبيه ، ها هو أبنه قبض عليه لأنه أذنب .

★★★



www.alkottob.com

# الـراء

## : **Ra'asan** ← رأسا

أي من الذاكرة

Har yau ban taba ba da labarin wani annabi ba , ko da suke duk ra'asan suke gare ni.

حتى اليوم لم أقص قصة أي نبي ، مع أنه كلها في رأسي أي في ذاكرتي .

Malam Musa babban malami ne , in ka zo karatu wajensa ra'asan zai biya maka. الأستاذ موسى عالم كبير إذا جئت لتتعلم لديه يعطيك العلم من الذاكرة .

Duk bin da na karanta , in ka tambaye ni shi zan kawo maka shi ra'asan. كل ما قرأت، إذا سألتني فيه أجبت عنه من الذاكرة .

## : **Ra'ayi** ← رأي

Mu duka uku ra'ayimmu ya zama ɗaya. نحن الثلاثة كلنا صار رأينا واحد .

Me ka gani game da wannan ra'ayin ? ماذا ترى بشأن هذا الرأي ؟

Kowa da irin ra'ayin da Allah ya yi masa.

كل له رأيه الذي هداه الله ـإليه ـ .

Kamar yadda mutane suke da yawa , haka kuma ra'ayoyinsu ya bambanta. كما أن الناس يكثرون ـ في عددهم ـ هكذا أيضا تختلف آراؤهم .

## : **Ru'uya** ← رؤيا

Wata ru'uyar gaskiya ce. بعض الرؤيا صادقة .

Yau na yi kyakkyawar ru'uya. رأيت اليوم رؤيا جميلة .

Yau na ga annabi a cikin ru'uya. اليوم رأيت النبي في الرؤيا .



www.alkottob.com

## : Rabbi ← رب

Ya rabbi ka dawwami sarkimmu. يارب أدم أميرنا .
Na yi roƙo ga rabbi don ya ƙaran buɗi. سألت الله ليفتح عليَّ .
Rabbana ya yi mana ruwa. اللهم انزل لنا المطر .

## : Riba ← ربا

Allah ya halatta ciniki, Kuma ya haramta riba. أحل الله البيع وحرم الربا .
Sayen azurfa da zinari shi ma riba ne, sai in ya kasance hannu da hannu. بيع الذهب بالفضة ربا ، إلا إذا كان يدا بيد .

## : Riba ← ربح

Akwai sana'ar da ta fi ta riba. توجد صناعة تفوقها ربحاً .
Ribar yau kuma ta wuce ka. ربح اليوم فاتك أيضا .
Ribar da zamu samu ga tasoshin nan ba ta da iyaka.
الربح الذي سنناله من هذه المحطات لا حدود له .
Wanda ya ƙwace dukiya ribarta ba zata halatta gare shi ba.
من اغتصب ثروة ربحها لا يحل له .
Noma a can yana da riba , amfaninsa kuwa kullum mai albarka ne.
الزراعة هناك مربحة ، وحاصلاتها دائما وفيرة .
Aka ba ni hakkina da ya riba wannan biyu.
أُعْطِيت حقي الذي زاد عن هذا مرتين .

## : Rubu'i ← ربع

In sun dawo sarki zai sam musu rubu'in daga cikin da suka samu.
إذا عادوا سيجعل لهم الأمير الربع مما نالوا .



www.alkottob.com

Ki nemo madara kamar rubu'in kwalaba guda.

أحضري لبنا حوالي ربع زجاجة واحدة .

Za'a fid da rubu'in ushuri. — سيُخرج ربع العشر .

Abin da za'a ba ta shi ne rubu'in dinari. — ماستُعْطي هو ربع دينار .

Zata gaji rubu'i. — سترث الربع .

## ربيع ← **Rabi'u** :

Dan autansu ana kiransa Rabi'u. — أصغرهم يُسمي ربيع .

Duk wannan abu ya auku day ga watan Rabi'u awwal ne.

كل هذا الأمر وقع في الأول من شهر ربيع الأول .

A cikin Rabi'u sani na wannan shekara zan yi aure.

في ربيع الثاني من هذا العام سأتزوج .

## رتب ← **Rattaba** :

تأتي بمعنى قال

Na kwashe labari duk na rattaba musu. — استجمعت كل القصة وقلتها لهم .

Ta rattaba mini yadda suka yi da ubanta. — قالت لي كيف فعلوا بوالدها .

Ya rattaba masa duk yadda suka yi da mai gidansa.

قال له كل ما فعلوه مع سيده .

Farka ya kwashe labarin biri da damisa duk ya rattaba masa.

استجمع التاجر قصة القرد والنمر وقالها كلها له .

## رجب ← **Rajab** :

Yin azumi ranar Rajab nafila ce. — صيام شهر رجب نافلة .

Zan tafi gida a cikin watan Rajab. — سأذهب إلى بلدي في شهر رجب .

Wata daya tsakanin Rajab da Ramalan. — شهر واحد بين رجب ورمضان .



www.alkottob.com

## : Raha ← راحة

Na ko gaya maka ba abin da ke ba ni raha illa ƙa ƙare labari.

قلت لك لا شيء يريحني إلا أن تنهي القصة .

Da na ce ko abin na raha ne har ina neman taimakonka.

ظننت أن الأمر مزاح حتى طلبتُ مساعدتك .

## : Rahama ← رحمة

Ya nema masa rahamar Allah. طلب له رحمة الله .

Allah ya yi masa rahama. رحمه الله .

Da ganinta sai hankalina ya tashi rahama ta rabu da ni.

عندما رأيتها ثار غضبي وذهبت عني الرحمة .

Ya ce ana dubansa da idon rahama. طلب أن ينظر إليه بعين الرحمة .

## : Araha أو Ruhusa ← رخص

Sun ga ya fi araha ne gare su. رأوا أنه أرخص لهم .

Wannan irin gishirin ke da araha. هذا النوع من الملح رخيص .

Ga shi ya sayad da akuya da araha. ها هو باع العنزة رخيصة .

## : Ridda ← رِدَّة

A kan kashe wanda ya yi ridda sai dai in ya tuba.

يقتل المرتد إلا إذا تاب .

Wanda ya bar yin salla don musun wajabcita shi kamar mai ridda ne.

من ترك الصلاة لإنكار وجوبها كالمرتد .

Bai yi ridda ba kuma ya yi iƙrari da salla. لم يرتد وأقر الصلاة .

## . Arziki ← رزق

Duk yawan arziki sarkin nan sai ya zama banza.

كل ثروة هذا الأمير صارت عبثا .



www.alkottob.com

Ni wannan arziki tun kaka da kakanni na gaje shi.

كل هذه الثروة ورثتها منذ الجد والأجداد .

Duk Ƙasan nan babu wanda ya fi mu arziki.

في كل هذه المدينة لا يوجد من يفوقنا ثروة .

Kafin shekara guda Sule ya zama mai arziki.

قبل عام واحد صار صالح ثريا .

Tabarakalla lalle mai arziki yana biki. تبارك الله لابد أن ثريا يقيم عرسا .

Mene ne sadakin auren mai arziki irinka. ما صداق زواج ثرى مثلك .

Ga abuyata tana roƙon arziki ta zauna. ها صديقتي ترجو أن تقيم .

Ga shi yana roƙo ni arziki yana sonka. ها هو يرجوني ، إنه يريدك .

Suka durƙusa duk gaba daya suna roƙonsa arziki ya taimake su.

ركعوا جميعا معاً ، يرجونه أن يساعدهم .

Ina roƙonka arziki ka bar ni. أرجوك أن تتركني .

Zai tanka masa , su yi rashin arziki , na hana shi.

سيرد عليه ، ويتشاجران ، فمنعتهم .

Wani attajiri ya ƙwace ta ba girma ba arziki. أحد التجار سلبها بسهولة .

Sarki ya yi wa farke goma sha biyu na arziki.

الأمير أعطى التاجر مالا كثيرا .

## رشوة ← Rashawa :

Kar ka ba da rashawa , kuma kada ka karɓa.

لا تدفع رشوة ، ولا تأخذ رشوة .

Rashawa tana daga cikin manyan zunubai. الرشوة من الذنوب الكبيرة.

Alƙali mai karɓar rashawa ranar kiyama zai hadu da azaba.

القاضي المرتشي سينال العذاب يوم القيامة .

## رعد ← Aradu :

Aradu ta faɗi wa itacce ta tsage shi biyu.

الرعد سقط على الشجرة فقسمها نصيفين .

Ƙarata kamar aradu ce. صوتها كالرعد .



www.alkottob.com

In kuma ƙarya nake yi aradu ta faɗo mini.

إن كنت أكذب فليسقط الرعد عليَّ .

Tun tuni wuta daga aradu aka fara gane ta.

منذ القدم عُرفت النار لأول مرة من الرعد .

## ركاب ← Likkafa :

Duk abin nan kuwa dokinsa ba sirdi balle likkafa ko linzami.

كل هذا وحصانه بلا سرج ولا ركاب أو لجام .

Likkafa sarki ta azurfa ce. ركاب الأمير من ذهب .

Na zunguri doki da likkafa. وخزت الحصان بالركاب .

## ركاز ← Rikazi :

An karɓar humusin rikazi. يؤخذ خُمس الركاز .

## ركعة ← Raka'a :

Ya yi nafila da raka'a uku. تنفل بثلاث ركعات .

Wanda ya ƙara raka'a daya ko biyu , sai ya yi sujjada ba'adi.

من زاد ركعة أو ركعتين سجد بعد السلام .

Wanda ya yi kokanta a cikin raka'a ko sujjada sai ya zo da ita.

من شك في ركعة أو سجدة جاء بها .

## ركوع ← Ruku'u :

Tsoron Allah cikin ruku'unka da sujjadarka. اتق الله في ركوعك وسجودك .

Kada ka yi addu'a cikin ruku'unka. لا تدع في ركوعك .

Zaka karanta ƙunuti bayan ka yi ruku'i. ستقرأ القنوت بعد أن تركع .



www.alkottob.com

## : Ramalan ← رمضان

Azumin watan Ramalan farilla ne. صوم شهر رمضان فريضة .

Wanda ya yi amai a cikin ranar Ramalan ba zai rama azumin wannan rana ba. من ذرعة القيء في رمضان فلا قضاء عليه .

Allah yana yi wa mutane da yawa gafara a cikin watan Ramalan.

يغفر الله لخلق كثيرين في شهر رمضان .

## : Rukuni ← رُكن

Ya mantad da rukuni ɗaya cikin nafila. نسي رُكنا من النافلة .

Rukunin ɗaki ya faɗi. سقط رُكن الحجرة .

Musulunci yana da rukunai biyari. للإسلام خمسة أركان .

Duk wanda ya yi musun rukuni ɗaya daga cikin rukunan musulunci ya kafarta. كل من أنكر رُكنا واحدا من أركان الإسلام كفر .

Ba zai sambanci rukun yamani da bakinsa ba amma zai taɓa shi da hannunsa. لا يقبل الركن اليماني بفمه ولكن يلمسه بيده .

## : Ruhubanai ← رهبان

Ana son nisantar kisan ruhubanai. يُجْتَنَبُ قتلُ الرهبان .

## : Rauhani ← روحاني

Me zamu yi ? Wannan dai lalle yana da sha'ani da rauhani ne.

ماذا سنفعل ؟ لابد أن هذا له علاقة بالروحاني ــ المشعوذ ــ

Yana wuridi sai ka ce wani mai rauhani. يقرأ تعاويز كأنه روحاني .

## : Ruwaito ← رُوِيَ

Ya yi musun abin da aka ruwaito game da shi. أنكر ما رُوِيَ بشأنه .



www.alkottob.com

Wanda ake binne ba a sallace shi ba , an ruwaito cewa sai a sallace shi yana cikin kabari.

من دفن ولم يصل عليه ، رُوِيَ أنه يصلي عليه في القبر .

An ruwaito cewa sanad da yara littafin Allah yana huce hushin Allah.

رُوِيَ أن تعليم الصغار كتاب الله يُطْفِيء غضب الله .

## : Ruwa ← رَوَي

تستعمل للدلالة على الماء

Ta marabace shi ta kawo masa ruwa ya sha.

رحبت به وأحضرت له ماءً فشرب .

Bayan ya sha ruwa ya yi hamdala.

بعد أن شرب الماء حمَدَ الله .

Suka yi ta farin ciki sai ka ce waɗanda suka fada cikin ruwan Alkausara.

فرحوا كثيرا كمن سقط في ماء نهر الكوثر .

Ina ruwanki da sha'anin gidana.

ما دخلك بشئون بيتي .

## : Riya ← رياء

Kome ka yi don riya , ladanta yabon da zaka samu ga mutanen da ka yi wa.

كل ما تفعله رياء ، ثوابك الثناء الذي تناله لدي من ترائيهم .

Kullum wai mutane da nake kira ina yi musu liyafa don riya ce.

دائما أقيم وليمة لمن أدعوهم رياء .

## : Riyali ← ريال

Riyali biyar na sayi wannan hular.

اشتريت هذه القلنسوة بخمس ريالات .

Riyali yana da daraja a ko ina.

الريال له قيمة في كل مكان .

Alhazai ba su san lisafin riyali sosai ba.

الحجاج لا يحسبون الريال جيدا .

★★★



www.alkottob.com

# الزاي

## : Za'ida ← زائد

Musa in ya ba da labari sai ya yi za'ida cikinsa.

إذا قص موسى قصة زاد عليها .

Ka fadi labari yadda ka ji shi ba tare da ka yi za'ida ba.

قل الخبر ، كما سمعت دون أن تزيد .

## : Zabubi أو Zabibi ← زبيب

Za'a ba da zakka daga cikin abincin mutane garin kamar sha'ir da zabubi.

تؤدي الزكاة من طعام أهل البلد مثل الشعير والزبيب .

Ya yi cinikin zabubi da inabi.

يبيع الزبيب والعنب .

## : Zakka ← زكاة

Zakkar kudi da ta amfanin gona da ta dabbobi farilla ce.

زكاة المال والزرع والماشية فريضة .

Ba'a yin zakka ga hatsi ko dabino wanda awon kowannensu ya kasa kwando biyar.

لا زكاة من حَبٍّ أو تمر في أقل من خمسة أوسق .

Ana hada zinari da azurfa wajen zakka.

يجمع الذهب والفضة في الزكاة .

## : Zamani ← زمان

Ya yi zamanin annabi Nuhu.

عاش في زمن النبي نوح .

Tun zamanin da haka Masar take kasa mai albarka.

منذ الزمن القديم ، ومصر هكذا بلد خصب .



www.alkottob.com

Allah ya ba shi hikima fiye da dukan mutanen zamaninsa.

وهبه الله حِكْمةً اكثر من كل أهل زمانة .

Allah ya ja zamanika.

أطال الله عمرك .

زنا ← **Zina** :

Shari'a ba ta yarda da su ba da zina.

الشريعة لا ترضى لهم بالزنا .

Wanda ya yi zina na da , kuma katangarce , sai a jefe shi har ya mutu.

من زنى من حر محصن يرجم حتى يموت .

Ba'a yi wa mutum haddin zina sai da amsa laifi ko kuwa da ciki wanda zai bayyana.

لا يُحَدُّ الزاني إلا باعتراف أو بحمل ظاهر .

زينة ← **Zina** :

Ba abin da ke kambama mutum irin ya sa wando mai zina da jabba.

لا شيء يَغُرُّ الإنسان مثل ارتداء السروال المزركش والجبة .

Kowa yana so ya yi wa gidansa zina , sai im ba shi da hali.

كل يريد أن يزين منزله إلا إذا كان رقيق الحال .

Dawakin sarki zina ne ranar sall.

خيل الأمير زينة يوم العيد .

زان ← **Zane** :

زخرف أو رسم

Ina so ka yiwo mini takalma daidai da ƙafata kuma ka zane su da kumfar zinariya.

أريد أن تصنع لي حذاء مناسبا لقدمي ، وتزينه بخيوط من الذهب .

Ya tara yara yana zana masu yaƙoƙin da ya halarta duka.

جمع الأولاد وأخذ يرسم لهم صورة الحروب التي حضرها .



www.alkottob.com

## : Zindiƙi ← زنديق

A kan kashe zindiƙi, kuma ba a karbar tubansa. يُقْتل الزنديق، ولا تُقْتل توبته
Zindiƙi shi ne wanda zai ɓoye kafirci. الزنديق هو الذي يُضْمر الكفر .

## : Zur ← زور

Ya yi shaidar zur. شهد زورا .
Kiyaye harshe daga yin ƙarya da shaidar zur yana daga farillai.
حفظ اللسان من الكذب وشهادة الزور من الفرائض .
Wanda ya yi wa shaidar zur ya sa aka kashe. أمر أن يُقْتل من شهد زورا .

## : Zawwal ← زوال

Lokacin sallar azahar muhtari shi ne tun daga zawwal.
وقت صلاة الظهر المختار هو من الزوال .
Zawwal shi ne gushewar rana daga tsakiya ta gota ɗin nan har zuwa ƙurshen ƙama. الزوال هو ميل الشمس من الوسط حتى تتجاوز نهاية القامة .

## : Zaiti ← زيت

An haramta a cin narkakken abu kamar man shanu ko zaiti da ɓera ya mutu a cikinsa. يحرم أكل الشيء السائل مثل السمن أو الزيت الذي مات فيه الفأر .

## : Zaituni ← زيتون

Za'a fid da zakka ga zaitunin. ستُخْرج الزكاة عن الزيتون .
Ba a samun zaituni sai a ƙasashen larabawa.
لا يوجد الزيتون إلا في بلاد العرب .
Bishiyar zaituni mai albarka ce. شجرة الزيتون مباركة .



www.alkottob.com

## : Ziyara ← زيارة

Ziyarar dakin Allah sau daya cikin rayuwa farilla ce a bisa kan musulmi. زيارة بيت الله مرة واحدة في العمر فريضة على المسلم .

Idan mutanen garinsu sun zo ziyararsa , suka tambaye shi dalilin da ya sa shi arziki gaba ɗaya haka.

إذا جاء أهل بلدهم لزيارته سألوه عن السبب الذي جعله ثريا مرة واحدة هكذا .

Suna ziyartar juna suna hira tare. يزورون بعضهم ويسمرون معاً .

Mutanen da yawa daga biranen Masar suna zuwa su ziyarce shi.

ناس كثيرون من بلاد مصر يأتون لزيارته .

## : Zayyana ← زَيَّن

Zan zayyana launin gemunsa siffar idonsa , da gashinsa da launin jikinsa. سأجعل لون لحيته بلون عينية ، وشعره بلون جسمه .

Na yi wa allona zayyana. زَيَّنت لوحي .

Ba wanda ya fi malam Musa iya zayyana.

لا أحد يفوق الأستاذ موسى في الزينة .

***



www.alkottob.com

# السين

## سائل ← Sa'ili :

تعني متسول

Sa'ilin nan ne ya zama amintaccen bawa. هذا السائل صار الخادم الأمين .
Kar ka zama sa'ili a tsakanin mutane. لا تكن متسولا بين الناس .
Da mutum ya zama sa'ili , gwamma ya zama mai faskare.
أن يكون الإنسان حطّابا خير له من أن يكون سائلا .
Sa'ili ba shi da mutunci a tsakanin mutane. ليس للسائل كرامة بين الناس .

## سبب ← Sababi :

تأتي بمعنى سبب أو مشكلة

Abubuwan da ke warware alwalla su ne karuruwa da sabubba.
الأمور التي تنقض الوضوء أحداث وأسباب .
Ilmi shi ne sababin girma ga ɗan Adam. العلم هو سبب العظمة لبني آدم .
Lalle mutumin nan ɗan sababi ne. إن هذا الرجل جلاّب للمشاكل .
Kada ka ja mini sababi. لا تجلب لي المشاكل .
Ba girma ba sababi. بلا سبب .

## سبابة ← Sabbaba :

Ya zuba ruwa a bisa sabbabansa. صب الماء على سبّابته .
In ka yi zaman tahiya ka sa idonka a kan sabbabarka.
إذا جلست للتشهد ضع عينك على سبابتك .



www.alkottob.com

Sabbaba da shi ake yin ishara lokacin tahiya.

السبابة يشار بها عند التشهد .

## السبت ← : Asabar

Zan gamu da Musa ranar asabar mai zuwa.

سألتقي بموسى يوم السبت القادم .

Asabar rana ce mai girma a wajen yahudawa.

السبت يوم مهم لدي اليهود .

Baƙi sun zo gidana ranar asabar. جاء الضيوف إلى بيتي يوم السبت .

## سبحان ← : Subhana

Subhana lillahi yaƙi ɗan zamba. سبحان الله الحرب خدعة .

Na ce «subhana lillahi». قلت «سبحان الله» .

Waziri ya ce «subhana lillahi». قال الوزير «سبحان الله» .

## سُبْعٌ ← : Subu'i

Mutum bakwai in aka ba su fam bakwai kowa zai samu subu'in kudin ke nan.

سبعة رجال إذا وزع عليهم سبع جنيهات . سينال كل سبع المال .

Ni subu'in gidan na samu da aka raba.

عند قسم المنزل حصلت على السبع .

## سبعين ← : Saba'in

Shekarata saba'in a nan ina ibada. سبعون عاما هنا أعبد الله .

Ya tsuguna yana zargin kansa da wautar da ta sa ya ƙi karbar sulensa ɗari da sana'in ya huta da azabar.

جلس يلوم نفسه على الغباء الذي جعله يرفض أخذ مائة وسبعين شلنا ويرتاح من العذاب .

Tsawonsa zira'i saba'in kaɗai. طوله سبعون ذراعا فقط .



www.alkottob.com

## : **Sabili** ← سبيل

تأتي بمعني بسبب

Suka zama kamar mahauta sabili da farin ciki.

صاروا كالمجانين بسبب السرور .

Ya koma ɗakinsa , ya yi kwance sabili da zafin ranar da ya ɗauka.

عاد حجرته ، ونام بسبب حرارة الشمس التي تعرض لها .

A wurin fa suka yi niyyar kwanaki da dama sabili da ciniki.

في هذا المكان نووا قضاء أيام ان وجدت الفرصة بقصد التجارة .

## : **Sutura** ← سترة

تأتي بمعنى ستر أو دفن

Kafa sutura ga wanda ba mamu ba. وضع السترة لغير المأموم .

Ta yi masa wanka bayan da ta sutura masa tsiramacinsa.

غسّلته بعد أن سترت عورته .

Aka yi masa sutura aka sa shi cikin bayi. ضنعت له سترة ووضع مع الخدم .

Da azahar za'a yi mata sutura. عند الظهر ستدفن .

Aka koma aka yi sutura malam Usman , kowa ya kama gidansa.

عادوا ودفنوا الأستاذ عثمان وعاد كل إلى منزلة .

Daga sharuɗɗan salla suturcewar al'aura. من شروط الصلاة ستر العورة .

Bai sami abin da zai suturce al'aura ba . لم يجد ما يستر العورة .

## : **Sittin** ← ستين

Sarki ya sa aka tara masa manyan malamai guda sittin na Ƙasarsa.

أمر الأمير أن يجمع له ستون من كبار علماء بلدة .

Kafin kwana sittin cikin fam goman nan saura duk bai fi sule saba'in.

قبل ستين يوما هذه العشرة جنيهات لم يبق منها أكثر من سبعين شلنا .



www.alkottob.com

### : Sujjada ← سجد

Wanda ya yi ragi ko ya yi Ƙari sai ya yi sujjada Ƙabali.

من نقص أو زاد سجد قبل السلام .

Ba a yin sujjada Ƙabali sai in an bar sunna biyu.

لا يُسجد قبل السلام إلا إذا تركت سنتان .

Wanda ya yi kokanto a cikin raka'a ko sujjada sai ya zo da ita.

من شك في ركعة أو سجدة جاء بها .

### : Sihiri ← سِحْرٌ

Ya Ƙarbi kudi da yawa gare su , kana ya yi musu na sihiri.

أخذ مالا كثيرا منهم ، ثم عمل لهم أعمال السحر .

Akun nan sihiri gare shi , in ya fara ba da labari.

هذا البيغاء ـــ كلامه ـــ كالسحر ـــ إذا بدأ يقص القصة .

A arewa da garin , akwai gonar wani mutum wanda yake mai sihiri da gaske.

إلى الشمال من المدينة ، توجد مزرعة رجل لديه سحر عجيب .

Wannan doki na sihiri ne.

هذا الحصان جميل .

Wani bahindi mai sihiri ya sato ya ɗauko bisa doki.

رجل هندي ساحر سرقة وأخذه فوق الحصان .

### : Suhuri أو Sahur ← سحور

Ya ce ta yi shirin girkin sahur.

طلب أن تعد طبيخ السحور .

Ga su nan da rana suna kai suna komawa don ɗaukar suhuri.

ها هم ليلا ونهارا ذاهبون عائدون لأخذ السحور .

### : Sudusi ← سدس

Kaka ta wajen uwa ta kan gaji sudusi.

الجدة من ناحية الأم ترث السدس .

Sudusin ya zama tsakaninsu.

السدس صار بينهم .

Idan ta wajen uban ita ce ta fi su kusanci to , sai sudunsi ya zamanto a tsakaninsu rabi-rabi.

إذا كانت التي للأب أقربهما فالسدس بينهما نصفين .



www.alkottob.com

Ya kan sami sudusi idan yana tare da ɗa namiji , ko dan da namiji.

له السدس مع الولد الذكر أو ولد الولد الذكر .

**: Sirri أو Asiri ← سِرٌ**

Ya ce in yi masa sutura , in rufe masa asiri domin ba sharifi ba ne.

طلب أن يسترة ، ويخفي سرة لأنه ليس شريفا .

Ba wanda ya san wannan asire. لا أحد يعرف هذا السِّر .

Na ga asirimmu zai tone. رأيت أن سرّنا سينكشف .

Zan gaya masa amsar tambayar a asirce.

سأقول له الإجابة عن السؤال سرًا .

Aka aika da dogarai a asirce suka maƙe gidan liman.

بعثوا بالجنود سرًا ليفتشوا منزل الإمام .

Ina zaka iya samo mini mutumin da zai sayi ƙaramin gidana cikin sirri. أين تستطيع أن تجد من يشتري منزلي الصغير في السرِّ .

Kada ka yi maganar sirri da mai surutu.

لا تتكلم في السر مع كثير الكلام .

Neman jin sirrin wani ba da izininsa ba haram ne.

محاولة سماع السر دون إذن صاحبه حرام .

Asirtawa a cikin inda ake asirtawa. السرِّ حيث يكون السرِّ .

**: Sura ← سورة**

Daga sunnonin salla ta da iƙama , karanta sura bayan fatiha.

من سنن الصلاة الإقامة وقراءة سورة بعد الفاتحة .

Suran farko ta zama gabanin na biyu ta kuma fi ta tsawo.

تكون السورة الأولى قبل الثانية وتفوقها طولا .

Idan karatun sura ya ƙara sai ya yi kabbara. إذا انتهت قراءة السورة كبّر .

**: Sirdi ← سرج**

Duk abin nan kuwa dokinsa ba sirdi balle likkafa ko linzami ma babu.

كل هذا والحصان بلا سرج ولا رِكاب ولا لجام .



www.alkottob.com

Aje cikin birni a kamo ƙato guda, a yi mini sirdi bisansa.

إذهب إلى المدينة ، وأمسك رجلا ضخما ، وضع لي سرجا على ظهر .

In ka ga goɗiya da sirdi tạna gudu , wani ta kyar.

إذا رأيت الفرس يجرى بالسرج فقد أوقع صاحبه .

## سَعْيٌ ← Sa'ayi :

Ya yi dawafi da sa'ayi da rage gashi. طاف وسعي وقصر الشعر .

Zai daina yin talbiyya yayin da ya shiga Makka har sai ya yi dawafi fa sa'ayi tsakanin Safa da Marwa.

يترك التلبية إذا دخل مكة حتى يطوف ويسعى بين الصفا والمروة .

## ساعة ← Sa'a :

تأتي بمعنى ساعة أو سعادة أو حينئذ ، أو حظ

Ba zamu yi tafiyar fiye da sa'a uku ba. لن نسير اكثر من ثلاث ساعات .

Ba shi da damar tafiya saura sa'a guda a tashi.

ليس لدية فرصة للسير ،بقي ساعة واحدة ولتتحرك .

Wata sa'a ta kan ja mutum ta kai shi halaka.

وساعة تجر الإنسان وتوصلة إلى الهلاك .

Ya roƙi Allah ya ba shi sa'a. سأل الله أن يهبه السعادة .

Wannan lalle ya sami sa'a hakika. لا بد أن هذا نال السعادة حقيقة .

Ka yi yake da yawa , duk kai ke cin nasara , amma a yau na ga babu sa'a. خضت حروبا كثيرة ، وكلها كنت تنتصر فيها ، ولكن اليوم لا أرى لك حظًا .

Ba ni da sa'a. ليس لي حظ .

Zan debam masa wa'adi im bai kawo ba sa'an nan in ɗaure shi.

سأعطية وعدا ، أن لم يُحْضِر حينئذ سأسجنه .

Zauna nan ka hardace wannan labari sa'an nan ka tashi.

اجلس هنا احفظ هذه القصة حينئذ قُم .



www.alkottob.com

In sarki ya gaji da kallo sa'an nan ya ba da sallama.

إذا تعب الأمير من النظر حينئذ يستأذن .

**سعيد ← Sa'ida :**

Ko yaushe ya kawo sai ɗan 'iya ya ce masa , yau ka fito cikin sa'ida.

دائما إذا أحضر يقول له طنثيا خرجت اليوم في لحظة سعيدة .

In zai kawo sa'ida , ai abin da ya kamata ke nan.

إذا جئت بمصلحة هذا هو ما ينبغي .

**سعير ← Sa'ira :**

Ba mai shiga Sa'ira sai wanda Allah ya azabta shi.

لا يدخل السعير إلا من عذبه الله .

Allah ya tanadi Sa'ira ne don azabta masu laifi.

أعد الله السعير ليعذب المذنبين .

Allah ka kyaye mu da shiga Sa'ira. وقانا الله من دخول السعير .

**سفر ← Safara :**

تأتي بمعنى التجارة

Gidan kuma na rigaya na sayad da shi cikin watan jiya don safara , bayan na yi shawara da ita.

سبق أن بعت المنزل في الشهر الماضي للتجارة بعد أن شاورتها .

Na sha wuya lokacin da nake yin safara tsakanin Kano da Kaduna.

لقيت الصعاب عندما كنت أتاجر بين كنو وكادونا .

Safara ba aikin rago ba ce. التجارة ليست حرفة الكسول .

Safara akwai samu , sai dai akwai wahala. التجارة فيها الربح وفيها التعب .



www.alkottob.com

## : Sakar ← سقر

Ba mai shiga Sakar sai wanda Allah ya azabta shi.

لا يدخل سقر إلا من عذبه الله .

Allah ya tanadi Sakar ne don azabta masu laifi.

أعد الله سقر لعذاب المذنبين .

## : Sukari ← سكر

Ya sa alkama da sukari. وضع القمح والسكر .

A kasan nan ma ana yin sukari. في هذا البلد أيضا السكر .

In ka sa baki sai ka ji kamar sukar. إذا وضعت في فمك شعرت كأنه سكر .

Ya kai su wani ɗan kauye , ya ce a tsare su , a rika ba su sukar.

أخذهم إلى قرية صغيرة ، وطلب أن يُحرسوا ويُعْطوا السكر .

## : Sukuni ← سكون

تأتي بمعنى الراحة أو الهدوء أو الثراء

Tun daga daren nan har zuwa daen salla, gwauro ba shi da sukuni.

منذ هذه الليلة حتى ليلة العيد والأعزب لا يرى الهدوء .

Annobar ɓera ta bulla hankalin likitocin ya tashi suka kasa samun sukuni. انتشر مرض الطاعون وثار غضب الأطباء وعجزوا عن الراحة .

Ba a ganinsa sai wurin masu sukuni. لا يُرى إلا حيث الأثرياء .

Kowa ya sani a lokacin kafin mijinta ya rasu ta fi shi sukuni.

الجميع يعرف قبل أن يموت زوجها وهي تفوقة ثراءً .

## : Sultu ← سُلت

An haɗa alkama da sha'ir da sultu wajen yin zakka.

جَمع القمح والشعير والسُّلت عند أداء الزكاة .



www.alkottob.com

Za'a ba da zakka daga cikin abincin mutanen garin kamar sha'ir da sultu.

تؤدي الزكاة من طعام أهل البلد مثل الشعير والسلت .

## : Sarauta ← سُلْطة

Ya ci sarautar Ƙasan nan. — كسب سلطة هذا البلد .

Ni kuwa na haye gadon srautar garin sai amru da nahayu.

اعتليت عرش السلطة في هذا البلد آمر وأنهي .

Kaddara da zata auku bayan an sayad da farin nan ita ce sarauta.

القدر الذي يحدث بعد بيع هذا الجراد هو تولي السلطة .

## : Salsala ← سلسل

تأتي بمعنى سلالة

Wannan Ƙauyen nan ne kuka fito salsalarku daga Musa ne.

أنتم من هذه القرية ، تسلسلتم من موسى .

In ka bi salsalar Bayajida zaka samu daga cikin larabawa ya fito.

إذا تتبعت تسلسل بيازيد ستجد أنه انحدر من العرب

Ni ba baƘo ba ne kowa ya san salsalata. — لست غريبا الكل يعرف نسبي .

## : Sulale ← سَلَّل

تأتي بمعنى تسلل

Na ji sun yi shiru sai na sulale na dawo.

سمعت أنهم سكتوا فتسللت وعدت .

Ya sulale da dare ya bi dan uwansa. — تسلل في الليل واتبع أخاه .

Ɓarawo ya sulale daga kurkuku. — اللص تسلل من السجن .



www.alkottob.com

## : Sallama ← سلَّم

تأتي بمعنى التسليم والسلام والأستئذان والموافقة

Suka yi sallama da juna. سلَّموا على بعضهم .

Da ya yi sallama ya yi addu'a. بعد أن سلَّم دعا .

Sarki ya aika aka sallami mutanen nan da ke waƙafi.

بعث الأمير ليسلِّم هؤلاء الناس الموقوفين .

Ya nufi wurin ya kafa salama kan ya wuce.

قصد المكان وأقام السلام ثم مضى .

Ana sallama a ƙofar gida. شخص يستأذن على باب المنزل .

Ga wani saurayi can a ƙofar gida yana sallama da ke.

ها شاب على باب المنزل يستأذون مِنْكِ .

Ya ce an sallama maka. قال موافق على البيع لك .

## : Sammu ← سُمٌّ

Ya gane ashe sammu ne babban maƙiyansa ya aikata masa a makirce.

فهم أن سمًّا بعث به له كبير أعدائه مكراً .

Ta yi mini sammu ne in ci in mutu. صنعت لي سمًّا أكله فأموت .

Ba wanda zai ba sarki wani abinci ya ci don tsoron sammu.

لا أحد يعطى الأمير طعاما ليأكله خشية السمّ .

## : Sama ← سماء

Na tada kai na hangi sama. رفعت رأسي نظرت إلى السماء .

Ga abin da aka umurce ni , in ɗauke ka ciki in tashi da kai zuwa sama. هاما أُمرت به ، أن أخذك في ــ الصندوق ــ وأطير بك إلى السماء .

An kawo sama ta biyar. وصلوا السماء الخامسة .

Na daga kai sama. رفعت الرأس إلى أعلى .

Shi kuwa ya kafa idnunsa sama. ثبت عينية أعلى .



www.alkottob.com

Allah sarki wanda ya halicci sammai da ƙassai.

الله الملك الذي خلق السموات والأراضين .

Galibanta ma a kan yi shekaru ba a samun ruwan sama ko kadan.

غالبا ما تمر السنوات دون أن يسقط المطر ولو قليلا .

Muka yi ta sako musu kibau kamar ruwan sama.

ارسلنا اليهم السهام كالمطر ـــ ماء السماء ـــ

## : Sam'an ← سمعاً

Ya ce sam'an wa ta'atan. قال سمعاً وطاعة .

In ka samu matar da ta bi ka sam'an wa ɗa'atan ka huta a rayuwarka.

إذا وجدت المرأة التي تطيعك .. سمعا وطاعة ترتاح في حياتك .

Musa ɗansa yana binsa sam'an wa da'atan. موسى ابنة يطيعة سمعا وطاعة .

## : Sanadi ← سَنَدٌ

تأتي بمعنى سبب

Watakila sai wannan shi zai zama sanadin arzikinka.

ربما يصير هذا سبب رزقك .

Musa zai zama sanadin cuce-cuce da raunuka.

موسى سيصير سبب أضرار وجراح .

Shi bikin nan na mutuwa ya kan zama sanadin yunwa a cikin ƙasarsu.

حفل الموت هذا يصير عادة سبب الجوع في بلدهم .

## : Sunna ← سُنَّةٌ

Ya riƙa kuma koyi da masu bin sunnan Annabi.

يعلم دائما من المتبعين لسنة النبي .

Ta zama matarka ta sunna. صارت زوجتك على السنة .



www.alkottob.com

Ba a yin sujjaɗa ƙabli sai in an bar sunna biyu.

لا يُسْجد قبل السلام إلا إذ تُركت سنتان .

Akawai sunnoni waɗanda suke ƙarfafa da nafilfil.توجد سنن مؤكدة ونوافل

## : Asuwaki ← سواك

Babu laifi ga mai azumi ya yi ta yin asuwaki.

لا بأس للصائم أن يستعمل السواك .

Yin asuwaki mustahabbi ne. استعمال السواك مستحب .

Mutahabban alwalla su ne farawa da bismilla yin amfani da asuwaki.

مستحبات الوضوء البدء باسم الله والاستفادة من السواك .

## : Siyasa ← سياسة

Wannan shi ne jazaman ƙuri'ata ta masu gaskiya ne , ba ya dan siyasa ba ne. اقتراعي هٰذا بالتأكيد اقتراع الصادقين وليس اقتراع السياسيين .

In har na faɗi a zaben nan , to da ni da siyasa har abada.

إذا رسبت في هذه الانتخابات سأترك السياسة إلى الأبد .

In kuwa gwauro ɗan gata ne, a kan yi masa siyasa.

إذا كان الأعزب من أسرة كبيرة يُعَامل عادة بالسياسة .

★★★



www.alkottob.com

# الشين

## : Sha'a ← شاء

Ba ya yin kome sai ma sha'a. لا يفعل إلا ما شاء .
Ma sha'a Allah. ما شاء الله .
In talauci ya yi wa ƙasa kanta rayuwar mutanenta sai, illa masha'a Allah. إذ أثر الفقر على البلد تكون حياة أهلها إلى مصير لا يعلمه إلا الله .

## : Sha'ani ← شأن

Ba ni da ta cewa cikin wannan sha'ani. ليس لدي ما أقوله في هذا الشأن .
Ban ce maka kome ba don ka hana ni tsalma baki cikin sha'anin manya. لن أقول لك شيئا ، لأنك منعتني من التدخل في شأن الكبار .
Shaihu ya ci gaba da sha'anin da yake ciki na jihadi.
استمر الشيخ فيما هو فيه من شأن الجهاد .
Ba ya ko sauka, yana can yana ta shaninsa na addini da ibada.
لا ينزل ، يبقى هناك ، مشغولا بأمر الدين والعبادة .
Duk mutanen garin babu wanda yake shiga cikin sha'anin ɗan'uwansa. كل أهل المدينة لايوجد من يتدخل في شأن أخيه .
A sayad da wani jaki nasa jiya don ya yi sha'anin salla.
باع حمارة أمس ليشتري حاجات العيد .
Ka gaya mana abin da ka sani ciin sha'anin mulki.
قل لنا ما تعرف في شئون الملك .
Ya fara koya masa sha'anin mulki. بدأ يعلمه شئون الملك .
Ya kira babban baransa ya danƙa masa sha'anin gidansa.
نادي اكبر خدمة وسلمه شئون منزله .



www.alkottob.com

Sha'anin haihuwa abu ne mai wuya. أمر الولادة صعب .

شئوم ← **Shu'umi** :

تأتي بمعنى سيّء

Na sayo shu'umin doki. اشتريت حصانا سيئا .
Kada Allah ya sa ka auri shu'umar mata. وقاك الله من زواج المرأة السيئة .
In gida ya yi ƙunci sai ya zama shu'umi. إذا كان المنزل ضيقا يكون سيئا .

شدَّد ← **Shaddada** :

Aka sake aikawa da yaƙi daga Masar amma abin ya rigaya ya shaddada. بعثوا مرة أخرى للحرب من مصر ، ولكن ساءت الأمور .
Kar ka shaddada wa mutane don kada Allah ya shaddada maka.
لا تشدد على الناس كي لا يشدد الله عليك .
Ciwon sarki ya shaddada. اشتد مرض الأمير .
Kar ka shaddada wa matarka don kada ƙiyayya ta shiga tsakaninku.
لا تشدد على زوجتك فتدب البغضاء بينكما .

شر ← **Sharri** :

Allah ya kyashe ka sharrin mutane. وقاك الله شر الناس .
Sau da yawa mutum yakan so abu ya zo ya zama sharri ne gare shi.
مرات كثيرة يريد الانسان شيئا فيأتيه ويصير شرًّا له .
Sauro ba ya kawo wa mutane kome sai sharri.
البعوض لا يجلب للإنسان إلا الشرَّ .

شرب ← **Sha** :

Yana shan shayi. يشرب الشاي .



www.alkottob.com

بعد أن شرب الماء حمد الله .

Bayan ya sha ruwa ya yi hamdala.

Ta marabace shi ta kawo masa ruwa ya sha.

رحَّبت به وأحضرت له الماء فشرب .

## شرح ← Sharaha :

شُرِح له .

An yi masa sharaha.

قرأت شرح العشرينية .

Na karanta sharahin ishriniyya.

Ina yin ƙoƙarin na yi wa littafin Buhari sharahi.

أحاول شرح كتاب البخاري .

## شرط ← Sharaɗi :

يوجد شرط واحد .

Akwai sharaɗi guda.

لدي شرط واحد نعمله .

Ina da sharaɗi daya wanda zamu yi.

Ka je yanzu cikin taro, ka ce ka ba shi ni amma da sharadi guda.

إذهب الآن في الجمع ، وقل أنك اعطيته إياي ولكن بشروط واحد .

Sharuɗɗan tuban yin nadama a kan abin da aka yi.

شروط التوبة الندم على ما فُعِلَ .

## شريعة ← Shari'a :

### تأتي بمعنى القانون

الشريعة لم تقل ذلك .

Shari'a ba ta ce haka ba.

A shari'a musulunci ba laifi ba ne in aure ki.

لا بأس في الشريعة الإسلامية أن أتزوجك .

Ko an doki mutum ya mutu ba wata shari'a balle a yi diyya.

حتى لو ضرب الإنسان ومات لا شريعة تعاقبه ولا دية .



www.alkottob.com

Aka yi shari'a. حُكِمَ .

Da alƙali ya ji haka ya yanke shari'a. عندما سمع القاضي ذلك حَكَمَ .

Alƙali da ya yarda hukuncinsa , mu je ya yi mana shari'a.

القاضي الذي يرضى حكمه ، نذهب ليحكم بيننا .

Aka shari'a da shi a kan haka. حقق معه على ذلك .

Alƙali ya ce tun da ya taka shari'a sai na yi masa ladabi.

قال القاضي طالما هتك الشريعة يجب أن أعاقبه .

Da gari ya waye alƙali ya zo gidan shari'a.

عندما طلع النهار جاء القاضي إلى المحكمة .

Da jin haka sai ta sheƙa a guje har gidan shari'a.

عندما سمعت ذلك جرت مسرعة إلى المحكمة .

## شرف ← Sharafi :

In mutum yana kan sharafinsa ba mai durƙusad da shi sai Allah.

إذا حافظ الإنسان على شرفة لايخضعة إلا الله .

Asalin mutum shi ne sharafinsa. أصل الإنسان شرفه .

Ana auren mace don sharafinta. تنكح المرأة لشرفها.

## شريف ← Sharifi :

Shi ba sharifi ba ne. هو ليس شريفا .

Ya shiga rigar sharifai. ادعي أنه من الأشراف .

Dalilin wannan al'amari dai baƙon nan sharifin nan, riga biyu na Shariftaka yake da su.

سبب هذا الأمر أن هذا الضيف شريف من ناحية الأم والأب .

Sarki ya ce «a kai shi gun dan'uwansa sharifi ya sauka».

قال الأمير «خذوه إلى حيث أخيه الشريف لينزل» .



www.alkottob.com

## : **Shirku** ← شِرْكٌ

Kar ka zama cikin ma'abotan shirku. لا تكن من أهل الشرك .
Fir'auna daga cikin babban ambaton shirku. فرعون من أكبر أهل الشرك .

## : **Shaɗaranji** ← شطرنج

Bai halatta a yi wasa da 'ya'yan dara ba ko shadaranji.
لا يجوز اللعب بالنرد ولا الشطرنج .

## : **Sha'aban** ← شعبان

Yin azumi watan sha'aban nafila ce. صيام شهر شعبان نافلة .
Zan yi aure a cikin watan sha'aban mai zuwa.
سأتزوج في شهر شعبان القادم.
Sha'aban shi ne watan na takwas a cikin jerin watannin hijira.
شعبان هو الشهر الثامن في السنة الهجرية .

## : **Sha'ir** ← شعير

An hada alkama da sha'ir wajen yin zakka.
جُمع القمح والشعير عند أداء الزكاة .
Za'a ba da zakka daga cikin abincin mutanen garin kamar sha'ir.
تؤدي الزكاة من عيش أهل البلد مثل الشعير .
Hatsinsu shi ne alkama da sha'ir. حبوبهم القمح والشعير .

## : **Shu'arau** أو **Shu'ara** ← شعراء

Kar ka bi abin da shu'ara'u suke faɗa don kar ka halaka.
لا تتبع ما يقول الشعراء حتى لا تهلك .
Hansa'u tana cikin shu'ara'un musulunci. الخنساء من شعراء الإسلام .



www.alkottob.com

Kar ka bi abin da shu'ara'u suke fada don kar ka halaka.

أريد أن أقراء كتب الشعراء السبع (المعلقات).

## : Shagali ← شغل

تأتي بمعنى عَمل أو فَرح أو شَغَل

Mutanen garin suka kwana arba'in suna shagali iri iri na addini da na al'ada. قضى أهل المدينة أربعين يوما في أعمال مختلفة دينية وعادية .

Aka yi babban shagali. أقيم فَرَحٌ كبير .

Aka yi shagalgula masu ƙayatarwa. أقيمت أفراح جميلة .

An karahanta waiwaye a cikin salla da dukkan abin da zai shagaltad da mutum. كُرِه الإلتفات في الصلاة وكل ما يشغل الإنسان .

Kada ka ba shaiɗan ya shagaltad da kai. لا تجعل الشيطان يشغلك .

## : Shafa'i ← شَفْعٌ

Wanda ya yi sallar isha'i sai ya tashi ya yi shafa'i da wutiri.

من صلى العشاء يقوم ويصلى الشفع والوتر .

Sa'an nan sai ya sallaci shafa'i da witiri da karatu a fili.

ثم يصلى الشفع والوتر جهراً .

## : Shufu'a ← شُفْعة

Ana yin shufu'a kurum ga ƙasa ne. تكون الشفعة في الأرض فقط .

Babu shufu'a ga abin da aka riga aka raba.

لا توجد شفعة فيما سبق وقُسِّمَ .

Ba a bayad da shufu'a haka kuma ba a sayad da ita.

لا تُوهب الشفعة ولا تُباع .



www.alkottob.com

## : Shafaƙi ← شفق

Lokacin 'isha'i tun daga fakuwan shafaƙi zuwa sulusin dare.

وقت العشاء من اختفاء الشفق إلى ثلث الليل .

Shafaƙi shi ne ja-ja-ja nan da yake wanzuwa a yamma daga ragowar hasken rana. الشفق هو الحمرة الباقية من المغرب من بقايا شعاع الشمس .

Lokacin sallar isha shi ne bayan ɓuyan shafaƙi.

وقت صلاة العشاء هو بعد اختفاء الشفق .

## : Shaƙiƙi ← شقيق

Shaƙiƙi ya kan kare na wajen uba. الشقيق يحجب الأخ للأب .

Dan uwa na wajen uba kamar shaƙiƙi ne, a wajen rashin shaƙiƙi.

الأخ من الأب كالشقيق حيث ينعدم الشقيق .

Rabon gadon 'yar'uwa shaƙiƙiya rabi ne. ميراث الأخت الشقيقة النصف .

'Yan 'uwa maza shaƙiƙai. الأخوة الرجال أشقاء .

Sai ka ce ba shaƙiƙai ba ne. كأنهم ليسوا أشقاء .

## : Shaƙiyi ← شقي

Idan na ga kai shaƙiyyi ne marasa tausayi in kashe ka.

إذا رأيت أنك شقي عديم الرحمة قتلتك .

Suka gaya masa ga wani shaƙiyyi, ya kawo musu fatan jakai wai su saya. قالوا له ها شخص شقي ، أحضر لهم جلد الحمير ليشتروه .

Da labari ya bazu cikin gari duk, aka tasam musu da dariya da shakiyanci. عندما انتشر الخبر في المدينة الجميع قابلوهم بالضحك والسخرية .

Yana gaɓar shakiyanci haka , sai ran nan uban ya kwanta ciwon ajali.

كان في قمة شقاوته ، عندما رقد أبوه بمرض الموت .



www.alkottob.com

## : Shakka ← شك

Ba shakk̃a kai waliyyi ne. لا شك أنك وليٌّ .
Ba shakka zai tafi da ni ƙasarsu. لاشك سيذهب بي إلى بلدهم .
Ba a yin azumi ranar shakka. لا يصام يوم الشك .
Da ma ina shakkar haka. لقد كنت أشك في ذلك .
Sarki ya yi shakkar wannan jawabi. شك الأمير في هذا الكلام .

## : Shukura ← شُكْر

Dan sarki ya yi shukura da ya kuɓuta. شكر ابن الأمير عندما نجا .
Na yi wa Allah shukura a bisa ni'imarsa a gare ni.

شكرت الله لنعمته عليَّ .

Dole ne ga musulmi ya yi shukura ga Allah.

يجب على المسلم أن يشكر الله .

In ka yi shukura ga Allah a bisa ni'imarsa sai ya ƙara maka.

إذا شكرت الله على نعمته زادك .

## : Shakawa ← شكوى

Sarki ya karɓa shakawarsa. أخذ الأمير شكواة .
Na miƙa shakawata gaban sarki. سلمت شكواى للأمير .
Du wanda ya je wa sarki da shakawarsa zai share masa hawaye.

كل من ذهب إلى الأمير بشكوى مسح له الدمع ــ أي أرضاه ــ

Kar ka miƙa shakawarka inda ba za'a kula da ita ba.

لا ترفع شكواك حيث لا يُهتم بها .

## : Shama'a ← شمعة

Ko wace kusaurwa kuma an kafa mata shama'a.

في كل ركن ثبتت شمعة .



www.alkottob.com

## شهد ← **Shaida** :

تأتي بمعنى شهد أو قال

Na shaida babu sarki sai Allah. شهدت ألا إله إلا الله .

Na shaida Muhammadu ne manzon Allh. شهدت أن محمد رسول الله .

Ba'a karɓar shaida sai daga adalai. لا تُقْبل الشهادةُ إلا من عدول .

Matar ta shiga gida ta shaida wa mijinta ana sallama a ƙofar gida.

دخلت المرأة البيت وقالت لزوجها شخص يستأذن على باب المنزل .

Da ya koma gida ya shaida wa uwar yarinya.

عندما عاد إلى المنزل قال لأم الفتاة .

Ya shaida mini cewa ya gama shiri gobe zai tashi da sasafe.

قال لي أنه أنهى الإستعداد ، غداً سيسافر في الصباح .

Kana da shaida ? هل لديك دليل ؟

Alkali ya nemi kan magana ya rasa don ba shaida.

بحث القاضي أصل المشكلة ولكن عجز لعدم الدليل .

Shaidun nan suka gaya masa wasicin da ya yi na raƙumansa.

قال له الشهود الوصية التي عملها بشأن جَمَله .

Ga shaidu da suka san abin da aka yi. ها الشهود الذين عرفوا ما حدث .

Sarki ya sa aka ɗaure shi shekara don ba shaidu.

أمر الأمير أن يسجن عاماً لعدم الشهود .

## شهادة ← **Shahada** :

Hakika masu shahada rayayyu ne. إن الشهداء أحياء .

Ya yi kalmar shahada. نطق بالشهادة .

Na ga an rubuta kalmar shahada a gefensa.

رأيت كلمة الشهادة مكتوبة على طرفة .

Suka yi shahada. استشهدوا .

Mutane da yawa suka yi shahada a wannan karo.

استشهد ناس كثيرون في هذه المعركة .



www.alkottob.com

## : **Shahara** ← شَهَرَ

Dalilin shahara garin nan shi ne kuza. سبب شهرة هذه المدينة هو الصفيح .

Da ya je yawon duniya sara ya koya har sarkin ɓarayi ya ci don shahara. عندما هام في الدنيا تعلم السرقة حتى صار رئيسا للصوص لشهرته .

Da dodanniyan nan ta ji haka ta san shaharata ba inda ba ta kai ba. عندما سمعت الجنية ذلك عرفت أن شهرتي وصلت كل مكان .

Ban taba jin ko sunansa ba, sai fayau ai ko shahararre ne ? لم اسمع اسمه إلا اليوم هل هو مشهور ؟

Nan da nan duk na shahara ga maroƙa. في الحال اشتهرت لدي المتسولين .

Wallahi yadda arzikina ya shahara nan ƙasar , kai ma sai ka kai haka nan. والله كما اشتهرت ثروتي هنا في البلد ، أنت أيضا تصل إلى هذا .

Labarinsa ya shahara ko ina cikin ƙasar. خبره اشتهر في كل مكان في المدينة .

## : **Sha'awa** ← شهوة

تأتي بمعنى شهوة أو رغبة أو متعة أو سرور

Ba ta kai shekarun da za a yi sha'awa gare ta ba. لم تبلغ العمر الذي تُشتَهي فيه .

Abin ya ba su sha'awa wai waliyyinsu ja'iru dai ashe, ko waliyyi ne da gaske. شيء يسرهم ، أي أن وليهم جائر ، ولي حقيقي .

Wannam ba shi da ma'ana mai ban sha'awa. ليس لهذا معنى جميل .

Ya sa masa kayayyaki masu ban sha'awa a ciki. وضع له في الصناديق أمتعة جميلة .

Tsabta dadi gare ta , ga mai yinta , ga sha'awa a idon masu gani. النظافة جميلة ، للقائم بها ، وجميلة في نظر الناظرين .

Sarkin fadansa ya riƙa nemo masa abubuwan da za su ba shi sha'awa. ظل رئيس القصر يطلب له الأشياء التي تعجبة .



www.alkottob.com

Ya koya musu wani abu wanda mutane zasu yi sha'awa ya saya da tsada. علمهم شيئا ، يعجب الناس فيشترونه .

Ka san abar sha'awa ce in zama ina iya jin maganar dabbobi.

تعرف أنه شيء عجيب أن أصير قادرا على سماع كلام الحيوانات .

## شاور ← Shawara :

### تأتي بمعنى مشاورة أو رأي

Yana iya shawaranta in ya so. يستطيع مشاورتها إن شاء .

Mun kawo maka shawara ne. جئنالك برأي .

Ina shawara haji ? ما الرأي ياحاج ؟

In ka bi shawarata kada ka sake yatsa cikin wannan al'amari.

إذا سمعت رأيي لا تتدخل في هذا الأمر مرة أخرى .

Kome zaku yi ban yarda muku ku yi shi ba , sai kun zo kun shawarci akun nan. كل ما تفعلونه لن أوافق عليه ، إلا إذا جئتم واستشرتم هذا الببغاء .

Suka shawarce shi da ya sake hanya. أشاروا عليه أن يُغيِّر الطريق .

Sarkin Sudan ya tara jama'a tasa ya shawarce su.

أمير السودان جمع رجاله وشاورهم .

Yana nan yana shawarwari. هنا يتشاور .

## شَوَّال ← Shawwal :

Aka sha domin ganin jinjirin watan shawwal.

يُفْطَرُ لرؤية هلال شهر شوال .

Ya tambaye ta «wane wata muke ciki» ta ce shawwal.

سألها «أي شهر نحن فيه» قالت شوال .

Watan shawwal yana daga cikin watannin haji.

شهر شوال من أشهر الحج .

Zan yi aure a cikin watan shawwal. سأتزوج في شهر شوال .



www.alkottob.com

## : Shayi ← شاي

In ka je kasuwa ka kawo mini shayi. إذا ذهبت إلى السوق أحضر لي شاي .
Ba na shan shayi mai zafi. لا أشرب الشاي ساخناً .

## : Shaihu ← شَيْخٌ

Duk inda ya ji ɗuriyar wani shaihun malami, sai ya aika masa kuɗi.
حيثما سمع شهرة شيخ عالم ، بعث له مالاً .
Shi ba abin da ke ransa illa ya yi karatu ya zama shaihun malamai.
هو ليس في نفسه إلا أن يتعلم ويصير شيخ العلماء .
In ka bibiya halinsa sai ka same shi waliyyi ne , ko kuwa shaihun malamai. إذا تتبعت حالة وجدته ولياً ، أو شيخ العلماء .

## : Shaiɗan ← شيطان

Aka yi mana addu'a don kada shaidan ya sake wasa da zukatammu.
دعا لنا لكي لا يلعب الشيطان مرة أخرى بقلوبنا .
Allah ya kyashe mu daga aikin shaiɗan. وقانا الله من عمل الشيطان .
Ga shi can yana bautar Allah , ni ina nan ina bin shaiɗa.
هاهو هناك يعبد الله ، وأنا هنا اتبع الشيطان .
Waɗansu 'yan garin shaiɗanu , suka tare ta suna jifarta.
بعض أولاد المدينة شياطين ، قابلوها بقذف الحجارة .
Na bar gida tun ina yaro saboda shaiɗancin neman asiri.
تركت المنزل منذ كنت صبيا ، للشيطنة وطلب السِّر .

★ ★ ★



www.alkottob.com

# الصاد

## صُبْحٌ ← Asuba أو Asubahin أو Subahi

Asuba na yi ya hau dokinsa ya kama hanya.

طلع الصبح فركب حصانه واتخذ الطريق .

Can kusan asuba , sa'an nan sai ga mai gida ya komo.

هناك قرب الصبح ، وإذا بصاحب البيت يعود .

Ya kutsa daji da sukuwa har kusan asuba sa'an nan ya tsaya.

توغل في الغابة عدواً ، حتى قرب الصبح ثم وقف .

Da asubahin farko Musa ya yi ɗamara.

في الصباح الباكر لبس موسى حزام الذخيرة .

Asubahin ranar kuwa Musa ya nufi kogi don ya yi wanka.

في صباح اليوم قصد موسى النهر ليستحم .

Lokanci sallar subahi tun daga hidowar alfijiri.

وقت صلاة الصبح من طلوع الفجر .

Ba a yin sallar nafila bayan sallar subahi.

لا تُصَلَّى النافلة بعد صلاة الصبح .

## صابون ← Sabulu :

Ga wurin wanke hannu, ga sabulu da tawal rataye.

ها مكان غسل اليد ، ها الصابون والمنشفة معلقة .

Yaya za'a yi wanka babu sabulu? كيف نغسل ولا يوجد صابون ؟

Ga ruwa ga sabulu duk dai suna fid da dauda.

ها الماء ، ها الصابون كلها تخرج القذارة .

In na yi dauɗa ya sayi sbulu , ya je rafi ya yi mini wanka.

إن أصابتني القذارة أشتري الصابون وذهب إلى النهر وحمَّاني .



www.alkottob.com

## : Sahibi ← صاحب

Yau na ci abinci ɗa sahibina. تناولت الطعام اليوم مع صاحبي .

Mutane da yawa sahibansa suka yi ta zuwa gare shi suna gaishe shi. ناس كثيرون أصحابة أتوا إليه لتحيته .

Ba a ambatun wani daga sahabban manzon Allah sai da mafi kyaun ambato. لا يذكر أحد من صحابة رسول الله إلا بأحسن الذكر .

## : Sahihi ← صحيح

Idan kuwa da wanda aka baiwa din ya mutu magadansa sun samu , su neme ta ga mai kyauta sahihi.

لومات الموهب له كان لورثته القيام فيها على الواجب الصحيح .

Katangancewa shi ne ya auri mace aure sahihi , ya taka ta , taku sahihi. الإحصان هو أن يتزوج آمرأة نكاحا صحيحا ويطأها وطأ صحيحا .

Aka sani maganin sahihi na zazzaɓi. عُرِفَ علاجٌ صحيح للحمي .

## : Sahara ← صحاري

تأتي بمعنى المفرد «صحراء»

Wata kila kun san labarin ḥamadan nan da ake kira sahara.

ربما عرفتم قصة هذه الحمادة التي تسمى صحراء .

Akwai iska mai ƙarfi da tsananin zafin rana a sahara.

توجد رياح قوية ، وحرارة شديدة للشمس في الصحراء .

## : Sahani ← صحن

Na sayo sahani kyakkyawa. اشتريت صحنا جميلا .



www.alkottob.com

Debo mini ruwa da wannan sahani. احضر لي ماء في هذا الصحن .

Dafa shayi a cikin shanin nan. سخن الشاي في هذا الصحن .

**: Sadaki ← صداق**

Sadakin da kuka yi wa yarinyan nan ban yarda da shi ba.

هذا الصداق الذي قدمتموه للفتاة لا أرضي به .

Zan biya duka sadakinta. سأدفع كل صداقها .

Mene ne sadakin auren irin waɗannan idan ba za ka cuce su ba ?

ما هو صداق مثل هؤلاء إذا لم تخدعهم ؟

yana wajabta sadaki. يستوجب الصداق .

**: Sadaka ← صدقة**

Ya ba shi sadaka. أعطاه صدقة .

Ya sa aka kama rago aka yanka aka yi mini sadaka.

أمَر أن يُمْسك خروف ويذبح ويتصدق لي به .

Masu gidan ku taimake ni da sadaka. يا أهل البيت ساعدوني بصدقة .

**: Sarrafa ← صَرَّفَ**

تأتي بمعنى التصرف أو التحكم

Linzami yana sarrafa doki. اللجام يتحكم في الحصان .

Tana sarrafa mijninta. تتحكم في زوجها .

Yana sarrafa kuɗinsa. يتصرف في ماله .

**: Siraɗi أو Siratsi ← صراط**

Hakika siratsi gaskiya ne. إن الصراط حق .



www.alkottob.com

Ba wani abu a ƙarƙashin siraɗi sai Jahannama.

ليس تحت الصراط إلا جهنم

Allah tsallakad da mu siradi ranar ƙiyama.

اللهم اعبر بنا الصراط يوم القيامة

## صاع ← Sa'i :

Ya yi wanka da sa'i.

اغتسل بصاع .

Sa'i shi ne mudu huɗu na irin mudunnabi.

الصاع هو أربع مدٌّ من مثل مد النبي

Kwando guda daidai yake da sa'i sittin.

الوسق يساوى ستين صاعاً .

Za'a ba da sa'i guda ga kowace mutun.

يُعطى صاع واحد لكل إنسان .

## صف ← Sahu :

Aka fita aka yi sahu.

خرجوا وكونوا صفًّا .

'Yan bindiga duk su yi sahu.

الرماه كونوا صفًّا .

Allah yana zuwa ranar Alƙiyama alhali mala'ikansa sun yi sahu-sahu.

يجيء الله يوم القيامة وملائكته صفا صفا .

Babu laifi idan an jera gawaye cikin sahu guda wajen yi musu salla.

لابأس إذا صفت الجثث في صف واحد عند الصلاة عليها .

## صفا ← Safa :

Ya fita zuwa Safa ya tsaya a kanta ya yi addu'a.

خرج إلى الصفا ووقف عليها ودعا .

Yana tsaya sau huɗu a kan Safa.

وقف أربع مرات على الصفا .



www.alkottob.com

## صفة ← Siffa :

### تأتي بمعنى شكل

Siffar wurin duk ta sake. شكل المكان كله تغير .

Ya taimake shi ya mai da shi siffarsa na asali.

ساعدة وأرجعة إلى شكله الأصلي .

Ba dama su koma gari cikin wannan siffa.

لا فرصة ليعودوا إلى المدينة في هذا الشكل .

Siffofi maɗaukakiya sun tabbata gare shi. لهُ الصفات العُلَى .

Bai gushe ba ga dukan siffofinsa da sunayensa.

لم يزل بجميع صفاته وأسمائه .

Tsoho yana sifanta masa shi. وصفه العجوز له .

Ba zan iya sifanta shi ba , domin da na gan shi.

لن استطيع أن أصفة لأني رأيته منذ مدة .

## صِفْر ← Sifiri :

Kullum in an koya masa aiki , shi sai ya yi ta wasa sai ya sami sifiri.

دائما إذا علِّم عملا ، يلعب كثيرا ويأخذ صفرا .

Ko kuwa sai na tashi jarraba ku kuma ka ci sifiri ?

وإذا قمت واختبرتكم تأخذ صفرا ؟

## صَفَر ← Safar :

Yau kin ga sha biyu ga watan Safar. اليوم تعرفين أنه الثاني عشر من شهر صفر

Zan yi aure a cikin watan Safar. سأتزوج في شهر صفر .

Watan Safar yana daga cikin watannin hijira.

شهر صفر من أشهر السنة الهجرية .



www.alkottob.com

## : Salla ← صلّى

### تأتي بمعنى الصلاة أو العيد

Tun fitarsa da safe , ba su dawo ba sai bayan sallar azahar.

منذ خروجه في الصباح لم يعودوا إلا بعد صلاة الظهر .

Da isarsa ya tarad da shi ya gama salla walaha yana wuridi.

عند وصوله وجده أنهى صلاة الضحى ويقرأ الورد .

Me nake ji haka kamar kiran salla ? ماذا أسمع كنداء الصلاة ؟

Ya sayad da wani jaki nasa jiya don ya yi sha'anin salla.

باع حمارة أمس ليشترى حاجات العيد .

Ran nan safiyar salla sarki ya yi shiri zai fito ya hau zuwa idi.

ذات يوم في صباح العيد أستعد الأمير ليركب ويخرج إلى العيد .

Yau kun ga ɗaya ga watan salla babba na sallame ku.

اليوم تعلمون واحد من شهر العيد الكبير أودعكم .

Sun kunna fitila suna ƙirgar dukiya don gobe salla.

أشعلوا المصباح ، يعدون المال لأن غدا العيد .

Yana sallar la'asar. يصلي العصر .

Duk musulmi suka yi salla. كل المسلمين صلوا .

Na yi sallar azahar nan gida. صليت الظهر في المنزل .

Zasu yi masa sukuwar salla. سيهجمون عليه .

## : Salati ← صلاة

### الصلاة على الرسول ﷺ

Mu yi salati bisa ga fiyayyen talikai. صلينا على أفضل الخلق .

Na rungume shi ina salati. عانقته وأنا أصلى على النبي ﷺ

Ko da na ji haka sai na yi salati. عندما سمعت ذلك صليت على الرسول ﷺ



www.alkottob.com

Ka yi salati har sarki ya ba da izini in isad da kai.

صلى على النبي ، حتى يأذن الأمير لأدخلك .

## : Suluhu ← صُلْحٌ

Suka yi suluhu da turawa. عقدوا صلحا مع الأوربيين .

Mun soma ba da kai suluhu. بدأنا نستسلم .

Ya ƙulla suluhu da sarki Audu. عقد صلحا مع الأمير عبده .

Muna cikin suluhu haka me ruwammu da wani shirin mayaƙa ?

نحن هكذا في صلح ماشأننا وإعداد المقاتلين ؟

## : Salihi ← صالح

Irin waɗannan ayyuka naka ai kai har yanzu salihi kake.

أعمالك هذه حتى الآن صالحة .

Musa salihin mutum ne. موسى رجل صالح .

In ka samu salihar mata ka huta. إذا وجدت امرأة صالحة استرحت .

A cikin larabawa akwai salihan mutane. في العرب يوجد أناس صالحون .

## : Sandal ← صندل

خشب الصندل

Ka sayo mini turaren sandal in ka je kasuwa.

اشترلي رائحة الصندل إذا ذهبت إلى السوق .

Sandal turare ne na asali. الصندل رائحة أصلية .

Na shafa sandal a rigata. عطرت ثوبي برائحة الصندل .



www.alkottob.com

: **Sunduƙi** ← صندوق

صندوق أو خزانة المال

Hukuma ta cika sanduƙinta da kuɗi. ملأت الحكومة خزانتها بالمال

Na sa suturata a cikin sunduƙi. وضعت سترتي في الصندوق

Wnnan sunduƙi ya tsufa. هذا الصندوق صار قديما .

: **Sana'a** ← صناعة

Dan kirki daga karatu sai aiki ko koyon sana'a.

الولد الطيب من العلم إلى العمل أو تعلم الصناعة .

Ba su san wata sana'a ba daga farauta sai neman zuma.

لا يعرفون صناعة إلا الصيد وجني العسل .

Ba ni da wata sana'a sai su. ليس لي صناعة إلا الصيد .

An ce noma shi ne asalin sana'o'i. يقال أن الزراعة أصل الصناعات .

Mun ji labarin wadansu kabilu da al'adarsu da yadda suke sana'o'insu. سمعنا قصة بعض القبائل وعاداتهم وكيف تكون صناعاتهم .

: **Sawaba** ← صواب

Mai girman kai ba ya yarda sawaba. المتكبر لايوافق على الصواب .

In kana kan kuskure , in ka ga sawaba sai ka bar kuskure.

إذا كنت على خطأ إذا ورأيت الصواب أترك الخطأ .

Ba mai shiryad da kai zuwa sawaba sai mai ƙaunarka.

لا يهديك إلى الصواب إلا حبيبك .

: **Sauti** ← صوت

Na ji sautin bandiri. سمعت صوت بندير .



www.alkottob.com

Na ji wani ƙaƙƙarfin sauti daga sama. سمعت صوتا عاليا من السماء .
Sautin rediona ba ya fito sosai. صوت مذياعي لا يخرج جيدا .
Na ji sautin bindiga na tashi. سمعت صوت بندقية ينطلق .

## صورة ← Sura :

Ya ja sura. رسم صورة .
Ya ta da kai zai dube su , sai suka fito masa da surarsa sosai.
رفع رأسة سينظر إليهم فظهروا له بصورتهم الحقيقية .
An ƙi yin surori a jikin gidaje da kuma ƙubbobi.
تُكْرَه الصور في الأسرة والقباب .

## صوم ← Azumi :

Bai halatta ga mai haila ba ta yi salla ko azumi.
لا يحل للحائض أن تصلي أو تصوم .
Zata rama azumin da ta sha da haila. ستقضى الصوم الذي فاتها بسبب الحيض .
Azumin watan Ramalan farilla ne. صوم شهر رمضان فريضة .
Yin niyya kullum ba tilas ba ne ga mai yin azumi idan har a farke ya yi niyyar kan cewa zai azumci watan.
النية كل يوم ليس ضرورة للصائم ، إذا نوى في أول يوم أنه سيصوم الشهر .

## صوفي ← Sufi :

Sufi ɗan baiwar Allah. الصوفي ابن أمة الله .
Imamu Musa babban sufi ne, الإمام موسى صوفي كبير .
Ba duk maganar sufaye ake karɓa ba. ليس كل كلام الصوفيين يؤخذ به .
Asalin sufanci kyakkyawan abu ne. أصل الصوفية شيء جميل .

★★★



www.alkottob.com

# الضاد

## ضحية ← Layya :

Liman zai fita zuwa masallaci tare da abin layyarsa.

سيخـرج الإمام إلى المصـلى بأضحيته .

Layya sunna ce a kan wanda yake da iko. الأضحية سُنّة على من يستطيعها .

Bai halatta ba yin layya da dabba mai ido ɗaya , ko mara lafiya.

لا تجوز التضحية بالدابة ذات العين الواحدة أو المريضة .

An so ga mutum ya yanke layyarsa da kansa.

يستحب للإنسان أن يذبح أضحيته بنفسة .

## ضرورة ← Larura :

Gyara murya don larura shi ma an yafe. غفر التنحنح للضرورة .

Larura tana halatta abin da aka haranta. الضرورة تُجِيز ما حُرِّم .

Im ba larura ba , me zai kai ni asbiti ?

إن لم تكن الضـرورة ، ماذا يحملني إلى المستشفى ؟

Ilmin mata larura ne ga ƙasa. عِلْم المرأة ضرورة للبلد .

## ضمير ← Lamiri :

Sai ka sa lamirin mace a maimakon lamirin namiji.

يجب أن تضع ضمير المؤنث بدلا من ضمير المذكر .



www.alkottob.com

## : Lamuni ← ضامن

Karenka ya yi wa 'yan uwansa lamunin ragona ya rarrabe su , har yanzu bai tattara mini kuɗina ba.

كلبك قدم لأخوته ضمان لخروفي ووزعة عليهم ، حتى الآن لم يجمع لي الثمن .

Shari'a ba ta daure shi ba , amma kai ne mai lamuninsa.

الشريعة لا تحبسة ، ولكن أنت ضامنه .

Ba ya lamunce ramuwar abin da ba a iya ɓoye shi.

لا يُضْمَن مالا يُغاب عليه

Ya lamince biyanta.

ضمن دفعة .

Idan ya halaka kafin shekara ko bayanta , ba zai lamince bayanta ba.

إذا هلكت قبل سنة أو بعدها ، لم يضمنها بعدها .

## : Liyafa ← ضيافة

Kullum wai mutanen da nake kira ina yi musu liyafa don riya ce.

كل يوم أدعو الناس واستضيفهم رياءً .

Ba na zo nan ba ne , don dukiyarka ko in ci liyafa.

لم آت هنا من أجل مالك أو لاستضافتي .

★★★



www.alkottob.com

# الطـاء

## طب ← Dibbu أو T'sibbu :

الكلمة الأولى تعني الطب والثانية تعني التنجيم

Na gamu da wani malamin ɗibbu. — التقيت بأحد أساتذة الطب .

Malaman dibbu suna da yawa a Masar. — علماء الطب كثيرون في مصر .

Mata suka fi yarda da tsibbace-tsibbace. — المرأة أكثر الناس رضا بالتنجيم .

Duk matsibbace maƙaryaci ne. — كل المنجمين كذّابون .

Asalin malamin tsibbu sun fito daga Maroco.

اكـثر علـماء التنجيم جاءوا من المغرب .

## طوب ← Tubali :

Sarkin ƙasa ya sa tubalin farko na ginin jami'a.

أمير البلد وضع أول طوبة في بناء الجامعة .

Da kadan kadan tubali yake zama gida. — رويدا رويدا الطوبة تصير منزلا .

Ina son tubalin ginin gidana. — أريد طوبا لبناء منزلي .

## طابور ← Dabur :

تأتي بمعنى طابور أو أصرَّ

Suja sun yi dabur. — الجنود وقفوا في الصف ثابتين .

Wani jarumi ya yi dabur a filin daga. — شخص شجاع وقف ثابتا فيميدانالقتال.

Na hana dana tafiya suja amma ya daburce sai ya je.

منعت ابني من الذهاب إلى الجيش ولكنه أصر على الذهاب .



www.alkottob.com

## : Tabi'a أو Dabi'a ← طبيعة

تأتي بمعنى طبع أو عادة

Ya ga dai a irin shigar dạ ya yi kamar sarkinsu ne , amma ga shi a ɗabi'a da murya kamar ba shi ba.

رأي أن دخوله كدخول أميرهم ولكن هاهو له طبع وصوت كأنه ليس هو .

Kalalatu ba ta ƙaunar wannan ɗabi'a ta mijinta.

كلالة لا تحب طبع زوجها هذا .

Ka daina wannan muguwar ɗabi'a. اترك هذه العادة السيئة .

Wadansu mutane tsabta ta kan zama dabi'a ce a gare su.

بعض الناس تصير النظافة عادة لديهم .

Ya ga irin gidanjen garin da dabi'un mutane na game da zamansu.

رأي شكل منازل المدينة وعادات الناس في حياتهم .

Ta yi , ta yi ta hana shi wannan tabi'a ya ƙi hanuwa.

حاولت كثيرا أن تمنعة هذه العادة فرفض الإمتناع .

Tabi'o'insu duk da maganarsu da launin jikinsu kamar na mutanen Sudan. عاداتهم كلها وكلامهم ولون جسمهم مثل أهل السودان .

## : Darika ← طريقة

Kai wallahi kuwa shi wata irin darika yake bi.

والله هي نفس الطريقة التي يتبعها .

Saboda me ? Don yana bin darika ɗin ? لماذا؟ لأنه يتبع هذه الطريقة؟

## : Tasa ← طاسة

Wata rana wani ɓarawo ya tafi ya yi satar tasa.

ذات يوم ذهب لص وسرق طاسة .

Da ranar kasuwa matar ta wanke tasar ta tafi da ita kasuwa.

في يوم السوق غسلت المرأة الطاسة وذهبت بها إلى السوق .



www.alkottob.com

Ya ƙai shi wurin wata tasa cike da toyẹ - toye.

أوصلة إلى مكان طاسة مملوءة باللحم المحمَّر .

Daga cikin tasoshin nan waɗansu murabba'a waɗansu da'irori.

بعض هذه الطاسات مربع والبعض مستدير .

## : Taga ← طاقة

تأتي بمعنى النافذة

Aku ya duba ta taga sai ya ga hadari ya taso.

نظر الببغاء من الطاقة فرأي العاصفة هبَّت .

Ya tarad da taga buɗe , ga fitila na ci kamar rana.

وجد النافذة مفتوحة والمصباح مشتعل كأنه الشمس .

Za'a bar waɗansu 'yan tagogi inda zai riƙa hanga.

ستترك بعض النوافذ حيث يطل منها .

In na tashi da safe na kan buɗe tagogi duka.

إذا قمت في الصباح أفتح كل النوافذ .

## : Dalibi ← طالب

Ni dalibi ne mai ƙoƙari. أنا طالب مجتهد .

Na aure wata ɗaliba mai karatu a jami'a. تزوجت طالبة تدرس في الجامعة .

Ɗaliban da suke karatu a Makka ba su shan wahala.

الطلاب الذين يدرسون في مكة لا يجدون صعوبة .

## : Tambura ← طمبورة

نوع من الطبول

Na ji aka buga mini tambura. سمعت تدق لي الطبلة .



www.alkottob.com

Kai tamburin aljannu da ɗaɗi. دق طبول الجن جميل .

Ya sa aka buga mini tambura tun da safe har azahar.

أمر أن تدق لي الطبلة منذ الصباح حتى الظهر .

## : Tumatir ← طماطم

Watakila za su sha rake da tumatir da lemon zaƙi.

ربما شربوا عصير القصب والطماطم والليمون الحلو .

Ga tumatir an yi masa darni. هاهي الطماطم أقيمت لها الحوامل .

Ya sa nama da tumatir da albasa. وضع اللحم والطماطم والبصل .

## : Dahiri ← طاهر

Wannan ruwan ɗahiri ne. هذا الماء طاهر .

Na yi ɗahara da ruwan dahiri. تطهَّرت بماء طاهر .

Kada ka yi salla a kan wannan tabarmar don ba ɗahira ba ce.

لا تصلي على هذه الحصيرة لأنها غير طاهرة .

Aka shaida mu dahirai ne. قيل لنا أننا أطهار .

Zata faye dauɗa har bai kamata ba ɗahirai ba kamarsu su zauna ciki.

ستكون قذرة جدا فلا ينبغي الأطهار وأمثالهم أن يجلسوا فيها .

## : Dawafi ← طواف

Bai halatta ga wanda ba ya da alwalla ba ya yi dawafi.

لا يحل لغير المتوضيء الطواف .

Ɗawafi shi ne kewayon ɗakin Allah watau Ka'aba.

الطواف هو الدوران حول بيت الله أي الكعبة .

Wanda ya yi taimama zai iya yin ɗawafi. من يتيمم يستطيع الطواف .



www.alkottob.com

# الظاء

## : Zarafi ← ظَرْفٌ

تأتي بمعنى أمر أو شأن أو عرض

Yana da wani aiki ne , har shi ma idan yana da zarafi yana so ya zo yo taimake shi. لدية عمل ، وهو أيضا إذا كان لدية ظرف ويريد المساعدة جاء وساعدة .
Akwai wani zarafi da nake so in yi a Masar. يوجد أمر أريد قضاءه بمصر .
Kar ka shiga cikin zarafina. لا تتدخل في أمري .
Ba na son mutum mai cin zarafin mutane.

لا أحب الرجل الذي يهتك عرض الناس .

## : Azzalumi ← ظالم

Duk sarakunan duniya nan babu azzalumi irinku.

كل أمراء هذه الدنيا لا يوجد ظالم مثلكم .

Sarki ya dubi hauni ya ce «a ba ni kan wannan azzalumi».

نظر الأمير إلى السياف وقال «اعطني رأس هذا الظالم» .

Ga shi abin da kika jawo mana lalatacciyar wofi azzaluma.

ها ما جلبتينة لنا فاسدة ظالمة .

Dila ya ce : Manyan azzalumai biyu ne , Allah ya halitta a duniya daga ubanka sai kura. قال الثعلب : كبار الظالمين في الدنيا أثنان خلقهما الله، أبوك والذئب .
Nan wurin zuwan talakawa ne , ba na azzalumai.

هنا مكان حضور الشعب ، وليس الظالمين .

Mayar da kayan zalunci da nisantar ayyukan haram suna cikin tuba.

رد المظالم واجتناب المحارم من التوبة .

Shi ba ya zalunci , ba shi kuwa son mai zalunci.

لا يظلم، ولا يحب الظالم .



www.alkottob.com

Ka hana zalunci , amma ṣu har yanzu ba su bari ba.

منعت الظلم ، لكنهم حتى الآن لم يتركوه .

Allah ya kyashe mu da cin amana da zalunci.

وقانا الله من خيانة الأمانة والظلم .

## الظُّهْر ← Azahar :

Na yi sallar azahar nan gida. صليت الظهر هنا في المنزل .

Farkon lokacin la'asar shi ne ƙarshen lokacin azahar.

أول وقت العصر هو أخر وقت الظهر .

Tun da azahar muke jiran isowarsa. منذ الظهر ننتظر وصولة .

Azahar na yi sai ga sarki ya aiko ɗan bushara an ci nasara.

حان الظهر وإذا بالأمير يرسل مبشِّراً بأنه انتصر .

Tun azahariya fari ne ya cika. مات منذ الظهرية .

## ظاهر ← Zahiri أو Dahiri :

Yanzu ai zahiri ne ita ce bora. الآن أصبح ظاهرا أنها الزوجة المكروهة .

Wannan abu ai a zahiri yake ga duk mai basira.

هذا الأمر صار ظاهراً لكل ذي بصيرة .

Wannan dahiri ne. هذا ظاهر .

Wannan magana dahiri ce. هذا الكلام ظاهر .

★★★



www.alkottob.com

# العـين

## عبادة ← Ibada :

Ni yanzu ba na wani aiki sai ibada. — أنا الآن ليس لي عمل إلا العبادة .

Musa ba abin da ya sa gabansa sai ibada. — موسى لم يجعل أمامة شيئا سوى العبادة .

Shekara saba'in a nan ina ibada. — قضيت سبعين سنة هنا في العبادة .

Na yi ibada ba dare ba rana. — أعبد ليلا ونهارا .

In ya tashi da safe ya yi ibada ga Allah. — إذا قام في الصباح يعبدالله

## عُتْمَة ← Atamati :

Sallar atamati ita ce sallar lisha. — صلاة العتمة هي صلاة العشاء .

## عجب ← Al'ajabi أو Ajaban :

Masasaƙi ya riƙe baki ya ga al'ajabi. — أمسك النجار فمة متعجبا .

Ga wani abin al'ajabi. — ها شيء عجيب .

Ya ga abin al'ajabi. — رأي شيئا عجيبا .

Ɓarayi suka dubi jaka suka yi ta al'ajabi. — نظر اللصوص إلى الحقيبة وهم يعجبون كثيرا .

Suka kewaye ta suna al'ajabi. — أحاطوها وهم يتعحبون .

Ajaban budurwa da ciki. — عجبا عذراء حامل .

## عجوز ← Ajuzi :

Ka yi aure da wuri kafin ka zama ajuzi 'yan mata ba su sonka. — تزوج بسرعة قبل أن تصير عجوزا فترفضك البنات .



www.alkottob.com

Matarka ta zama ajuza sai ka auri wata.

زوجتك صارت عجوزا يجب أن تتزوج أخرى .

Na hangi fadar ajuzai ta cika. رأيت مجلس الشيوخ امتلأ .

**عجلى ← Ujila :**

تأتي بمعنى متعجل

Don Allah ka yi maza ka ƙare in tafi, ujila nake yi.

بالله أسرع وانته لأذهب ، أنا متعجل .

Ni ba zan karɓi ɗinkinka ba sabo da na san ujilarka.

لا آخذ خياطتك لأني عرفت أنك متعجل .

Zan biya Musa bashinsa in huta da ujilar sa.

سأدفع لموسى أجرة لأرتاح من تعجلّه .

**عجمي ← Ajami :**

تعني الخط العربي

Rubutun ajami yana da wuyar karantawa ga wanda bai san shi sosai ba. كتابة الخط العربي صعب قراءتها على من لم يعرفها جيدا .

Na karanta littafin «ajami da larabaci».

قرأت كتاب « العجمية والعربية » .

**عيد ← Idi :**

Da aka sauko daga idi sai na fita waje yawo.

عندما انتهوا من صلاة العيد خرجت لأتجول .

Sallar idi biyu sunna ce. صلاة العيدين سنة .

Ya yi shiri zai fito ya hau zuwa idi. استعد ليخرج ويركب إلى العيد .



www.alkottob.com

can da hantasir fari sai ya ga ladan ya fito da takalma da sanda zashi idi. بعد الضحى وإذا بالمؤذن يخرج بحذائة وعصاة متوجها لصلاة العيد

## عدة ← Idda :

Babu aure cikin idda. لا زواج في عِدَّة .

Ba ta cika ida ba. لم تكمل العدة .

Ya sake aurad da ita bayan ta yi idda wata uku ke nan. زوجها مرة أخرى بعد أن أتمت عدة الثلاثة أشهر .

## عادة ← Al'ada أو La'ada أو Ta'ada :

تعنى عادة أو بقشيش

Suna da wata al'ada su kan taru su riƙa yawo.

عندهم عادة وهي أن يجتمعوا ويتجولوا .

Na ɗauko AlƘur'ani, ina dubawa kamar al'adata sai barci ya share ni.

أخذت القرآن ، أنظر فيه كعادتي حتى يغلبني النوم .

Nan da nan sai ya yi al'adar da ya gaya masa.

وفي الحال فعل العادة التي حدثه عنها .

Mun ji labarin waɗansu ķabilu da al'adunsu.

سمعنا قصة بعض القبائل وعاداتها .

Ya ci na ɗaya a gasar nuna al'adun gargajiya.

كسب المركز الأول في سباق الفنون الشعبية .

Ya yi musu ƙari , suka sallama ya kawo la'ada ya ba su.

زادهم ، فوافقوا ، أحضر العادة ــ البقشيش ــ وأعطاهم .

Na saya ashirin biyu babu la'ada ciki.

اشتريت باثنين وعشرين وليس فيهم العادة .

Ni na san dabarar da na yi , na mayar musu doki su ba ni kuwa la'adata. اعرف حيلة أعملها ، فأعيد لهم الحصان ويعطوني البقشيش الذي دفعته .

Ba shi da wata ta'ada sai karanta. ليس له عادة إلا القراءة .



www.alkottob.com

## : Adadi ← عدد

Bai san adadin raka'o'in da ya sallata. لم يعرف عدد الركعات التي صلاها .
Babu zakka ga wanda rabonsa bai kai adadin zakka ba.
لا زكاة على من لم تبلغ حصته عدد الزكاة .
Idan sun kai wannan adadi za a ba da tinkiya 'yar shekara ɗaya.
إذا بلغوا هذا العدد يعطى شاة بنت عام واحد .
Da adadinsa ya cika ya tafi wurin alƙali ya roƙe shi gafara.
عندما اكتمل عددها ذهب إلى القاضي وسأله المغفرة .

## : Adali ← عدل

Ko da mutane suka ga adalin sarkinsu na da sai duk murna ta cika garin. عندما رأي الناس عدل أميرهم القديم ، ملأ السرور كل المدينة .
Sarkin nan fa yadda nake ji , ana faɗa duk inda adali ya kai , ya kai.
هذا الأمير كما سمعت ، يقال حيثما كان العدل هو يكون .
In ya yi kokanta a cikin labarinsa , to , sai ya tambayi adali biyu.
إن شك في خبرة يسال عَدْلين .
Ba a karɓar shaida sai daga adali. لا تُقْبل الشهادة إلا من عدول .
Ya ɓatad da wanda ya wulakantad da adalcinsa. أضل من خذله بعدله.
Idan ka ga sarakuna sun tsaya wa adalci , sun bar zalunci faɗa da su yana da wuya. إذا رأيت الأمراء، وقفوا مع العدل ، وتركوا الظلم القتال معهم يكون صعباً.
Su yi masa godiya bisa ga wannan adalci da ya yi.
شكروة على هذا العدل الذي أقامة .

## : Azaba ← عذاب

Za'a shigad da su cikin azaba mai tsanani.
سيدخلهم في عذاب شديد .
Muna tsoron azabarka. نخشى عذابك .



www.alkottob.com

Ina neman tsari da kai daga azabar wuta. أعوذ بك من عذاب النار .

In na azabtad da shi yadda zai sheƙi ƙanshin mutuwa.

إذا عُذِّب سيشم رائحة الموت .

### عذر ← Uziri :

Babu laifu game duban ga yarinya don wani uziri.

لا بأس من النظر إلى الفتاة لعذر .

Na gaya wa malamina yau ba zan halarci karatu ba sabo da ina da uziri. قلت لأستاذي اليوم لن أحضر الدرس لأنه لدي عذر .

Ba zan karɓi uzirinka ba , sabo da na san maƙaryaci kai ne.

لن أقبل عذرك لأني عرفت أنك كاذب .

Ba wanda ba ya karɓar uziri sai shaidan.

لا أحد لا يقبل العذر إلا الشيطان .

### عربية ← Larabaci :

Ni yanzu a ƙalla na san kalma ta kusa talatin a cikin larabaci.

الآن أعرف على الأقل ثلاثين كلمة تقريبا في اللغة العربية .

Sun saye da tufafi irin na larabawa sun yi shigar alhazai.

اشتروا ثيابا مثل ثياب العرب ودخلوا مع الحجاج .

Ga shi dai kana da sani da lafazi irin na larabawa.

ها لك معرفة وأسلوب مثل العرب .

### عرش ← Al'arshi :

Shi ya rinjayi al'arshinsa mai girma da zatinsa.

هو يعتلي عرشة المجيد بذاته .

Ba wanda ya san mala'ikan al'arshi sai Allah.

لا أحد يعرف ملائكة العرش إلا الله .

Allah ya sa mu a ƙarƙashin al'arshinsa ranar ƙiyama.

نسأل الله أن يجعلنا في ــ ظل ــ عرشة يوم القيامة .



www.alkottob.com

## عَرَض ← Arala :

### تأتي بمعنى يحدث

Ya siffanta wa sani irin makiricin da zai yi wannan abu ya arala.

وصف لساني المكر الذي يفعله ليحدث هذا الأمر .

Bayan na tashi daga aikin an aralu mini da sallar jana'iza.

بعد أن تركت العمل أديت صلاة الجنازة .

Rigingimu sun aralu mini a wannan shekara. عرضت لي مشاكل في هذا العام .

## عِرْض ← Irli :

'Yan dokan nan sun karya mini irli.

هؤلاء الجنود سبوني في عِرْضي .

Alti sai da irli domin wuri. ألتي يبيع عرضه من أجل المال .

An ci irlinsa. هُتِك عرضه .

An keta irlinsa. مُزِّق عرضه .

Iyalin mutum su ne irlinsa. أسرة الرجل عرضه .

In ka kiyaye irlinka ba mai taka shi. إذا حافظت على عرضك لا يطأه أحد .

## عروض ← Urula :

Urula ita ce dukiya kamar gidaje da gonaki da bayi.

العروض هي الثروة مثل المنازل والمزارع والعبيد .

Ba a yin zakka ga urula sai in ta zamanto ta fatauci.

لا يُزَكِّي على العروض إلا إذا صارت للتجارة .

## عرفة ← Arafa أو Arafat :

Wankan Arafa sunna ce. غُسْل عرفة سُنَّة .



www.alkottob.com

Kwana a Mina daren ranar Arafa sunna ce.

المبيت بمنى ليلة يوم عرفة سُنَّةٌ .

Ya wuce zuwa Arafa.

مضى إلى عرفة .

Ya tafi zuwa masallacin Arafa a ranar Arafa.

ذهب إلى مصلى عرفة في يوم عرفة .

Yin azumi ranar Arafat nafila ce.

صيام يوم عرفات نافلة .

**عارية ← Aro :**

Aro abin mayarwa ne.

العارية مؤداة .

Bayan aro kuwa , ba a gaskata shi game da halakarsa , game da wanda ake iya ɓoye shi.

العارية لا يُصدق في هلاكها ، فيما يغاب عليه .

Ya ba da aron riga.

أعار القميص .

Ko ina mai aro za shi , da sanin mai riga.

حيثما يذهب المستعير (للقميص) يكون بعلم صاحب القميص .

Abin aro ba ya rufe katara.

المعار لا يستر العورة .

Ba a aron bakin mutum a ci masa albasa.

لايعار فمالإنسانليأكلالآخر به البصل.

**عريان ← Uryana :**

Na ga mahaukacin yana yawo uryana.

رأيت مجنونا يسير عريانا .

Kar ka bar danka ya tafi waje uryana.

لا تترك ابنك يخرج عريانا .

Kafin musulunci ya zo larabawa uryana suke yin ɗawafi.

قبل الإسلام كان العرب يطوفون عرايا .

**عِزّة ← Izza :**

Yau kuma ina izzar taki?

اليوم أين عزّتك ؟

Duk izzarka in ba ka da ilmi Banza ne ka yi.

كل عزتك لا فائدة إن لم تنل علماً .

Musa don ya sami kuɗi sai izza yake wa mutane.

لينال موسى المال يجب أن يحترم الناس .



www.alkottob.com

## عزم ← Azama :

تأتي بمعني عزم أو نوى

Ka yi azama ka tafi makaranta. اعزم على أن تذهب إلى المدرسة .

Na ga Musa ya yi aẕamar girbe da dawarsa.

رأيت موسى يعزم على حصاد دخنة .

Ibrahimu mutum ne mai azama a kan aikinsa.

إبراهيم رجل ذو عزم في عملة .

## عِشاء ← Isha'i أو Lisha'i :

Wanda ya yi sallar isha'i da taimaman sai ya tashi ya yi shafa'i da witiri bayansa. من صلى العشاء بالتيمم يقوم ويصلى الشفع والوتر بعدها .

ZaɓaɓBen lokacin isha'i tun daga fakuwan shafiƙi zuwa sulusin dare na farko. الوقت المختار لصلاة العشاء من مغيب الشفق إلى ثلث الليل الأوّل .

Kafin lisha ta yi duk namiji da ke garin yana bayan gari wajen nemona. قبل حلول العشاء كل رجل في المدينة كان خارجها يبحث عنى .

Da dare bayan lisha wata mace ta rasu. في الليل بعد العشاء ماتت امرأة .

Ya shiga fada lisha. دخل القصر عِشاءً .

## عُشْرٌ ← Ushira :

Aka cire ushira aka ba yaro sauran. أخذ العُشر وأُعطى الولد الباقي .

Aka yi musu kimma aka cire ushira. حددت قيمتهم وأُخذ العشرُ .

Na biya kuɗin ushira a kotu. دعفت غُشر المال في المحكمة .

Ni ban san ushiri hakkin wane ne ba a cikin gado.

لم أعرف العُشْر حق مَنْ في الميراث .

## عشرين ← Ashirin :

Daga ashirin zuwa ashirin da huɗu za'a ba da awaki huɗu.

من عشرين إلى أربعة وعشرين يُعطى أربع شياة .



www.alkottob.com

Zai ba ni shanu ąshirin. سيعطيني عشرين بقرة .

Aukiya ɗaya kuwa daidai take da darhimai ashirin.

أوقية واحدة تساوي عشرين درهماً .

### : Ashura ← عاشوراء

Yin azumi ranar ashura nafila ce. صيام يوم عاشوراء نافلة .

Azumin ashura yana da falala mai yawa. صيام عاشوراء له فضل كبير .

Na yi azumi ranar ashura. صمت يوم عاشوراء .

Ban samu damar yin azumin ashura ba a wannan shekarar.

لم أجد فرصة لصيام عاشوراء هذا العام .

### : Asibai ← عَصَبَة

'Yan uwa mata tare da 'ya'ya mata kamar asibai ne garesu.

الأخوات مع البنات كالعصبية لهن .

Majiɓincin ba ya gado tare da asibai. لا يرث المولى مع العصبية .

### : La'asar ← عَصْر

A cikin la'asar ne da magariba ai a taƙaita karatu.

في العصـر والمغرب تُقَصَّر القـراءة .

Farkon lokacin la'asar shi ne ƙarshen lokacin azahar.

أول وقت العصر هو نهاية وقت الظهر .

In la'asar ta yi sai mu tafi tare mu duba.

إذا حان العصر نذهب معاً لنرى .

Da la'asar ta yi, ya tuna inda ya zubad da shi.

إذا حان العصرو تذكر أين صبة .

In ba ki bar gidan nan ba, kafin la'asariya gobe to, zan zo in fid da ke da ƙarfi. إن لم تتركي هذا المنزل قبل غد العصرية سآتي وأخرجك بالقوة .



www.alkottob.com

## : Atishawa ← عطش

Wanda ya yi atishawa cikin sallarsa kada ya shagala da cewa «alhamdu lillahi».

من عطس في صلاته لا ينشغل بقوله «الحمد لله» .

Ya yi atishawa.

عطس .

Wanda ya yi atishawa sai ya ce «alhamdu lillahi».

من عطس يجب عليه أن يقول «الحمد لله» .

Ya yi miƙa ya yi atishawa sau uku ya yi hamdala.

تمدد وعطس ثلاث مرات وحمد لله .

## : Alas ← عَلَسُ

Alas wata ƙwaya ce wacce take kama da ƙwayar burri.

العلس هو حب صغير يشبة حبة البر .

Idan Alas shi ne abincin mutanen garin sai a fid da ita daga zakka.

إذا كان العلس قوت أهل المدينة أخرجت منه الزكاة .

## : Ilmi ← عِلْمٌ

Neman ilmi farilla ce.

طلب العلم فريضة .

Ilmin da ba zai yi amfani ba , kuma jahilicin da ba zai yi cuta ba.

عِلْم لا ينفع وجهالة لا تضر .

Malam ya kawo waɗansu litattafan ilmi ya ba ni.

الأستاذ أحضر بعض كتب العلم وأعطاني إياها .

Ya yi suna a kan ilmi da wayo da fasaha.

له شهرة في العلم والذكاء والفصاحة .

Basira da ilmi da wayo su ne kaɗai bambancimmu da dabbobi.

البصيرة والعلم والذكاء هي وحدها التي تفرقنا عن الحيوانات .



www.alkottob.com

### : Illa ← علة

سبب أو مرض

Yin jama'insa don wata illa da ke tare da shi. جَمْعة لعلة فيه .
Kwaya tana yi wa kwakwalwa illa. الحبوب المخدرة تسبب العلة للمخ .
Kar ka sha giya don kar ka yi wa jikinka illa.
لا تشرب الخمر حتى لا تسبب لجمسك علة .

### : Alama ← علامة

تأتي بمعنى علامة أو دليل أو أثر

Na share ƙasa sai ka ce mai shirin haɗɗi na zana wata alama.
كنست الأرض كضارب الرمل ، ورسمت علامة .
Mun ga alama a hanya. رأينا علامة على الطريق .
Da Musa ya ji alamar bayi sun yi barci ya tasam ma wajen Aku.
عندما أدرك موسى أن العبيد ناموا قصد مكان الببغاء .
Iliya ya ga alamar ba su yarda da zancensa ba.
أدرك إلياس أنهم لا يوافقون على كلامة .
Da na ga alamar sun sha wuya na tambaye su dalili.
عندما أدركت أنهم تعبوا سألتهم عن السبب .
Da sarki ya ga alamar ba gaskiya cikin maganarsa ya sa dogarawa su tambaye shi. عندما أدرك الأمير الكذب في كلامة جعل الجنود يستجوبونه .
Ya nuna alamar yana kishinta. أظهر أنه يكرهها .
Ba hanya ba alamarta. لا الطريق ولا أثرة .
Na iya samun alamar gari. استطعت أن أجد أثر المدينة .
Ba gida ko daya a wurin sai waɗansu alamu kawai na bukkoki a nan ne. لا يوجد منزل واحد في المكان إلا بعض الآثار فقط لأكواخ .



www.alkottob.com

Ya sake miƙa hannun guda da kyar ya taɓa shi , sai kuma ya alamta wannan hannun kuma ya miƙa.

مرة أخرى مد يداً بصعوبه ولمسه ، ثم علّم هذه اليد ومدّها .

## : Umura ← عُمْرَةٌ

An umurci mai yin hajji ko umura ya yi wanka yayin ɗaukar harami.

أمر مؤدي الحج أو العمرة أن يغتسل عند الإحرام .

Babi kan aikin hajji da umura. باب في أعمال الحج والعمرة .

Na yi hajji da umura. أديت الحج العمرة .

Tsakanin umura da umura kaffarar zunubi ne.

بين العمرة والعمرة كفارة للذنوب .

## : Inabi ← عنب

Ya yi cinikin zabibi da inabi. يتاجر في الزبيب والعنب .

Na shuka inabi a cikin lambu. زرعت العنب في الحديقة .

Wannan inabin mai zaƙi ne. هذا العنب حلو .

Nawa ne kilon inabi baƙi? بكم كيلو العنب الأسود ؟

## : Inda ← عند

### تأتي بمعنى حيث

Ya nuna masa inda sarki ya ce a gina gida kafin safe.

أراه حيث قال الأمير أن يبني له منزل قبل الصباح .

Zo in kai ka inda zaka huta da wahala.

تعالى لآخذك حيث سترتاح من التعب .

Mu je zuwa inda Allah ya nufu mu je.

لنذهب إلى حيث أراد الله أن نذهب .



www.alkottob.com

## عفريت ← Ifritu :

Muka gama ka da ifritu ya kai ka garin yanzu.

جمعناك بعفريت يحملك إلى المدينة الآن .

Sun yi niyya ifritun nan ya halaka su.

أرادوا أن يهلكهم هذا العفريت .

Na hango wani mutum a koluluwar dutse sai ka ce ifritu.

رأيت رجلا على قمة الجبل كالعفريت .

## عافية ← Lafiya :

Allah ya ba mu lafiya. اللهم هبنا العافية .

Mutanen gida suka yi ta murna saboda mai gida ya dawo lafiya.

أهل البيت فرحوا كثيرا لأن رب البيت عاد سالماً .

Allah ya koma da kai lafiya. أعادك الله سالماً .

Ka gode wa Allah da ya ba ka rai da lafiya.

أشكر الله الذي وهبك الحياة والعافية .

## عقوبة ← Uƙuba :

Ya riƙa tuba ga Allah tun gabanin ya nufi uƙuba a kansa.

يتوب إلى الله قبل أن ينزل العقوبة به .

Shi zai sha uƙuba sakamakon zunubinsa. سينال العقوبة جزاء ذنبة .

## عاقبة ← Aƙiba :

In fitina ta tashi ba wanda ya san aƙibarta sai Allah.

إذا نشبت الفتنة لا يعلم عاقبتها إلا الله .

Ba wanda ya san aƙibar lamarinsa. لا أحد يعرف عاقبة أمرة .

Kyakkyawar aƙiba tana gama su tsoron Allah.

العاقبة الطيبة تجعلهم يخشون الله .



www.alkottob.com

## : **Akasi** ← عكس

Bari in gaya maka akasin labarin da ka bayar.

دعني أقول لك عكس القصة التي قدمتها .

Ba na son ka ringa zuwa mini da akasin abin da nake so.

لا أريد أن تأتيني بعكس ما أحب .

Na sa rigata a bisa akasi. لبست ثوبي بالمقلوب .

## : **Aure** أو **Al'aura** ← عورة

### تأتي بمعنى العورة أو الزواج

Ta isa fada ta nemeta da aure. وصلت إلى القصر وطلبتها للزواج .

Sabili da kuɗinsa ne ya sa na fi son 'yata ta aure shi.

لكثرة ماله جعلتني أحب أن تتزوجه ابنتي .

Ya sake aurad da ita bayan ta yi idda wata uku ke nan.

زوجها مرة أخرى بعد وفاتها عدة الثلاثة أشهر .

Daga sharuɗɗan salla suturcewar al'aura. من شروط الصلاة ستر العورة .

Al'aurar namiji shi ne abin da ke tsakanin cibi da gwiwa.

عورة الرجل هي ما بين السرة والركبة .

Ana ummartar musulmi da rufe al'aura. يؤمر المسلم بستر العورة .

cinya al'aura ce , ammam fa ba kamar al'aura ita kanta ba.

الفخذ عورة ولكن ليس كالعورة نفسها .

## : **Auli** ← عول

Idan waɗanda suka ragu ɗin nan 'yar 'uwa ce ko 'yan 'uwa mata na wajen 'yaye biyu ko uba kurum sai a yi musu auli.

إن كان من بقي أختا أو أخوات لأبوين أو لأب أُعِيل لهن .



www.alkottob.com

Ba a yi wa 'yar 'uwa auli tare da kaka sai a masa'alar da ake kira garra'u.

لا يعال للأخت مع الجد إلا في الغراء وحدها .

## عَيْب ← Aibu أو Laifi :

Dokin nan da aibu , wannan ka saya yana kuwa da aibu.

هذا الحصان فيه عيب ، هذا الذي اشتريت به عيب .

Wannan ita ce mai aibi. هذه فيها عيب .

Wanda ya warke ba tare da aibatawa ba , to babu kome a gare shi.

من شفي بدون عيب لا شيء عليه .

Bai halatta a adaltar da mata ko aibantansu ba.

لا يجوز تعديل النساء ولا إعابتهن .

Idan ba ta yi ba , ba laifi. إذا عملت لا عيب .

Babu laifi ga masu sallar lisha a masallaci su jinkirta ta kadan.

لا بأس ـــ لا عيب ـــ لمصلى العشاء بالمسجد أن يؤخرها قليلا .

## عيال ← Iyali :

Kai ne mai abotata a tafiyar kuma wakilina a cikin iyali.

أنت الصاحب في السفر والخليفة في الأهل .

Yana da iyali suna zuwa daga baya. له عائلة قادمة بعد ذلك .

Ya kwashe iyalinsa ya koma gari. جمع عائلته وعاد إلى المدينة .

Wannan shi ne muhimmi gama dattijo kamarka, bai kamata ya zauna babu iyali.

هذا أمر مهم لعجوز مثلك ، لا ينبغي أن يعيش بلا عائلة .

## عينة ← Ainihi :

Za'a gan shi da ainihinsa. سيراه بعينة .

Ya karɓi hajjarsa idan har za'a iya gane ta ainihinta.

أخذ سلعته إذا أمكن رؤيتها بعينها .



www.alkottob.com

## : Ayyana ← عَيَّن

Sai ka ɗauri aniyar yin sallar da zaka yi ka ayyanta ta.

يجب نية الصلاة التي ستعينها .

Mazaunin gida lafiyayye ba ya yin taimama don sallar janaza sai fa janazar ta ayyana a kansa.

المقيم في المنزل صحيحا لا يتيمم لصلاة الجنازة إلا إذا تعينت عليه الجنازة .

★★★



www.alkottob.com

# الغين

## غائط ← Gayiɗi :

Kar ka yi gayiɗi a kan hanya. لا تتبرز في الطريق .

Wanda ya yi gayiɗi alwallarsa ta warware. من تبرز انتقض وضوءه .

Ba mai yin gayiɗi a gaban matane sai mara kunya.

لا يتبرز أمام الناس إلا عديم الحياء .

## غَرَّاء ← Garra'u :

Garra'a ita ce mace ta mutu ta bar mijinta da 'uwarta da 'yan uwanta na wajen 'yaye biyu.

الغراء هي المرأة التي ماتت وتركت زوجها وأمها وأختها لأبوين أو لأب .

Ba yankawa 'yan'uwa mata wani abu in suna tare da kaka sai a masa'alar da ake kira garra'u kurum.

لا يُرْبِي للأخوات مع الجدّ إلا في مسألة ما يسمي الغَرّاء فقط .

## غرارة ← Algarara :

الجوال أو القماش المصنوع منه (الجوت)

Na zuba gorona a cikin algarara. وصعت ثمار الكولا الخاص بي في الغرارة .

Na lullube kula da algarara. لففت الزمزية بالجوت .

Ina son ka suwo mini algarara. أريد أن تشتري لي غرارة .

## غريب ← Garibi :

Ba wani garibin mutum a cikimmu. ليس فينا رجل غريب .



www.alkottob.com

A makarantam mu akwai littattafi garibai. في مدرستنا كتب غريبة .
Wannan kalmar gariba ce a wajena. هذه الكلمة غريبة عليَّ .

## : **Gartsa** ← غَرَسَ

### تأتي بمعنى عضَّ

Ta kama kunnensa ta gartsa haƙora. أمسكت أذنه وعضته .
Abokina ya gartsa mini cizo. صديقي عضني عضا شديدا .
Garin shan nono jinjiri ya gartsa uwarsa cizo.
من أجل رضاعة اللبن عض الطفل أمه .

## : **Garali** ← غرض

### تأتي بمعنى غرض أو أمر

Ya ɗauki mini kuɗina ya kashe garalin gabansa da su.
أخذ مالي ليقضي به غرضا أمامه .
Ni garalin gabana ya ishe ni. أنا لدي أمر يكفيني .
Ba wani garalin da zai sa ni in sha giya. . ليس أمامي أمر يجعلني أشرب الخمر

## : **Gargara** ← غرغرة

### تعني سكرة الموت

Da ya kai gargara , sai ya kira 'ya'yan nan ya yi musu wa'azi.
عندما بلغ غرغرة الموت دعي الأولاد ووعظهم .
Yana nan , can bayan kwana uku ya kai gargara.
وهو على هذا الحال ، بعد ثلاثة أيام وصل إلى غرغرة الموت .
Ciwo ya kai gargara. اشتد المرض .



www.alkottob.com

Yunwa ta kai gargara. بلغ الجوع مداة .

## : Gafara ← غَفَرَ

Da adadins ya cika , ya tafi wurin alƙali ya roƙe shi gafara.

بعد أن اكتمل عدده ، ذهب إلى القاضي وسألة المغفرة .

Na shiga na nemi gafara ga iyayena. دخلت وطلب المغفرة لدي والدّي .

Ka yi mini gafara bisa ga abin nan da zam faɗi. اغفرلي ما أقول .

Na gafarce ka duniya da lahira. غفرت لك في الدنيا والأخرة .

Shi ya tuba da yin ƙarya , yana roƙon sarki ya gafarta masa.

تاب من الكذب وسأل الأمير أن يغفر له .

Ina roƙon Allah ya gafarce mu bisa kan abin da muka aikata.

أسأل الله أن يغفر لنا ما فعلنا .

## : Gafala ← غفل

Yana gafala , me ya haɗa matarsa da matar yaronsa ?

إنه غافل ، ماذا جمع زوجته وزوجة خامة ؟ .

Ana gafala a duniyan nan. غافل في هذا الدنيا .

Kun san abin da ke tsakanimmu dai da malam gafalallen nan.

انتم تعرفون ما بيني وبين هذا العالم الغافل .

## : Gallaba ← غَلَّب

Rigimar yahudawa ta gallabi larabawa. مشكلة اليهود غلبت العرب .

Salahuddin ya yi gallaba a kan kiristoci. صلاح الدين تغلب على الصليبين .

Da haɗan kai mutane kaɗan suke gallabar masu yawa.

بالإتحاد قليل من الناس يغلبون الكثيرين .



www.alkottob.com

## غالبا ← Galibi :

Irin namun daji da tsuntsayen da ake samu a cikin hamada galibi masu cin nama ne.

نوع الحيوانات المفترسة والطيور التي توجد في الصحراء غالبا آكلة للحوم.

Aka sa wa yaron Musa , amma galibi suna kiransa kyauta.

سمي الولد باسم موسى ، ولكن غالبا ينادونه هدية .

Ka sani galiban ɓera a rami yake zama.

تعرف أن الفأر يكون غالبا في الجحر .

## غَلَّة ← Galla :

لا غلة لغاصب . Babu galla ga mai ƙwace.

سيرد ما أكل من غلة . Zai mayad da abin da ya ci na galla.

## غيلة ← Gila :

لا يُعْفي عن قتل الغيلة . Ba a yin rangwame a kan kisan gila.

Mutum ya samu ya yafe game da jininsa na kisan ganganci idan bai zamanto kisan gila ba ne. للرجل العفو عن دمة العمد إن لم يكن قتل غيلة .

## غلط ← Galaɗi أو Galatsi :

Kar ka zauna tsakanimmu ka ringayi mana galatsi.

لا تجلس بيننا وتكثر الغلط

Ai wannan abin da ka aikata galatsi ne a fili.

هذا الذي فعلته غلط صريح .

Ko mahaifinka ba zai jure wannan galatsin naka ba.

حتى والدك لا يصبر على غلطك ..



www.alkottob.com

## : Ganima ← غنيمة

Abin da ya bari kuma ya zama ganimar matar. ما ترك صار غنيمة للمرأة .
Aka raba ganima. وُزِّعت الغنيمة .
Ana raba ganimar da aka samu wajen yaƙin kashi biyar.
وزعت الغنيمة التي نالوها من الحرب خمسة أقسام .
Wanda ya yi sata daga baitulmali da kuma wajen ajiyar kayan ganima sai a yanke masa. من سرق من بيت المال أو حيث تحفظ الغنيمة تقطع يده .

## : Gainu ← غيب

Sanin gaibu sai Allah. لا يعلم الغيب إلا الله .
Ba zan sayi gaibi ba. لن اشتري شيئا لم أره .
Ka shiga da gaibi ? هل دخلت في الغيب ؟

## : Giba ← غيبة

Ya yi hanin aikata abin ƙi , da yin ƙarya da giba da annamimanci.
حرم عليه عمل المكروة والكذب والغيبة والنميمة .
Giba mummunar abu ce a musulunci الغيبة أمر سيء في الإسلام .
Giba tana cin lada kamar yadda wuta take cin auduga.
الغيبة تأكل الأجر كما تأكل النار القطن .
In tsoron Allah ya cika zuciyarka ba zaka ringa gibar mutanen ba.
إذا ملأت خشية الله قلبك لن تغتاب الناس .

## : Gaya ← غاية

Ya yi ƙoƙari gayar ƙoƙari. اجتهد غاية الاجتهاد .
Abin ya kai gaya. بلغ الأمر الغاية .
Ilmin malam ya kai gaya. علم الأستاذ بلغ الغاية .
Ba wanda ya san gayar ilmi sai Allah. لا أحد يعرف غاية العلم إلا الله .



www.alkottob.com

## Gaira ← غَيْرَ

تفيد الإستثناء أو النقص

Ɗaya ya yi gaira. — ناقص واحد ـــ أي إلا واحد .

Ya kawo kuɗi daidai ba gaira. — آحضر المال كاملا دون نقص .

Rashin gaskiya ya yi masa gaira. — الكذب عابة .

Kai ka ji sun mai da kai wawa babu gaira babu dalili.

جعلوك مجنونا دون عيب أو سبب .

Na ba shi kuɗinsa cikekku ba samu gaira a ciki.

أعطيته ماله كاملا لا نقص فيه .

## : Gyara ← غيَّر

تأتي بمعنى أصلح

Akawu ya girgiza kai ya gyara taguwa. — هزَّ الكاتب رأسه وأصلح ثوبة .

Maƙera kuwa suka shiga gyara makamai. — بدأ الحدادون يصلحون الأسلحة .

Kafin in sa a gyara su gwamma im ba ka wadansu kaya masu daraja.

قبل أن أمر باصلاحهم الأفضل أن أعطيك بعض المتاع الأحسن .

Bayan na zauna kuma na ɗan gyara gida ina so in aika iyalina su zo.

بعد أن أقيم وأصلح المنزل قليلا أريد أن أبعث لعائلتي لتأتي .



www.alkottob.com

# الفاء

## في الأزل ← Filazal :

Dan aljanna tun fil azal , Allah ya rubuta shi.

داخل الجنة كتب الله أسمه منذ الأزل ـ في الداخلين ـ

Abin da zai same ka tum fil azal Allah ya shirya shi.

ما سيصيبك أعده الله لك منذ الأزل .

Haka Allah ya halicce ni tum fil azal ba na san mata.

هكذا خلقني الله منذ الأزل لا أحب النساء .

## فائدة ← Fa'ida :

In an ruɓanya wannan kyautar za'a fi samun fa'ida.

إذا كررت هذه الهدية ستنال فائدة اكثر .

Na sami fa'ida.

نلت فائدة .

Ba na shiga abin da ba zan sami fa'ida a ciki ba.

لا أتدخل فيما لا أنال منه فائدة .

Zaman Makka na fa'idantu da shi.

استفدت من الإقامة في مكة .

## فأل ← Alfalu :

تعنى الفأل الحسن أو الفائدة

Yana son kyakkyawar alfalu.

يحب الفأل الحسن .



www.alkottob.com

Ni tun rayuwata ba na zaɓen lamari sai mai alfalu a gare ni.

أناطول حياتي لا أختار إلا الأمر الذي أجد فيه فائدة لي .

Kada ka shiga abin da ba zai yi maka alfalu ba.

لا تدخل فيما لا يعود لك بالفائدة .

## فاتحة ← Fatiha :

Daga sunnunin salla karatun sura bayan fatiha.

من سنن الصلاة قراءة سورة بعد الفاتحة .

Wanda ya maimaita karatun fatiha da rafkannuwa sai ya yi sujjada ba'adi.

من كرَّر قراءة الفاتحة سهوا سجد بعد السلام .

## فترة ← Fatara :

تعنى الغياب فترة طويلة أو الفقر

Mun yi fatara ganinka. مضت فترة لم نرك .

Ba na son in yi fatarar ko da darasi daya.

لا أحب أن اتغيب ولو درسا واحدا .

Na yi fatarar zuwa wajen malamina. غبت فترة طويلة عن أستاذي .

Fatara mai ta da tsohon bashi. الفقر مُحْي الدين القديم .

In fatara ta samu mutum mai arziki sai ka gan shi kamar mahaukaci.

إذا أصاب الفقر رجلا غنيا تراه كالمجنون .

## فتيلة ← Fitila :

تعنى المصباح

Ya hangi mutum da fitila. رأي من بعيد رجلا بمصباح .



www.alkottob.com

Na kashe fitilar.

أطفأت المبصاح .

Sun kunna fitila sana ƙirgar dukiya don gobe salla.

أشعلوا المصباح وجلسوا يَعُدون المال لأن غدا العيد .

Ya kunna fitilà ya kwanta ya bar ta tana ci.

أشعل المصباح ونام وتركة مشتعلاً .

Ga fitilu masu haske a kowace kusurwa.

ها المصابيح المضيئة في كل ركن .

## فتنة ← Fitina :

Yana son tafi wurin fitina.

يريد أن يذهب حيث الفتنة .

Fitina ta auku.

وقعت الفتنة .

Duk tsararrakinsa sun dame shi da fitina don sun ga ba shi da jaruntaka.

كل أقرانة صايقوة بالفتنة لأنهم رأوه ليس شجاعا .

Yanzu raina a kwance yake , tun da na rabu da fitinannen matan nan.

الآن هدأت نفسي ، منذ بعدت عن هذه المرأة الفاتنة .

Ina neman tsari da kai daga fitinar rayayyu da matattu.

أعوذ بك من فتنة المحيا والممات .

Kada ka fitinamu bayansa.

لا تفتنا بعده .

## فتوى ← Fatawa :

Ina da fatawa ya shugabammu.

عندي فتوى يا سيدنا .

Kada ka amsa fatawa im ba ka son hukuncinta ba.

لاترد على فتوى إن لم تعرف حكمها .

Na gabatad da fatawa zuwa ga babban malamin garimmu.

قدمت فتوى إلى كبير علماء مدينتنا .

In kana da kuɗi waɗansu malaman sai su sa maka fatawa kamar yadda kake so.

إذا كنت ذامال بعض العلماء يفتونك كما تريد .



www.alkottob.com

## : Faj'atan ← فجأة

Yau na haɗu da abokina faj'atan a kasuwa.

اليوم قابلت صديقي فجأة في السوق .

Jarrabawa ta zo mana faj'atan. الإختبار جاءنا فجأة .

Ni ba na son al'amari ya zo mini faj'atan.

لا أحب أن يأتيني الأمر فجأة .

## : Alfijiri ← فجر

Sai ka yi hanzari ka ga alfijiri ya keta.

يجب أن تسرع ، ترى أن الفجر قد انشق .

Ya duba gabansa sai ya ga haske kamar hudowar alfijiri.

نظر أمامة فرأي نورا كطلوع الفجر .

Gari ya soma wayewa alfijiri ya fasa. بدأت المدينة تظهر والفجر يطلع .

## : Fajiri ← فاجر

Kar ka zauna da fajiri sai in ya zama dole.

لا تجلس مع الفاجر إلا أذا صار الأمر ملحًا .

Fajirin mutum ba mai hana shi zina.

الإنسان الفاجر لا يمنعة شيء عن الزنا .

Fajirci mummunar sifa ce ga musulmi. الفجور صفة قبيحة للمسلم .

## : FIdil أو Fijil ← فجل

An fitad da zakka ga mai da aka fitar daga ƙwayar fidil.

تخرج الزكاة من الزيت المستخرج من حب الفجل .



www.alkottob.com

## فحشاء ← Alfahasha :

Salla tana kangiya daga barin alfahasha.

الصلاة تنهى عن الفحشاء والمنكر .

Kiyaye harshe daga yin ƙarya da alfahasha yana daga farillai.

حفظ اللسان من الكذب والفحشاء من الفرائض .

Allah ya tafiya muku da yin alfahasha. أذهب الله عنكم عمل الفحشاء .

Ya wajaba gare shi ya kiyaye harshensa daga alfahasha da munkari.

وجب عليه أن يحفظ لسانه من الفحشاء والمنكر .

## فَحْلٌ ← Fahali :

Matan da ta reni yaro 'ya'yan waccan matar da 'ya'yan fahalinta sun zama 'yan uwa. المرأة التي ترضع صبيا ، أولادها وأولاد فحلها صاروا أخوة .

## فخر ← Alfahari :

Allah ya tafiyar muku da yin alfaharin da iyaye.

أذهب الله عنكم التفاخر بالآباء .

Ya fara hura hanci yana alfahari. بدأ يشمخ بأنفة فخراً .

Ba abin da ya fid da ni gida sai in sami abin alfahari.

ما أخرجني من وطني إلا أن أبحث عما أفخر به .

## فداء ← Fida'u :

ما يقدم فداء للمتوفي

Na karanta wa mahaifina Ƙur'ani don ya zama fida'u a gare shi.

قرأت لوالدي القرآن ليكون فداءً له .



www.alkottob.com

Fida'u ga mahaifa alheri ne. الفداء للوالدين خير .

An gayyace mu karatun fida'u a gidan Musa.

دعينا لنقرأ ــ القرآن ــ فداء في بيت موسى .

## : Faraji ← فَرَجٌ

Allah ya yi mini faraji. اللهم افرج عنا .

Ba abin da zai hana ni shan wahala sai in na haɗu da wani faraji na Allah. لا شيء يخفف عني التعب إلا أن أنال الفرج من الله .

In ka yi haƙuri a kan wata masifa ta same ka , Allah zai yi maka faraji. إذا صبرت على المصيبة التي تصيبك سيأتيك الله بالفرج .

## : Farji ← فَرْجٌ

Janaba shi ne fakuwan hashafa a cikin farji.

الجنابة هي غياب الحشفة في الفرج .

Farjinta bai halatta ga mijinta ba sabo da haila.

فرجها لا يحل لزوجها بسبب الحيض .

Farjin mace yana halatta ne ga namiji in ya aureta.

فرج المرأة يحل للرجل إذا تزوجها .

## : Fara'a ← فَرِحَ

Ya tashi ya tarye su da fara'a. قام وقابلهم بفرح .

Ya lura kuma ya ga tsohuwar ba ta da fara'a kamar da.

نظر فرأي العجوز لا تفرح كما كانت من قبل .

Abu ɗaya ne kaɗai zai faranta mini zuciya. شيء واحد فقط سيفرح قلبي .

Tsalle-tsalle suka yi , sun 'yan kuka kamar suna fara'a da wata bushara. أخذوا يقفزون ويبكون كأنهم يفرحون ببشارة .



www.alkottob.com

## : **Farilla** ← فريضة

Yin salloli biyar farilla ne. الصوات الخمس فريضة .

Yin karatun fatiha a salla farilla ne. قرأءة الفاتحة في الصلاة فريضة .

Azumin watan Ramalan farilla ne. صوم شهر رمضان فريضة .

Ba a yin sallar farillai biyu da taimama ɗaya.

لا تصلى فريضتان بتيمم واحد .

Ya faralta wadansu ayyukan da zuciya zata ƙudurta su.

فرض بعض الأعمال التي يعتقدها القلب .

Ya wajaba a sanasshe su abubuwan da Allah ya faralta daga aiki ko ƙauli. وجب أن نعلمهم ما فرض الله من فعل أو قول .

## : **Furu'a** ← فروع

تأتي بمعنى علم الفقة

A cikin wannan littafi akwai jimila da asalin furu'a da dangoginta a bisa tafarkin Imamu Malik.

في هذا الكتاب يوجد جُمَلٌ من أصول الفقة على مذهب الإمام مالك .

Ilmin faru'a wajibi ne ga musulumi. علم الفقة ـ تعلمة ـ واجب على المسلم .

In ka san ilmin larabaci , ba ka san na furu'a ba ka yi kome ba.

إذا تعلمت العربية ، ولم تتعلم الفقة ما فعلت شيئا .

## : **Faraga** ← فراغ

تعنى سعة الوقت أو الرزق

Na dadi ban samu faragar ziyartar malamina ba.

مضي وقت ولم أجد الفراغ لزيارة أستاذي .

Idan ka sami faragar aikata wani lamari , to ka aikata shi tun ba ka rasa ta ba. إذا وجدت الفراغ لتفعل أمرا افعلة قبل أن تضيع الفرصة .



www.alkottob.com

In na sami faraga zan sayi mota. إذا وجدت سعة من المال سأشتري سيارة .

**فرق ← Farƙi :**

Farƙin musulumi da kafiri salla. فرق المسلم من الكافر الصلاة .

Ni ban ga wani farƙi ba tsakanin ra'ayina da naka.

لا أجد فرقا بين رأيي ورأيك .

Dukiya ba wuya ta farraƙa tsakanin 'yan 'uwa.

ليس من الصعب أن يفرق المال بين الأخوة .

**فروة ← Alfarwa :**

تعنى الخيمة

Duk wurin da zasu tafi sai su je da tanti watau alfarwa ta fatar dabbobi. حيثما يذهبون ـ يذهبون بخيمة من جلد الحيوانات .

Daga tsakiyar lambun kuma akwai wata alfarwa.

في وسط الحديقة أيضا توجد خيمة .

**فساد ← Fasadi :**

In fasadi ya yi yawa a ƙasa Allah yana ɗauki albarkat ta.

إذا اكثر الفساد في الأرض نزع الله بركتها .

Zama da masu fasadi yana lalata zuciya.

الجلوس مع الفاسدين يفسد القلب .

Hana aikata fasadi kyakkyawan abu ne. منع عمل الفساد أمر طيب .

**فسّر ← Fassara :**

تأتي بمعنى فسَّر أو ترجم

Ko da na gane haka , sai maganar fassarar mafarkin malaman nan ta faɗo mini. عندما رأيت ذلك ، تذكر تفسير هذا العالم للرؤيا .



www.alkottob.com

Na ce masa ya tuna da fassarar mafarkin da aka yi masa jiya.

قلت له أن يتذكر تفسير الرؤيا الذي فُسّر له أمس .

Ci gaba mu je yadda ya fassarata. استمر حتى نسمع كيف فسَّرها .

Ku lura da yadda zai fassara ma'anar wasiƙa.

انظروا كيف سيترجم معنى الرسالة .

Karantawa yake daga alfu laila yana fassara. يقرأ من ألف ليلة ويفسّر .

## : Fasiƙi ← فاسق

In ya zama fasiƙi ne , to a nan fa , wajibi ne ma a ƙaurace masa.

إذا صار فاسقا وجب في هذه الحالة هجرانه .

Bai halatta gare shi ba abutan fasiƙi ko zama da shi.

لا يحل مصاحبة الفاسق أو الجلوس معه .

Da ma kowa ya santa fasiƙa ce. لقد عرف الجميع أنها فاسقة .

## : Fasaha ← فصاحة

تأتي بمعنى الفصاحة أو الذكاء

Gobe ka ji fasaha wajen Haziƙi. غدا ترى الفصاحة من حاذق .

Ya yi suna a kan fasaha da wayo da ilmi. أشتهر بالفصاحة والثقافة والعلم .

Duk mutane suka yi ta mamakin fasahar Sufiyanu.

كل الناس تعجبوا من ذكاء سفيان .

Ya yi amfani da fasaharsa don ya san mu. استفاد من فصاحته ليعرفنا .

## : Fasali ← فَصْلٌ

تأتي بمعنى فصل من كتاب أو فصّل أو قسّم

Fasali ke nan a cikin sha'anin tsarki. فصل في أمور الطهارة .

Am fasalta riga. فُصّل له ثوب .



www.alkottob.com

Sarki ya ce a jina gida kafin safe , da irin fasalin da ya ce ana so duka.

قال الأمير أن يبني منزل قبل الصباح ، بالتفصيل الذي قال أنه يريده كله .

Ana raba aiki fasali - fasali. وزِّع العملَ قسماً قسماً .

An sa ni fasalin goro. طُلب مني تقسيم الكولا .

## : Falala ← فَضَّل

Yana shiryad da wanda ya so , ya yi masa gam da katar da falala tasa.

يهدي من يشاء فيوفقة بفضلة .

Don neman falalar da ke cikin sallar jama'a,

لينال الفضل الذي في صلاة الجماعة .

Ya gode falalarsa. شكر فضلة .

## Fiɗira ← فطرة

Abubuwa biyar suna cikin fiɗira... خمس أشياء من الفطرة ...

Dukan abin haihuwa ana haifarsa ne a kan fidirar musulunci.

كل مولود يولد على فطرة الإسلام .

Fiɗirar da Allah ya halicce mutum a kanta tana da wuyar canjawa a gare shi. الفطرة التي خلق الله الإنسان عليها يصعب تغييرها .

## : Fi'ili ← فعل

Ilmin nahawu yana koya ma yadda zaka gina fi'ili.

علم النحو يعلم كيف تكوّن الفعل .

Lokatan fi'ili a larabaci uku ne. أزمنة الفعل في العربية ثلاثة .

## : Faƙiri ← فقير

In mutum faƙiri ne , kaɗan ne daga cikin mutane suke girmama shi.

إذا كان الإنسان فقيرا ، قليل من الناس يحترمونه .



www.alkottob.com

In faƙiri ya kan̄a kansa ba mai wulkanta shi.

إذا عفَّ الفقير نفسه لا أحد يحتقرة .

Faƙiranci wani lokaci ya kan sa mutum ya zama kamar mahaukaci.

الفقر يجعل الإنسان أحيانا كالمجنون .

## : Fakat ← فقط

Sau biyu nake bukatar cin abinci a rana fakat.

احتاج للطعام مرتين في اليوم فقط .

Idan na karanta darasi sau ɗaya fakat ya ishe ni.

إذا قرأت الدرس مرة واحدة فقط يكفيني .

## : Fiƙihu ← فقة

Ya kan ganar da abubuwa da yawa na tushen fiƙihu da rassansa.

يفهم كثيراً من أصول الفقة وفروعة .

Neman sanin ilmin fiƙihu wajibi ne a kan musulumi.

طلب معرفة علم الفقة واجب على المسلم .

Malam Nasiru babban malamin fiƙihi ne. الأستاذ ناصر عالم كبير في الفقة .

Akan sami bambanci tsakanin malamin fiƙihu.

يوجد خلاف بين علماء الفقة .

## : Fallasa ← فلس

### تأتي بمعنى فضح أو صرف

Cikin kwana bakwai yana iya fallasad da su duke.

في سبعة أيام يستطيع صرفها جميعا .

Suka shiga fallasad da rabonsa. بدأوا يصرفون نصيبة .

Makau ne yake fallasar ka a cikin talakawa. ماكو يفضحك في الشعب .

Yi gama da bakinka , kada ka fallasa ni. أمسك فمك ، لاتفضحني .



www.alkottob.com

## : Fanni ← فن

Wane fanni ka ɗauka na ilmi ? أي فن أخذت من العلم ؟

A wannan lokacin wasan ya ci na ɗaya ne a fannin wasannin kwaikwayo. في هذا الوقت نالت المسرحية المركز الأول في فن التمثيل .

Ni ban koya ɗaya daga cikin waɗannan fannoni ba.

لم أتعلم فنا واحدا من هذه الفنون .

A wane fanni ka ɗauke shi. من أي نوع من الأشخاص اعتبرته .

A fannin mutumin kirki muka ɗauke shi. اعتبرناه من الناس الطيبين .

## : Finjali ← فنجال

Ciko mini finjalin nan da shayi. املأي هذا الفنجال بالشاي .

Haramun ne shan ruwa da finjali zinari.

حرام شرب الماء في فنجال من الذهب .

Finjalin tangaran ba shi da wuyar fashewa.

الفنجال الزجاج ليس صعبا كسره .

## : Fahrasa أو Fihirisa ← فهرس

Wannan littafi faharasa dinsa yana da wuya. هذا الكتاب فهرسته صعبة .

Idan zaka sayi littafi fara duban faharasa ɗinsa.

إذا اشتريت كتابا انظر أولا إلى فهرسته .

## : Fahimta ← فهم

Ni duk ban fahimta da abin da aka ce ba. أنا لم أفهم ما قيل .

Mai hankali duk ai ya kamata ya fahimta da haka ba sai am faɗi ba.

العاقل يجب أن يفهم ذلك لا ينتظر أن يقال له .

Ya fahimtad da abin da ya faru. فهم ما حدث .



www.alkottob.com

## : **Fawwala** ← فَوَّض

Na fawwala masa shi. فوضة فيه .

Na fawwala lamarina ga Allah. فوضت أمري لله .

Kar ka fawwala lamarinka ga Allah ba bare da bin ka'idodin da shari'a ta shirya maka.

لا تفوض أمرك لله دون اتباع القواعد التي وضعتها الشريعة لك .

Na daina neman wani magani a bisa wannan cutar , na fawwal al'amurrata ga Allah. تركت طلب الدواء لهذا المرض ، وفوضعت أموري لله .

***



www.alkottob.com

# القاف

## : **Ka'imi** ← قائم

تأتي بمعنى رب البيت أو ولي الأمر

Mace im ba ta da wani Ƙa'imi a kanta sai ta wulkanta.

المرأة إن لم يكن لها ولي تحتقر .

Ina da Ƙa'imin da zai taimake ni in yi aure.

لدي ولي الأمر الذي سيساعدني لأتزوج .

Yanzu ba ni da wani Ƙa'imin da zai taimake ni tun da mahaifina ya mutu.

الآن ليس لدي ولي الأمر الذي سيساعدني بعد وفاة والدي .

## : **Kubba** ← قُبَّة

Ƙubbar masallacin annabi koreya ce. قبة الحرم النبوي خضراء .

Masallacin garimmu yana da Ƙubba. مصلى مدينتنا له قبة .

Na gina masallaci mai Ƙobbobi hudu. بنيت مصلى لها أربع قبب .

An Ƙi yin surori a jikin gidaje da kuma Ƙubbobi.

يكره الصور في الأسرة والقباب .

## : **Kabari** أو **Kabari** ← قبر

Hakika muminai za'a jarraba su cikin Ƙabarinsu.

إن المؤمنين سيسألون في قبرهم .

An Ƙi a yi gini kan Ƙabari ko shafe shi da suminti.

يكره البناء على القبور أو تجصيصها .



www.alkottob.com

In bature ya shiga ƙasar mu ya zo kabarin sa ke na.

إذا دخل الأوربي بلدنا فقد جاء إلى قبره .

Ya tafi hurumi ; ya duba wani sabon kabari , ya tona , ya dauko gawar , ya kawo gida.

ذهب إلى المدفن ، بحث عن قبر جديد ، حفرة ، وأخذا الجثة ، وحملها إلى المنزل .

Ya sa akwatinsa cikin wani kabari daga kaburburan da ke kusa da shi.

وضع صندوقة في قبر من القبور القريبة منه .

## : Kabli ← قَبْل

Wanda ya yi riga , ya yi ƙari , ya yi sujjada ƙabli.

من نَقَص أو زَاد سجد قبل السلام .

Ba a yin sujjada ƙabli sai in an bar ṣunna biyu.

لا يسجد قبل السلام إلا إذا تُركت سنتان .

## : Alƙibla ← قبلة

In ya ba alƙibla baya sai ya yanke sallarsa.

إذا أعطى القبلة ظهرة يجب أن يقطع صلاته .

Zai fuskanci alƙibla.

سيواجة القبلة .

Wanda ya kauce wa alƙibla sai ya mai da salla cikin lokaci.

من انحراف عن القبلة أعاد الصلاة في الوقت .

Fuskantar alƙibla farilla ce.

مواجهة القبلة فريضة .

## : Kabila ← قبيلة

Ni ina daga cikin kabilar Gwari.

أنا من قبيلة جواري .

Kowace kabila tana kishin mutanenta.

كل قبيلة تغار على رجالها .

Hausawa kabilu ne iri-iri.

الهوساويون قبائل مختلفة .



www.alkottob.com

Mun ji labarin wad̃ansu kabilu na Nigeria ta arewa.

سمعنا أخبار بعض قبائل نيجيريا الشمالية .

Mutanen hamadan nan kabilu iri iri ne. سكان هذه الصحراء قبائل مختلفة .

## قبلية ← Kabliyya :

Ya san kabliyya da ba'adiyya. يعرف كل شيء في العالم ـ أي قبلة وبعده .

Na kawo mata kabliyya da ba'asiyya ta Ƙi. أحضرت لها كل شيء فرفضت .

## قتال ← Kitala :

Sai an sha Ƙitala da shi tukuna ya biya. لا يدفع إلا إذا قاتلناه .

## قدّر ← Kaddara :

Hakika Allah ne ya Ƙaddara shi. إن الله قدرة .

Shi ne mai Ƙaddara al'amurra da zatinsa. هو مقدر الأمور بذاته .

Allah shi ne mai Ƙaddara harkokinsu da ajalinsu.

الله هو المقدر لحركاتهم وأجلهم .

Ƙaddara ta rabo ni da mutanen har na fad̃o nan.

القدر فصلني عن الناس حتى دخلتُ هنا .

Ƙaddara ta kawo mu nan cikin mutane. القدر جاء بنا هنا في الناس .

Tsaya ku ji abin Ƙaddara. انتظروا لتسمعوا المقدَّر .

Allah ya Ƙaddara haihuwar wannan yaro. الله قدّر ولادة هذا الولد .

In Allah ya Ƙaddara zai karye sai ya karye. إن قدر الله أن ينكسر سينكسر .

Abin da ya Ƙaddara yana da makawa ne ? هل ما قدر ـ الله ـ يتأخر ؟

Ka ba da gaskiya da Ƙaddara alherinsa da sharrinsa.

تؤمن بالقدر خيره وشره .



www.alkottob.com

## قذف ← Ƙazafi :

An yi saɓani a kan zargin Ƙazafi. أُخْتُلِفَ في لعان القذف .
Ya yi musu bulala tamanin don Ƙazafi. جلد ثمانين جلدة للقذف .
Ba a yin haddi ga mai yi wa yaro Ƙazafi. لايقام الحد على قاذف الصبي .
Babu haddi a kan wanda bai balaga ba wajen yin Ƙazafi.
لا حد على من لم يَبْلُغْ في قذف .

## قراءة ← Karatu :

تأتي بمعنى القراءة أو الدرس

Dan kirki daga karatu sai aiki ko koyon sana'a.
الولد الطيب من الدرس إلى العمل أو الصناعة .
Ya fara koya mini karatu. بدأ يعلمني القراءة .
Zai koya musu karatu a masallaci. سيعلمهم القراءة في المسجد .
Yana ba da karatu. يلقي درساً .
Shaihu yana ba da karatu. الشيخ يلقي درساً .
Bayan na gama ba da karatu sai suka tashi kowa ya yi alwalla.
بعد أن انتهيت من إلقاء الدرس ، قاموا وكل توضأ .

## قروء ← Kuru'i :

Abin da ake nufi da Ƙuru'i shi ne tsarki da ke tsakanin jini biyu.
ما يقصد بالقروء هو الطهر الذي بين الدمّين .

Wadda take akwai sauran bauta , a jikinta Ƙuru'i biyu ne.
من يوجد فيها بقية رق ، لها قراءان .
Iddar mace wadda take 'ya ce, Ƙuru'i uku ne. عدة المرأة الحرة ، ثلاث قروء .



www.alkottob.com

Al'aƙara'i shi ne wankan haila , shi ne tsarki.

الإقراء هو غسل الحيض ، هو الطهر .

## : Karau ← قارورة

تعني زجاجة صغيرة

Wannan al'amari na game da ƙarau ba mu muka ƙaga shi ba.

هذا الأمر الخاص بالقارورة لم نخترعة نحن .

Na samu wata ƙatuwar ƙarura. وجدت قارورة كبيرة .

Na shanye wata ƙatuwar ƙarura a kan hanya.

شربت قارورة كبيرة في الطريق .

An ba ni ƙarura guda ta turare. أعطيت قارورة واحدة من العطر .

## : Alƙur'ani ← قرآن

Alƙur'ani zancen Allah ne. القرآن كلام الله .

Ban san kome ba cikin alƙura'ni sai wata aya,

لم أعرف شيئا من القرآن إلا آية واحدة .

Na sauke alkur'ani ranar laraba sha tara ga watan Muharram.

حفظت القرآن يوم الأربعاء التاسع عشر من شهر محرم .

## : Karni ← قَرْن

A cikin ko wane karni ana samun mujaddadi. في كل قرن يأتي مجدد .

Shekara dari ita ce ƙarni guda. المائة سنة قرن واحد .

Ba'a samun mutumin da ya rayu ƙarni biyu a yanzu.

لا يوجد الإنسان الذي يعيش قرنين الآن .



www.alkottob.com

## : Kirani ← قِران

Siffar Ƙirani ita ce ya yi haramar yin hajji da umura gaba daya.

صفة القران هي أن يُحرم بحج وعمرة معاً .

Wanda ya yi tamattu'i ko Ƙirani ba daga jama'ar Makka ba , to hadaya ta wajaba gare shi.

من تمتَّع أو قَرن من غير أهل مكة، وجب الهدى عليه .

Kadaitawa ga hajji shi ya fi ga malikiyya daga yinta tare da tamattu'i ko kuma Ƙirani.

الإفراد بالحج أفضل عند المالكية من التمتع والقران .

## Karuna ← قارون

Ran nan sai na ce musu su raka ni su a wani tabki wai shi Tabkin Karuna.

ذات يوم قلت لهم أن يصطحبوني للصيد في بحيرة تسمي بحيرة قارون .

Farken ya yi ya yi , suka Ƙi , suka ce ai ko ya fi Dan Ƙaruna kudi , ba su wa 'yan nan salla.

حاول التاجر كثيرا ، فرفضوا ، وقالوا لو فاق ابن قارون مالاً ، لن يصلوا على هذه الفتاة .

## : Kirali ← قراض

Kirali ya halatta da dinari da dirhami.

القراض جائز بالدينار والدرهم .

## : Ƙuri'a ← قرعة

Ƙuri'a ta fado kan zomo.

وقعت القرعة على الأرنب .

Kad dai in ce ba zaka jefa mini Ƙuria.

لا أقول أنك لن تقترع لي .

Ba ka san masu jefa Ƙuri'a sun fi ka lalata ba.

ألا تعلم أن الناخبين اكثر منك فساداً .

Wannan shi ne jazaman Ƙuri'ata ta masu gaskiya ne,

اقتراعي هذا بالتأكيد اقتراع الصادقين .



www.alkottob.com

## : Kissa ← قصة

Kada ka amasa jawabi sai ka san Ƙissa tata.

لا ترد على كلامي حتى تسمع قصتي .

Na karanta wata Ƙissa mai daɗi. قرأت قصة جميلة .

Yana da kyau mutum ya dinga karanta kisoshi don ya Ƙara sani.

هو رجل جيد دائما يقرأ القصص ليزداد معرفة .

Akwai wani littafin Ƙisoshe ta annabi Sulaimana.

يوجد كتاب قصص النبي سليمان (عليه صلاة والسلام) .

## : Kasida ← قصيدة

Na rubuta Ƙasida mai baiti goma. كتب قصيدة من عشرة أبيات

In kana da murya mai daɗi , in ka rera Ƙasida kowa sai ya kalle ka.

إذا كان لك صوت جميل وقرأت قصيدة الجميع ينظر إليك .

Akwai wani littafin da ya tattara Ƙasidu iri - iri.

يوجد كتاب يجمع قصائد مختلفة .

## : Kasaru ← قصْر

Matafiya ba yi wa sallar magariba kasaru المسافر لا يصلي المغرب قصراً .

Ba zai fara Ƙasaru ba har sai ya wuce gidajen gari kuma ya bar su a bayansa. ولا يقصر حتى يتجاوز منازل المدينة وتصير خلفة .

Wanda ya tafiya mil arba'in da takwas lalle ne ya yi sallar Ƙasaru.

من سافر ثمانية وأربعين ميلا عليه أن يصلي قصرا .

## : Kisasi ← قصاص

A kan yi Ƙisasi ga rauni na ganganci. يتم القصاص في الجراح العمد

Babu Ƙisasi tsakanin da da bawa a rauni. لا قصاص بين الحر والعبد في الجرح.



www.alkottob.com

## : Alƙali ← قاضي

Ta fito zata koma gidan alƙali ta shaida masa ba ta sami kome ba.

خرجت لتعود إلى بيت القاضي لتقول له أنها لم تجد شيئا .

Da adadinsa ya cika , ya tafi wurin alƙali ya roƙe shi gafara.

عندما اكتمل العدد ، ذهب إلى منزل القاضي ليسأله المغفرة .

Aka kai wani ƙara wurin alƙali. رفُعت شكوى إلى القاضي.

Sarkin fawa ya sa su gaba har majalisar alƙali.

رئيس القصابين دفعهم أمامة إلى مجلس القاضي .

Alƙali ya tambayi mai kudin nan. سأل القاضي صاحب هذا المال.

## : Keta ← قطع

تعني قطع أو هتك

Nan da nan maridi ya kekketa tsoho. في الحال قطّع المارد الرجل العجوز.

An keta irlinsa. هُتِك عرضة .

Kar ka keta irlin wani don kada a keta naka.

لا تهتك عرض أحد كي لا يُهْتك عرضُك .

## : Ka'ida ← قاعدة

قاعدة أو قانون

An yanke ƙa'ida wata biyu a gama haraji

وضع قانون لجمع الخراج في شهرين .

Yana aika ba ƙa'ida. يعمل بلا قاعدة .

Ya wuce ka'ida da aka yi masa. تجاوز القاعدة التي وُضعت له.



www.alkottob.com

## قفيز ← Kafizi :

Kwando biyar daidai yake da kafizi shida da rubu'in kafizi.

الخمسة أوسق تساوي ستة أقفزة وربع قفيز .

## قال ← Ƙala :

تأتي بمعنى شيء في عبارة «لم يقل شيئا»

Iliya dai bai ce Ƙala ba , don ya sani ba Ƙarfinsu ko dabararsu ta ba su wannan nasara ba.

لم يقل إيليا شيئا ، لأنه عرف أنه ليست قوتهم ولا حيلتهم التي وهبتهم هذا النصر .

Sun zo , sun sauka , ba mu ce musu Ƙala ba.

جاءوا ونزلو ، ولم نقل لهم شيئا .

## قيل وقال ← Ƙila wa Ƙala :

Suna cikin ƘilawaƘala. في قيل وقال .

## قليلا ← Kalilan :

Tun da yake akwai sauran wadansu abokai, Ƙalilan da 'yan 'uwa masu zuwa wurinka.

طالما أنه يوجد بقية من الأصدقاء ، قليل من الأخوة القادمون إليك .

## قَلَمٌ ← AlƘalami :

Ya daki alƘalami ya sami takarda ya rubuta. أخذ القلم وأحضر ورقة وكتب .

Ya ce a kawo masa alƘalami da tawwada da takarda.

طلب أن يُحضر له القلم والمحبرة والورقة .



www.alkottob.com

Alƙalami ya bushe. جف القلم أي انتهي الأمر .

Ba su san bakin alƙalami ya rigaya ya bushe ba,

لم يعرفوا أن سِنَّ القلم سبق أن جفَّ أي انتهي الأمر من قبل .

## قامة ← Kama :

Lokacin sallar la'asar yana farawa daga ƙarshen ƙaman nan har zuwa fatsi - fatsin rana. وقت صلاة العصر يبدأ من نهاية القامة حتى اصفرار الشمس .

## قمح ← Alkama :

An haɗa alkama da sha'ir wajen yin zakka.

جُمع القمح والشعير عند أداء الزكاة .

Kuma lalle ya yi shuke shuke iri - iri kamar su albasa da alkama.

لا بد أن تُزرع أنواع كثيرة مثل البصل والقمح .

Hatsinsu shi ne alkama da sha'ir. حبوبهم القمح والشعير .

## قنوت ← Kunuti :

Zaka karanta ƙunuti bayan ka yi ruku'i. ستقرأ القنوت بعد الركوع .

Kana iya yin ƙunuti gabannin ruku'i. تستطيع أن تعمل القنوت قبل الركوع .

Kunuti a sallar asuba abu ne mai kyau. القنوت في صلاة الصبح شيء حسن.

## قنديل ← Kyandir :

Ka taimake da kyandir da tawada da alƙalami. ساعد بمصباح ومحبرة وقلم .

Na kunna kyandir a cikin ɗakina.

اشعلت المصباح في حجرتي .

In ka je kasuwa ka sayo mini kyandir.

إذا ذهبت إلى السوق اشتري لي قنديلا .

Barawa ya sace mini kyandir ɗina. اللص سرق مني مصباحي .



www.alkottob.com

## قول ← Ƙauli أو Alkawari :

الكلمة الأُولى تأتي بمعنى القول والثانية بمعنى الوعد أو العهد

Ya wajaba a sanasshe su abubuwan da Allah ya faralta daga aiki da Ƙauli.
وجب أن نعرفهم ما فرض الله من عمل أو قول .

Ya iya Ƙaulin magana.
يحسن قول الكلام .

Mun ɗauki alkawari , kullum mun riƘa aiko maka da ɗaya daga cikimmu.
اتخذنا عهدا ، أن نبعث لك كل يوم بواحد منّا .

Ya dauki alkawari zai yaƘi.
اتخذ عهدا بأن يحارب .

Ina alkawarin da ka ɗauka ?
أين العهد الذي اتخذته ؟

Ina so ka yi mini alkawari cewa in mun tafi zamu dawo tare.
أريد أن تعدني بأن نعود معاً إذا ذهبنا .

Ya ce zamu tafi tare, bisa ga alkawarin da ya yi mini.
قال سنذهب معاً ، بناء على الوعد الذي قطعة لي .

Ya aiko a gaya masa , yau fa alkawari ya ciko.
بعث من يقول له ، اليوم انتهي الوعد .

Ya kai masa don ya cika alkawari ya kuma nemi albarka.
وصل إليه ليفى بالوعد وينال البركة .

## قَيد ← Kaidi :

Al'amarin nan sake ne ba Ƙaidi.
هذا الأمر طليق بلا قيد .

## قَيَّدَ ← Kayyade :

تأتي بمعنى حَدَّد

An Ƙayyade kwana uku zai biyu.
حدد ثلاثة أيام ويدفع .

An Ƙayyada aiki.
حُدِّدَ العملُ .



www.alkottob.com

Na ji har Ƙayyade masa lokacin da zai komo daga aiki.

سمعت أنه حدد له الوقت الذي سيعود فيه من العمل .

A nan arewa inda aka Ƙayyade don ɗaukar fasinja su ne Kano da Kaduna.

هنا في الشمال حيث حدد ، نقل المسافرين إلى كنو وكدونا .

## : Kima ← قيمة

Za'a yi Ƙima ga wanda ya kashe ta. ستقدر قيمة ما قتله .

Ya ba da Ƙimarsa. أعطى قيمته .

Idan ta Ɓace to ba da Ƙimarta ta kama shi. إن فسرت فعلية قيمتها .

Wanda ya halakad da wani kaya , to biyan Ƙimarsa ta kama shi.

من أهلك متاعا فعلية قيمته .

Al'amarin nan namu game da talakawa na gaya wuce kima.

أمرنا هذا مع الشعب تجاوز الحد .

Ruɗewan nan tawa ta wuce kima. حيرتنا هذه تجاوزت الحد.

Ga zafin rana fiya da kima. ها حرارة الشمس زادت عن الحد .

Tana sona gaba da kima. تحبني زيادة عن الحد .

## : Kiyama ← قيامة

Sai ka zauna nan har ranar tashin Ƙiyama.

يجب أن تعيش حتى يوم قيام القيامة .

Nan zaki yi ta zama har ranar tashin Ƙiyama.

هنا ستقيمين حتى يوم قيام القيامة .

Allah ya haɗu mu da alheri a ranar Ƙiyama.

الله يجمعنا على الخير في يوم القيامة .

## : Kiyamul laili ← قيام الليل

Sarki ya cire zobensa na zinnariya don zai yi taimama a yi Ƙiyamul laili.

خلع الأمير خاتمة الذهبي ليتيمم ويقوم الليل .



www.alkottob.com

Na yi alwalla na fito masallacin Ƙofar gida in yi Ƙiyamul laili.

توضأت وخرجت إلى المصلى على باب المنزل لأقوم الليل .

## قيلولة ← Kailula :

Na haye bisa gada don in taɓa dan Ƙailula.

صعدت فوق السرير لأستريح من القيلولة .

Bayan na farka daga dan Ƙailula , na baro ta can a kwance a kan gado.

بعد أن استيقظت من قيلولة قصيرة ، تركتها هناك راقدة على السرير .

***



www.alkottob.com

# الـكاف

## : Ka'in ← كائن

Aka samo kan  itace ashirin aka haɗa wuta ka'in da na'in.

أُحضر من فروع الشجر عشرون واشعلت نار كبيرة .

Kogi ya cika ka'in da na'in. امتلأ النهر تماما .

Wasa ya cika ka'in da na'in. امتلأ الملعب تماما .

Abu ya yi ka'in da na'in. أصبح الأمر خطيرا .

Hadari ya ɗauro ka'in da na'in. العاصفة حجبت السماء تماما .

## : Kabbara ← كَبَّرَ

Daga farillan salla niyyar salla mu'ayyana da kabbarar harama.

من فرائض الصلاة نية الصلاة المعينة وتكبيرة الإحرام .

Idan karatun sura ya ƙare sai ka yi kabbara.

إذا انتهت قراءة السورة يجب أن تكبِّر .

Sau ka daga kanka tare da kabbara. يجب أن ترفع رأسك مع التكبيرة .

Na fito fage na ti kabbara. دخلت الميدان مُكَبِّراً .

An fada masa da kabbara. هجمت عليه مُكبِّرا .

## : Kaba'ir ← كبائر

تعني المفرد أي الكبيرة

Shaidar wanda mai bayyana kaba'ira ba ta halatta.

شهادة مُظْهِر الكبيرةْ لا تجوز .

Mutumin kirki ba ya aikata kaba'ira. الرجل الطيب لايعمل الكبيرة .



www.alkottob.com

Aikata kaba'ira yana cikin sababin fari. عمل الكبيرة من أسباب القحط .

Shan giya yana daga cikin manyan kaba'irai. شرب الخمر من الكبائر العظيمة.

## : Littafi ← كتاب

Shi ne littafin na farko wanda ya koya wa mutane batun addini.

هو الكتاب الأول الذي علم الناس أمر الدين .

Ba shakka idan mai karatu ya karanta littafin nan zai fada cikin kogin tunanin. لا شك إذا القاريء قرأ هذا الكتاب سيغرق في بحر من التفكير .

Alƙur'ani shi ne littafin Allah. القرآن هو كتاب الله .

Mai gidana ya kawo wadansu littafan ilmi ya ba ni.

أحضر سيدي بعض كتب العلم وأعطاني إياها .

## : Kitabiyya ← كتابية

Allah ya halatta tarawa da kitabiyya. أحل الله نكاح الكتابية .

Za'a tilasta bakitabiyya bisa ga yin idda. تُجبر الكتابية على العدة .

Musulunci bai yarda bakitabe ya auri musulima ba.

الإسلام لا يوافق أن يتزوج الكتابي مسلمة .

## : Kafadar ← كتف

Mun ga wani saurayi a kan wani ingarma , takobi rataye a kafadarsa.

رأينا شابا على حصان ، والسيف معلق بكتفه .

Wani lokaci ta kan sauka a kafadar mutum. أحيانا تنزل على كتف الإنسان.

Ya bangaji kafadata don neman rigima. وخزني في كتفي جرًّا للمشاكل .

## : Kaza ← كذا

Na ce musu a ina kuka gan shi ? suka ce gari kaza.

قلت لهم أين رأيتموه ؟ قالوا مدينة كذا .



www.alkottob.com

Ya ce wa mutane a yi kaza , a bar kaza.

قال للناس يُفْعل كذا ، ويُتْرك كذا .

buta kuma, da ya zo a debi kuɗi kaza daga baitulmali.

لأكتب ، عندما يأتي يُعْطى مالٌ كذا من بيت المال .

Su dawo su ce «kogi kaza ya tashi cinsu suka kuɓuta da kyar kayan nan».

عادوا وقالوا «نهر كذا فاض وأغرقهم ونجوا بصعوبة بهذا المتاع».

### : Kurasi ← كُرَّات

Bai kamata ga wanda ya ci kurasi ko albasa ya shiga masallaci ba.

لا ينبغي لمن أكل الكرات أو البصل أن يدخل المصلى .

### : Karimci ← كرم

Ban taɓa ganin mutum mai karimci irin Musa ba.

لم أر أبدا رجلا كريما مثل موسى .

Sarkin Zazzau ya yi masa karimci mai yawa. أمير زاريا أكرمة كثيراً .

Ya saukad da mu , ya yi man karimci mai yawa. أنزلنا وأكرمنا كثيراً .

In kana so a dauke ka a mutum karimi, to, duk faɗa sai ka mayar da shi wasa da dariya. إن‌كنت تريد أن تُعْتبر كريماً ، كلما يقال أجعله مزاحا وضحكا .

### : Karama ← كرامة

Dan Hudiyo ya nuna masa karama. ابن فوديو أظهر له كرامة .

Sai sarki kadai suka sani wannan karamata. لايعرفون‌هذه‌الكرامة إلا للأمير فقط.

Mutumin mai karama. رجل ذو كرامة أو كريم .

Nuna karama gare shi. مُظْهِر للكرامة .

Karama bayan zilla. كرم بعد ذلة .

### : Karahanta ← كراهة

An karahanta waiwaye a cikin salla. كُرِهَ الإلتفات في الصلاة .



www.alkottob.com

Ya karahanta shi bai kuma halatta shi ba. كَرِهَة ولم يُجزة .

Yawan aikata karahiya zai tura mutum zuwa ga aikata haramun.

كثرة عمل المكروه يجر الإنسان لعمل الحرام .

Aikata karahanci ba ya sa a rubuta maka zunub.

بعمل المُكْرِه عليه لا يكتب لك ذنب .

## : Kasabi ← كسب

Zama ba tare da wani kasabi ba, ba zai amfani mutum ba.

بقاء الشخص بلا كسب ، لا يفيدة .

Mutumin da ya ce ya rasa abin da zai yi a cikin kasabaci - kasabacin duniyan nan karya yake.

الإنسان الذي يدعى أنه عجز عن أن يجد ما يكسبة في هذه الدنيا كذاب .

Duk kasabin da mutum zai yi mutuƙar ba haramun ba ne, ba laifi.

كل ما يكسبة الإنسان طالما أنه ليس حرام ، لابأس به .

## : Kasada ← كسد

تأتي بمعنى الخسارة أو والتشجع

Har yanzu al'adarsu ke nan  al'ada ta kasada.

حتى الآن عادتهم عادة خسارة .

Tafiyar zata zama kasada ne wajen shi. السفر سيصير خسارة لهم .

Bin tsuntsuwan nan kasada ne. اتباع هذا الطائر خسارة .

Suka kasada suka tasam masa, da suka ƙara matsawa sai suka ga ashe mutum ne.

تشجعوا وهجموا عليه ، ولما أقتربوا منه كثيرا أدركوا أنه إنسان .

Duk abin nan Bawa na nan ƙulle - ƙullen ko ya kasada ne ya fito, ko ya rufe wa kansa asiri ya gudu.

كل هذا وباو يفكر هل يتشجع ويدخل ، أم يخفي سرة ويهرب .



www.alkottob.com

## : Kassara ← كسَّر

Ba zaka kassara masa dan abin nan da yake taƙama da shi ba.

ألا تكسر له هذا الشيء الصغير الذي يتباهي به .

## : Keso ← كيس

Ya kawo keso kuɗi ya ba ta. أحضر كيس المال وأعطاها .

Wanda ya mallaki keso guda a zamanin da mai kuɗi gaske ne.

من كان يملك كيسا واحدا من المال قديما غنيي حقا .

Ya ba ta keso daya. أعطاها كيسا واحداً .

A zimanin yanzu ba'a amfani da kalmar keso a bangaran kuɗi.

في الوقت الحالي لا تستعمل كلمة كيس في الناحية المالية .

Ba kowa ne yake mallakar keso gudu ba a da.

ليس كل واحد كان يملك كيسا واحاد من المال في الزمن الماضي .

## : Kusufi ← كسوف

In rana ta yi kusufi musulumi su kan yi sallar kusufi.

إذا إصاب الشمس الكسوف يصلي المسلمون عادة صلاة الكسوف .

Mutane suna tsorata da aukuwar kusufi. الناس يخافون من حدوث الكسوف .

Ran jummu'a rana ta yi kusufi. كُسِفت الشمس يوم الجمعة .

## : Kasala ← كسل

Allah ya yi mutumin nan ba mai kasala ba ne. لم يجعل الله هذا الرجل كسولا .

Nan da nan ya ji duk kasala ta rufe shi.

في الحال شعر أن كل الكسل يغطية .

Zasu ji jikinsu ya yi nauyi suna jin kasala.

سيشعرون أن جسمهم ثقل ، ويشعرون بالكسل .

Muzaru ya ji kasala ta kama shi. القط شعر بالكسل يستولي عليه .



www.alkottob.com

## : Kuskus ← كُسْكُسْ

Matata ta dafa mini kuskus. زوجتي طبخت لي كسكس .
Kuskus abinci na mai sauƙin dafawa. الكسكس طعام سهل الطهي .
Ka sayo mini kuskus na fam daya. اشتر لي كسكسا بجنية واحد .

## : Ku'i ← كوع

Daga sunnonin alwalla su ne wanka hannuwa biyu ziwa ku'i.
من سنن الوضوء غسل اليدين إلى الكوع .
Wanke hannuwa zuwa ku'inka biyu. أغسل يديك إلى الكوعين .

## : Ka'aba ← كعبة

Dawafi shi ne kewayon dakin Allah watau Ka'aba.
الطواف هو الدوران حول بيت الله أي الكعبة .
Ka'aba ita ce a alƙiblar musulumai daga ko ina.
الكعبة هي قبلة المسلمين من كل مكان .
Rigar Ka'aba baƙa ce. كسوة الكعبة سوداء.
Ka'aba tana da daraja a wajen musulumai. للكعبة منزلة لدي المسلمين .

## : Kafe أو Kife ← كَفَى

### تأتي بمعنى قلب

Zunubin mutanen garin nan ya isa a kife.
ذنب أهل هذه المدينة يكفى أن يكبهم على وجوههم .
Ya sami albasa mai yaji, ya kifa turmi ya hau ya zauna sa'an nan ya yi ta ci. أخذ بصلا حارا ، وقلب الهاون وصعد وجلس ، وأخذ يأكل .



www.alkottob.com

Daga jikina ya kafe na ce su taimake ni in cire shi daga taɓo.

عندما انكفأ حماري طلبت أن يساعدوني لأخرجه من الطين .

Ya kafe shi da mari.

لطمة على خدة .

## : Kafatan ← كافةً

Kafatan garin nan.

في كل هذه المدينة .

Duk kafatanin larabawa ba wandan bai san sharrin Isra'ila.

العرب كافة لا يوجد بينهم من لا يعرف شر إسرائيل .

Kafatan musulumai ba su cin naman alhanzir.

المسلمون كافة لا يأكلون لحم الخنزير .

Duk kafatan mutanen gidanmu ba wanda ba ya girmama mahaifinsu.

كافة أهل بلدي يحترمون أباءهم .

## : Kafiri ← كافر

Wanda ya yi salla da gangan ba tare da alwalla ba wannan kafiri ne.

من صلي عمدا دون وضوء كافر .

Ya kama kan kafiri ya murɗe.

أمسك رأس الكافر ولواها .

Ya ce sai shi kafiri dan kafiri jikan kafiri.

قال هو كافر ابن كافر حفيد كافر .

Wani kafiri ya laɓaɓo ya sace mini tufafina.

واحد كافر تسلل وسرق ثيابي .

Ka ga lalatacciyar banza kafira, kai dai ne kafiri.

انظر الفاسدة الكافرة ، وأنت أيضا كافر .

In ka halaka mun halaka mun kuma fada a hannan kafirai.

إذا هلكت هلكنا ووقعنا في يد الكافرين .

Suka yi wa kafirai zobe.

أحاطوا بالكفار .

Ya halicci wuta ya tanade ta gidan azaba ne ga wannan da ya kafirci.

خلق النار وأعدها دار عذاب لمن كفر .

Ba a kafirta daya daga cikin masu alƙibla don ya aikata zunubi.

لا يُكَفِّر أحد ممن يتوجهون إلى القبلة لأنه عمل ذنبا .



www.alkottob.com

## : **Kaffara** ← كفارة

| | |
|---|---|
| Ba kaffara a kansa. | ليس عليه كفارة . |
| Kaffara tana wajaba a kansa. | تجب عليه الكفارة . |
| Kaffararsa ita ce ciyad da musakai aittin. | كفارته هي إطعام ستين مسكينا . |
| Ya yi kaffara da 'yanta baiwa. | كفّر بتحرير رقبة (عبد) . |

## : **Kafur** ← كافور

| | |
|---|---|
| Daga Ƙaeshe za'a sa kafur. | في الأخيرة يوضع كافور . |
| Ka sayo mini kafur daga kasuwa. | اشترلي كافوراً من السوق . |
| Na sa kafur a cikin adakata. | وضعت الكافور في حقيبتي . |
| Wannan kafur ɗin yana da Ƙamshi. | هذا الكافور له رائحة جيدة . |

## : **Likkafani** ← كفن

| | |
|---|---|
| Ya yi masa likkafini da tufafi uku farare. | كفن في ثلاثة أثواب بيض . |
| Za'a nemi likkafani daga cikin dukiyar mijinta. | يؤخذ ثمن الكفن من مال زوجها . |
| Ya ɗauki gawar ya sa cikin likkafani. | أخذ الجثة ووضعها في الكفن . |
| An haɗa shi da likkafani. | كُفِّن . |

## .: **Kifaya** ← كفاية

| | |
|---|---|
| Faralu kifaya. | فرض كفاية . |
| Sallar jana'iza faralu kifaya ce. | صلاة الجنازة فرض كفاية . |
| Kar ka bar faralu ainihi don aikata faralu kifaya. | لا تترك فرض العين لتعمل فرض الكفاية . |



www.alkottob.com

Ba wanɗa bai san ma'anar falalu kifaya ba a cikin musulumai.

لا أحد لايعرف معنى فرض كفاية بين المسلمين .

## كلام ← Kalami :

Sarki ya ji daɗin kalaminsa. سمع الأمير حلو كلامه .

Da jin wannan kalami nawa sai ya yi ƙara. عندما سمع كلامي هذا صرخ .

Bayan da sarki ya mai da kalami sai yarinyar ta ce , zaka sami da namiji. بعد أن كرر الأمير الكلام قالت الفتاة ، سترزق طفلا ذكرا .

## كلمة ← Kalma :

An rubuta kalmar shahada a gefensa. كُتِبت كلمة الشهادة على طرفة .

Wace kalma ce ka rubuta wa sarkin musulunci?

اى كلمة كتبت لأمير المسلمين.

Kudin buga waya sule ne in kalmomin da ka yi amfani da su wuce takwas.

ثمن أرسال البرقية شلن إذا كانت الكلمات التي استفدت بها — في البرقية — بلغت الثمانية .

Don ka san kalmomi uku cikin turanci sai ka ce ka ji harshen ?

لأنك عرفت ثلاثة كلمات في الانجليزية تقول أنك تعرف اللغة ؟ .

## كل يوم ← Kullum :

تأتي بمعنى دائما

Kullum in na dube shi , in tuna da kai. دائما إذا نظرت إليه أتذكرك .

Kullum in an koya musa aiki shi sai ya yi ta wasa sai ya samu sifiri.

دائما إذا علمتهم عملا ، يلعب كثيرا ثم ينال صفرا .

Matarsa kullum tana fama da shi a kan haka. زوجته دائما تعاني معه من هذا.

Kullu yaumin bayan an yi sahuri , an dinga kirna gwauro irin na tsiya ke nan. كل يوم بعد تناول السحور ، يُستدعي رجل أعزب من الفقراء .



www.alkottob.com

## : **Kallafa** ← كَلِفَ

تأتي بمعنى تعلّق

Ya ƙallafa ransa ga tafiya. علّق نفسة بالسفر .
Ya ƙallafa ransa ga kańarin nan. علق نفسة بهذا الكناري .
Ta ɗauki kanta ta ƙallafa kan Audu. شغلت نفسها بحب عبده .

## : **Kamar** ← كما

تأتي بمعنى مثل أو حوالي أو كأن

Dokin nan tashi yake kamar tsuntsu. هذا الحصان يطير مثل الطير .
Ga shi musulmi ne amma zaciyarsa kamar ta kafiri.
هاهو مسلم ولكن قلبة مثل الكافر .
Na sake yin tafiya kamar kwana ashirin. مرة أخرى سرت حوالي عشرين يوماً.
Ta kwanta rigingine , ta buɗe baki kamar ta mutu.
رقدت على ظهراها ، وفتحت فمها كأنها ماتت .
Kamar yadda musulmi ba ya son kafiri , haka ba ya son ko hanya ta gama mu da shi. كما لايحب المسلم الكافر ، هكذا لا أحب الطريق الذي يجمعني به .
Ka samu aboki wanda ya kamance ka. وجدت صديقا يشبهك .

## : **Kamisliki** ← كمثلك

Kano kamusliki alfun. مدينة كانو تساوي ألف .

## : **Kamili** ← كامل

Ga wani saurayi kamili can a ƙofar gida yana sallame ka.
ها شاب كامل على باب المنزل يستأذنك .



www.alkottob.com

Wannan mutumin kamili ne.

هذا الرجل كامل .

## : Kammala ← كَمَّل

An kammala aiki.

أكمل العمل .

Ba na karɓi kuɗin sai ka kammala ba.

لن آخذ المال إلا كاملاً .

Ina jira ne , ka gama sauka AlƘur'ani , ka sami ilmi ka zama kammalallen mutum.

انتظر أن تحفظ القرآن ، وتنال العلم وتصير رجلا كاملاً .

## : Kanari ← كناري

Ya kama kanari.

أمسك طائر الكناري .

Ya ƙallafa ransa ga kanarin nan.

علق نفسة بهذا الكناري .

Wannan ya nuna cewa kanari ba shi da girman kai ke nan.

هذا يظهر أن الكناري ليس متكبّرا .

## : Kinaya ← كناية

Musa yana so ya tambaye ni kudi amma bai tambaye ni a sarai ba , sai dai ya yi mini kinaya.

موسى يريد أن يسألني مالا، ولم يسألني صراحة فكنّي بطلبة.

Kinaya tana daga cikin ilmin balaga a larabci.

الكناية من علم البلاغة في العربية .

In ka yi wa mai hankali kinaya yana fahinta.

إذا خاطبت الذكي بالكناية فهم .

## : Kaifiyya ← كيفية

Ba wanda ya san kaifiyya inda rai yake sai Allah.

لا أحد يعرف أين تكون الروح إلا الله .



www.alkottob.com

In zaka ba da labari ka faɗa kaifiyyar yadda ya auku.

إذا نقلت خبرا فقلة كما وقع .

Musa ya fahinci kaifiyyar gyaran mota. موسى عرف كيف يصلح السيارة .

## : Kausara ← كوثر

Babban tabkin aljanna shi ne Alkausara. اكبر أنهار الجنة الكوثر .

Allah ka shayad da mu ruwan Alkausara. اللهم اسقنا ماء الكوثر .

Babu musulumin da ba ya fatan ya sha ruwan Alkausara.

لا يوجد مسلم لا يتمنى أن يشرب ماء الكوثر .

★ ★ ★



www.alkottob.com

## : Lu'ulu'u ← لؤلؤ

Zaka tarad da ita rufe da murfin lu'ulu'u. ستجدها مغطاة بغطاء من اللؤلؤ .
Ta ci ado da kaya iri iri na zinari da lu'ulu'u da jauhar.
تزينت بحلي مختلفة من الذهب واللؤلؤ والجوهر .
Muka iske dukiya bisa dukiya lu'ulu'u da murjani.
وجدنا ثروة فوق ثروة من اللؤلؤ والمرجان .

## : La'ilaha illa llah ← لا إله إلا الله

Za'a laƙƙana masa fadar «la'ilaha illa llahu». سيلقنة قول«لا إله إلا الله» .

## : Labudda ← لابد

Ya ce labudda ikon Allah ya wuce haka. قال لابد قدرة الله تجاوز ذلك .
Labudda haka aka yi in sha 'allahu. لابد أن يفعل هكذا إن شاء الله .

## : Linzami ← لجام

Duk abin nan kuwa dokinsa ba sirdi balle likkafa ko linzami.
كل هذا وحصانة بلا سرج ولا ركاب ولا لجام .
Ya ja linzami ya tsaye. شدَّ اللجام فوقف .
Ya juya linzami ya kama hanyar da ya fito.
أدار اللجام واتخذ الطريق الذي خرج منه .
Ya hau dokin ba tare da linzami ba. ركب الحصان بدون لجام .



www.alkottob.com

## : Lahadu ← لَحْد

Lahadu shi ya fi sayuwa ga ma'abutan ilmi daga tsaga Ƙasa.

اللحد أحب إلى أهل العلم من شق الأرض .

## : Lahani ← لَحْنٌ

تعنى العيب

Ita ba ta da wani lahani. ليس فيها أي عيب .

Mun koyi amfanin tsabta , mun kuma san lahanin Ƙazanta.

تعلمنا فائدة النظافة ، وعرفنا عيب القذارة .

Shi ma yana da lahani ga hannuwansa. هو أيضا فيه عيب في يدية .

Tsananin sanyi ya lahanta shi. شدة البرد عابتة .

Tun da ya lahanta shi haka. طالما عابة كذلك .

## : Lazimta ← لَزِمَ

Ciyarwa ba ya lazimtar namji sai na matarsa kawai.

لا يلزم الرجل النفقة إلا على زوجته فقط .

An yi hani da yin saki cikin haila idan kuma har ya yi sakin ya lizimce shi. نُهِي أن يطلق في حيض ، فأن طلق لزمة .

Wannan abin da ya lizimce shi. هذا ما لزمة .

## : La'ana ← لعن

Miji shi ne zai fara kuma zai yi la'ana da shaiduwa ga Allah sau huɗu.

يبدأ الزوج فَيَلْعَنُ أربع مرات شهادة بالله .

Matar ta yi la'ana sau huɗu. تلعن المرأة أربع مرات .



www.alkottob.com

Don albarka kuka same shi , amma zai zama la'ana , zai jawo muku abin kunya. طلبتموة من أجل البركة ، ولكن سيصير لعنة ، وسيجر لكم العار .

Ta gaya masa dukan abin da tsakaninsu da Audu , da yadda shi ne ya la'anta shi ya lalace duniya.

قالت له كل مابينها وبين عبده ، وكيف لعنة حتى يفسد في الحياة .

Ka la'ance shi domin shi maƙiyin 'yan Adam ne. لعنته لأنه عدوبني آدم.

Ni da ku aurad da ita ga wannan la'anannen gara ku ba da ni.

زوجوها لي أفضل من تزويجها لهذا الملعون .

Allah ya raba ka da la'anannun mata irin matan nan su biyu.

نجاك الله من هؤلاء النسوة الملعونات مثل هاتين المرأتين .

## : Lugga ← لغة

Ba wata lugga da zata gagare shi har mutane suna ce masa malam ilmi. لا توجد لغة تتعذر عليه حتى سماه الناس أستاذ العلم .

Wane fanni ka ɗauka na ilmi , ka koya tafsiri ko lugga ?

أي فن أخذت من العلم ، تعلمت التفسير أم اللغة ؟

## : Lafazi ← لفظ

تأتي بمعنى كلمة أو أسلوب

Hausa ba ta rasa marubuta ba , masu lafazi da daɗin labaru.

لا ينقص الهوسا الكتاب أصحاب الكلمة الجيدة والقصص الممتع .

Ga shi dai kana da sani da lafazi irin na larabawa.

ها لديك معرفة وأسلوب كأسلوب العرب .

In ka yi zance da shi , kai ji lafazinsa sai ka ce ba a daji ya girma ba.

إذا تحدثت معه تسمع أسلوبية كأنه لم ينشأ في البادية .



www.alkottob.com

## : Lakabi ← لَقَبٌ

Yanzu ita ma tana da ikon kirana da wannan lakabi.

الآن تستطيع هي أن تناديني بهذا اللقب .

A cikin gidan matar sarki da dangi sai lakabi iri-iri suka sa wa yaron.

في بيت النساء الأمير وأقاربة يسمون الصبي بلقب مختلف .

## : Loma ← لقمة

Loma ta fadi kasa. وقعت اللقمة على الأرض .

Bai sa ko loma bakinsa ba don bakin ciki.

لم يضع ولو لقمة في فمة بسبب الحزن .

Kafin mai gida ya kai loma guda shi ya kai uku.

قبل أن يأخذ صاحب البيت لقمة واحدة ، يأخذ هو ثلاث .

Ya budi baki zai sa wannan lomar sa'an nan ya dauki sanda ya kore shi. فتح فمة سيضع هذه اللقمة ، فأخذ العصا وطردة .

## :Lakkana ← لَقَّن

لقن أو تلقّى

Za'a lakkana masa fadar «la'ilaha illallahu». سيلقنة قول «لا إله إلا الله» .

Na lakkanci ilmin larabaci ne daga malamai na larabawa.

تلقيت علم العربية من أساتذة عرب .

Na hadu da wani likita wanda ya lakkanci ciwon idon.

قابلت طبيبا تلقى علم مرض العيون .

## : Lakin ← لكن

Lakin ni ba bawanka ba ne. لكني لست عبدك .



www.alkottob.com

## : Lum'a ← لُمْعَةٌ

Lum'a ita ce ɗan wani wuri da aka bari wanda ruwa bai taɓa shi ba.

اللمعة هي المكان الصغير الذي تُرِك ولم يمسة الماء .

Wanda ya manta da lum'a , sai ya wanke wurin luma'ar tare da niyya.

من نسي لمعة وجب غسل مكان اللمعة مه النية .

## : Allo ← لَوْح

Daga allo yake dubawa. ينظر في اللوح .

Kada maras alwalla ya taba allon da aka rubuta Alƙur'ani mai girma.

لا يمس غير المتوضيء اللوح الذي كتب فيه القرآن العظيم .

Ya fitar da sabon allo. خرج بلوح جديد أي خرج بفكرة جديدة .

## : Luɗu ← لوط

Wanda ya aikata aikin mutanen ludu da namiji balagagge wanda ya biya masa, sai a jefe su. من فَعَل فِعْل قوم لوط بذكر بالغ أطاعة رُجما .

Wanda ya ce da wani mutum kai mai ludu , sai a yi masa haddi.

من قال لرجل يالوطي حُدَّ .

## : Launi ← لَوْن

Ruwan nan launinsa ya jirkita. هذا الماء لونة تغيَّر .

Za'a nisanci dukan tufa mai launi baƙi. يبتعد عن كل ثوب لونة أسود .

Launin jikin waɗansu mutane ƙasashen nan rawaya ne kamar Sinawa.

لون جسم بعض سكان هذه البلاد أصفر مثل الصينيين .

Launin jikinsu kamar na mutanen Sudan.

لون جسمهم كلون جسم أهل السودان .



www.alkottob.com

### : Lailatul Ƙadari ← ليلة القدر

Kamar wanda aka haifa a daren lailatul Ƙadari. كمن ولد في ليلة القدر .

### : Lemon ← ليمون

Watakila zasu sha rake da tumatir da lemon zaƙi da inabi.
ربما شربوا عصير قصب أو طماطم أو ليمون حلو أو عنب .

Zaku sami 'ya'yan itatuwa kamar su lemon zaƙi su mangwaro masu gina jiki. ستجدون ثمار الأشجار مثل الليمون الحلو والمانجو التي تُبني الجسم .

★★★



www.alkottob.com

## : Metan ← مئتان

Kafin gobe war haka ya gina mini gida mai tsawo taki metan fadi taki dari. قبل الغد في مثل هذا الوقت بني لي منزلا طولة مئتا خطوة وعرضة مائة .
Na ba wa abokina rancen fam metan. أعطيت صديقي قرضا مئتي جنية .
Na samu fam metan. وجدت مئتي جنية .

## : Mawallafi ← مؤلف

Ya zama mabudi na ga mai niyyar zama mawallafi.
صار مفتاحا لمن ينوي أن يصير مؤلّفا .
Mawallafin «Magana jari ce» mutum mai ƙoƙari.
مؤلف «الكلام رأس مال» رجل مجتهد .
Hausawa suna da mawllafa masu yawa. الهوساويون لديهم مؤلفون كثيرون .

## : Mamu ← مأموم

Kafa sutura ga wanda ba mamu ba. وضع السترة لغير المأموم .
Rafkannuwar mamu liman din ya dauke masa. سهو المأموم يتحمله الإمام .
Idan liman ya yi rafkannuwa da tauyewa ko ƙari to , shi mamu ya yi masa tasbihi. إذا سها الإمام بنقص أو زيادة سبح به المأمون .

## : Ma'muna ← مأمونة

Wadda kuma ta isa har ƙwaƙalwa, to, ita ake kira ma'muna.
والتي تصل إلى الدماغ فهي المأمونة .



www.alkottob.com

A kan ba da sulusin diyya game da ma'muna. يُدفَع ثلث الدية للمأمونة .

## : Mummuni ← مؤمن

Na kama kaina sai ka ce wani mummuni. عففت نفسي كأني مؤمن .
Dan birni ya yi saƙo , yana jin wa'azi kamar wani mummuni.
ابن المدينة أصغى يستمع الوعظ كأنه رجل مؤمن .
Takarda ta fito daga sarkin mummunai. خرجت الرسالة من أمير المؤمنين .
Hakika mummunai za a jarraba su cikin ƙabarinsu.
إن المؤمنين سيسألون في قبورهم .

## : Mubasharatan أو Mubashara ← مباشرة

مباشرة أو مداعبة

Daga makaranta na zarce zuwa gida mubasharatan.
خرجت من المدرسة إلى البيت مباشرة .
Kada ka yi mubashara da matar da ba taka ba ce.
لا تداعب المرأة التي ليست امرأتك .
Mubasgaratar mace da ranar azumi abu ne mai hadari.
مداعبة النساء في يوم الصيام أمر خطير .

## : Mubaya'a ← مبايعة

Ya shiga ya yi gaisuwa ya kuma yi mubaya'a. دخل فحيًّا وبايع .
Suka yi masa mubaya'a. بايعوه .
Bari dai mu fara yin mubaya'a. دعنا نبدأ بالمبايعة .



www.alkottob.com

## : Mubayyani ← مبين

Ya faralta ayyukan biyayya da gabubba mabayyana zasu aikata.

فَرَضَ على الجوارح الظاهرة أعمالا من الطاعات تعملها .

Cikin ya zama mabayyani.

صار الحمل ظاهرا .

Ta kasance a cikin littafi mabayyani.

تكون في كتاب مبين .

Shi haske ne mabayyani.

هو نور مبين .

## : Mata'i ← متاع

متاع أو حاجة أو منفعة

Mutane da yawa suna ƙarya ne don ɗan mata'in da zasu samu.

كثير من الناس يكذبون لينالوا منفعة قليلة .

Im mutane suka son zasu wani mata'i daga gare ka , kome ka nema a gare su ba wuya sun yi maka.

إذا أراد الناس أن ينالوا منفعة منك ، كل ما تطلبة منهم يؤدونة لك بسهولة .

Musa ya buge ni don ya san , ba wani mata'i da zai samu a gare ni.

موسى ضربني لأنة ، لن ينال أي منفعة مني .

## : Mutu'a ← متعة

Yin azumi kwana biyu da ke bayan ranar babbar salla , bai inganta ba , sai mai yin mutu'a wanda bai iya samun hadaya.

صوم اليومين التالين لعيد الأضحى لا يجوز إلا للتمتع الذي لا يجد هديا .

## : Misƙala ← مثقال

Ba ku kula da sha'aninsa ba ko misƙala zarratin.

لا تهتمون بأمرة ولو مثقال ذرة .



www.alkottob.com

Ba na son ƙarya ko da misƙala zarratin. لا أحب الكذاب ولو مثقال ذرة .

: **Musula** ← مَثَّل

مثل بالجثة

Wanda ya yi musula da bawansa musula a sarari na daga yanke wata gaba ya 'yantu gare shi. من مثَّل بعبده مثلة ظاهرة من قطع جارحة عتق عليه .

: **Misali** ← مثال

مثال أو مِثْل

Wanda ya aikata aikin aheri ko da misalin zarra ce zai gan shi.
من يعمل عمل خير ولو مثل ذرة سيراه.
Bai kai misalin yin zakka ba. لم يصل مثال الزكاة .
Namiji da misalin rabon mata biyu. للذكر مثل حظ الأنثيين .
Na misalta maka daga waɗancan abubuwan da zasu amfana da kiyaye shi. مثلت لك من ذلك ما ينتفعون بحفظة .
Na misalta wa magini yadda zai gina mini gidana.
وصفت للبنّاء كيف يبني منزلي .
Ka ka ya yi mata azaba misalin shekara biyu.
هكذا كال لها العذاب حوالي سنتين .
Duk mutanen garin kowa yana da nadin baƙin rawani misalin yadi uku. كا أهل المدينة ، كل يلف عمامة سوداء حوالي ثلاث ياردات .
Ya ga yaro misalin dan shekara huɗu tsaye.
رأي ولدا ابن حوالي أربع سنوات واقفا .
Ran nan ya isa misalin mutane ya zama jarumin gaske.
ذات يوم بلغ غاية جمال الرجال وصار شجاعا جدًّا .
Bawa daya ya kama , amma bawan nan ya isa misali.
عبدا واحد أسر ، ولكن هذا العبد بلغ الغاية في الجمال .



www.alkottob.com

## : Masalan ← مَثَلاً

Masalan , na yi da kaina.
مثلا ، سأعملة بنفسي .
Ba ni sule goma , masalan goma sḥa biyar.
أعطني عشر شلنات ، أو مثلا خمسة عشر .

## : Mujaddadi ← مُجَدِّد

Yau na haɗu da jikan mujaddadi.
اليوم قابلت حفيد المجدِّد .
A cikin kowane ƙarni ana samu mujaddadi.
في كل قرن يأتي مجدِّدٌ .
Allah ya sa mu cikin ceton Annabinsa ya ko ba mu albarkacinku mujaddadai.
جعلنا الله في حماية نبية ووهبنا بركتكم — أيها — المجددون .

## : Mujaza ← مجاز

تأتي بمعنى سبب

Kar ka zama mujazar halaka jama'a.
لا تكن سببا في هلاك الناس .
Wani lokaci dukiya tana zama mujazar taɓewa.
أحيانا تصير الثروة سببا في الضلال .
Aiki da ilmin addini yana zama mujazar shiga aljanna.
العمل بعلم الدين يصير سببا لدخول الجنة .

## : Majusi ← مجوسي

Mutumin nan wani majusi ne.
هذا الرجل مجوسي .
Majusi ya musulinta.
أسلم مجوسي .
Kada ka ci yankan majusai.
لا تأكل ما ذبح المجوس .
Ba a ci dabbar da majusai suka yanta.
لا تأكل من لحم الدابة التي ذبحها المجوس .



www.alkottob.com

## : Majalla ← مجلة

Wata majalla mai fitowa duk wata uku. مجلة تظهر كل ثلاثة أشهر .

Na sayi majallar Umma. اشتريت مجلة الأمة .

Makarantammu ta yi majalla. أصدر معهدنا مجلة .

## : Majalisa ← مَجْلس

Sarki ya kore su daga majalisa. طردهم من المجلس .

Sarki ya isa majalisa ya harɗe , mutane duka na kewaye da shi.

وصل الأمير المجلس وجلس وأحاط الناس به .

Sarkin fawa ya sa su gaba har majalisar alƙali.

رئيس القصابين دفعهم أمامة حتى مجلس القاضي .

## : Majanuni ← مجنون

Ba mai yawo tsirara sai majanuni. لا يسير عاريا إلا مجنون .

In kana zama da majanunai sai ka zama majanuni.

إذا جلست مع المجانين تصير مجنونا .

Wata mace majanuniya ta doke dana. امرأة مجنونة ضربت ابني .

## : Majahuli ← مجهول

Ba za'a sayar da abu ba a kan abin da ke majahuli.

لا يباع شيء بشيء مجهول .

Kar ka zama majahuli alhali a tsakanin mutane.

لا تكن مجهول الحال بين الناس .

Garba ya sayo wata majahular mota ba wanda ya san haƙiƙarta.

أبو بكر اشتري سيارة مجهولة ، لا أحد يعرف حقيقتها .



www.alkottob.com

Mu'amala da majahulan mutane ba ta da dadi.

التعامل مه الناس المجهولين ليس مريحاً .

## : Muhibba ← محب

تأتي بمعنى المحبة

Kyauta tana jawo muhibba. الهدية تجلب المحبة .

Tana da muhibba ga ta kuma da kayan fasali. محبوبة وكذلك حسنة التربية .

## : Mahaddaci ← محدث

تأتي بمعنى حافظ القرآن

Ina tsammani muryar mahaddacin malamin nan ce.

أظن هذا صوت الأستاذ الحافظ للقرآن .

Ibrahimu mahaddacin Alƙur'ani ce. إبراهيم حافظ للقرآن .

A cikin makarantammu akwai mahaddata masu yawa.

في مدرستنا يوجد كثير من الحافظين ـ القرآن ـ

## : Mahadudi ← محدود

Ina zuwa makaranta a lokaci mahadudi. أذهب إلى المدرسة في وقت محدود .

Ni ban ƙayyade kuɗi mahadudi ba , a bisa sadakin 'yata ba.

لم أقيد مالا محددا لصداق ابنتي .

Hausa tana da ƙa'idodi mahdudai. الهوسا لها قواعد محدودة .

## : Almuharram ← مُحَرَّم

Na yi umura a cikin watan Almuharram. أديت عُمْرةً في شهر محرم .



www.alkottob.com

Shekarar hijiriyya tana farawa ne daga watan Almuharram.

السنة الهجرية تبدأ من شهر المحرم .

Matata ta haihu a cikin watan Almuharram. زوجتي وضعت في شهر المحرم .

## : Maharbi ← محارب

تأتي بمعنى الصياد

Ya ce wa maharbi alhamdu lillahi na gode. قال للصياد الحمد لله أشكرك .

Maharbi ya harbi shaho. اصطاد الصياد صقرا .

Wannan bakan na maharbi ne. هذا قوس الصياد .

Maharbi ya tafi farauta. ذهب الصياد للصيد .

## : Maharrami ← مِحْرَّمٌ

Haramun ne mace ta kadaita da wanda ba maharraminta.

حرام أن تنفرد المرأة بمن ليس محرماً لها .

'Ya maharrama ce a wajen ubanta. البنت محرمة من ناحية أبيها .

## : Mahalli ← محل

Me ya kawo ka nan ? me ya rude ka har da ka za mahallarka ?

ماذا جاء بك إلى هنا ؟ ماذا خدعك حتى جئت إلى محلك ؟

Im mutum ba shi da mahallin kwana a cikin gari yana cikin wahala.

إذا لم يكن للإنسان محل للنوم في المدينة يقع في مشكلة .

Mahalli mafi alheri ga mace gidan mijinta. أفضل مكان للمرأة بيت زوجها .

## : Muhallili ← مُحَلِّلٌ

Babu laifi ga tseren dawaki , idan kuma har sun sanya wani muhallili a tsakaninsu. لا بأس بسباق الخيل ، وإن جعلوا شيئا محللا بينهم .



www.alkottob.com

## محسد ← Mahassada :

تأتي بمعنى الحسود

Mahassada ba ya shugabanci.
الحسود لا يسود .

Rayuwa cikin mahassada tana da wuya.
الحياة مع الحسود صعبة .

Mahasadansa suna ta murna sai ka ce wadanda aka ba su gashin tozo.
صار حسادة مسرورين جدا كمن أعطيتهم سنام الجمل .

## محمدية ← Muhammadiyya :

تعنى الإسلام

Farkin nan na da wani kare wanda yake jin so , abin har ya wuce na muhammadiyya.

هذا التاجر له كلب يشعر نحوه بالحب ، لدرجة تجاوزت حب الإسلام .

Da danka ya taso yi ƙoƙarin kai shi makarantar muhammadiyya.

إذا شب ابنك حاول أن تدخله المدرسة الإسلامية .

Mu ba mu son wata makaranta ba sai ta muhammadiyya.

نحن لا نحب إلا المدرسة الإسلامية .

## محاورة ← Muhawara :

Muhawara ta shiga tsakanin malami da almajiransa.

بدأت المحاورة بين الأستاذ وتلميذه .

An yi muhawara a kan hakkin mata.
قامت محاورة حول حق النساء .

Su duka biyu suka mutu , shi ya sa wannan muhawara.

الإثنان كلاهما ماتا ، وهو السبب في هذه المحاورة .



www.alkottob.com

## : Muhutari أو Muhtari ← مختار

Lokacin sallar azahar muhtari shi ne tun daga zawwal.

وقت صلاة الظهر المختار هو من الزوال .

Da rana ta faɗi , shi ne muhutarin lokacin sallar magariba.

عند غروب الشمس هو الوقت المختار لصلاة المغرب .

Sunan abokina Muhutari. اسم صديقي مختار .

## : Mukhatali'ati ← مُخْتَلِعَةُ

Babu ciyarwa ga mukhatali'ati. لا توجد نفقة للمختلعة .

## : Mahaluƙi ← مخلوق

Ba wani mahaluki nan daga ni sai kai. لا يوجد مخلوق هنا إلا أنا وأنت .

Wa ya sace tufafina ? lalle dai ba wani mahaluki ba ne , don ni kaɗai na shigo. من سرق ثيابي ؟ لابد أنه ليس مخلوقا ، لأني دخلت وحدى .

Ban taba ganin wani mahaluki ba , sai fa kai yau.

لم أر أي مخلوق أبداً ، إلا أنت اليوم .

## : Mudu ← مُدٌّ

Sa'i shi ne mudu huɗu na irin mudunnabi.

الصاع هو أربع من مثل مدّ النبي .

Manzon Allah ya yi alwalla da ruwa cikin mudu-nnabi.

توضأ الرسول بماء في مد النبي .

Mudunnabi awon riɗili da ɗaya bisa ukunsa. مد النبي يزيد رطل وثلث .

Na yi sadaka da mudu biyu na shinkafa. تصدقت بمد من الأرز .

Mudu hudu da shinkafa ya ishe ni abincin rana.

أربعة مد من الأرز تكفيني طعاما في اليوم .



www.alkottob.com

## مدّة ← Mudda :

Na yi jiran abokina mudda mai tsawo amma bai zo ba.

انتظرت صديقي مدة طويلة ولكن لم يأت .

Salla ba ta dauka mudda mai tsawo. الصلاة لا تأخذ مدة طويلة .

Ni ba na iya jiran mutum mudda mai tsawo.

لا استطيع أن انتظر الإنسان مدة طويلة .

## مُدَبَّرة ← Madabbara :

Ko wace mace mai ciki ɗanta ne zai gaji matsayinta ga fansa ko kuma madabbara. كل امرأة ذات حمل ابنها يرث منزلتها من معتقة إلى مُدَبَّرة .

## مَدَدٌ ← Madadi :

تأتي بمعنى بَدَلٌ

Allah ya azurta ni da madadin dana da ya mutu.

رزقني الله بدلاً من ابني الذي مات .

Sarki ya ba ni doki a madadin nawa da ya karba.

أعطاني الأمير حصانا بدلا من حصاني الذي أخذة .

Zan ba ka madadin kuɗinta da na karɓa.

سأعطيك بدل مالك الذي أخذته .

## مداراة ← Madarati :

تأتي بمعنى الشيء الكمالي أو الإضافي

Bayan abinci wajibi ina kawo ɗan abin mudarati gidana.

بعد الطعام يجب أن أحضر قليلا من الأشياء الإضافية إلى بيتي .



www.alkottob.com

Ba'a rasa abin mudarati daga gare ka ba. لا تُعْدَم الأشياء الإضافية لديك .

Ba'a samu wajibi daga gare ka ba , balle abin mudarati.

لا يوجد واجب لديك ولا غير واجب .

## : Madahu ← مِدْحٌ

Yau mun karatun madahu. اليوم درسنا المدح .

A cikin madahu akwai abubuwan da ba gaskiya ba ne.

في المدح توجد أمور ليست حقيقية .

Shauƙi ya yi ƙoƙari a cikin madahunsa. شوقي برع في مدحة .

## : Madina ← مدينة

Ya fi kyau mu ziyarci kabarin fiyayyen halita a Madina.

الأفضل أن نزور أفضل الخلق في المدينة .

Ba abin da nake so illa in samu dama mu ziyarci Annabi a Madina.

لا أريد شيئا إلا أن نجد الفرصة لنزور النبي في المدينة .

## : Muzakara ← مذاكرة

Yawan muzakara zai sa ka sami makkana wajen rubutar jarrabawa.

كثرة المذاكرة تجعلك متثبتا من الإجابة في الإختبار .

Mun yi muzakara tare da abokina. ذاكرنا مع صديقي .

Ni kadai nake yi muzakara a ɗakina. أنا وحدى أذاكر في حجرتي .

## : Maziyyi ← مَذْي

Abin da ake ce ma maziyyi shi ne wani ruwa da ke fitowa yayin jin daɗi ƙarami. مايقال له المذي هو ماء يخرج عند الشعور باللذة الصغري .



www.alkottob.com

Wanken azzakari dukansa wajibi ne a kansa in maziyyı ya fito masa.

غسل الذكر كله واجب عليه إن خرج منه المذْي .

Karuruwa su ne bawali da bayan gida da iska da maziyyi da wadiyyi.

الأحداث هي البول والغائط والريح والمدي والودي .

## مُرَبَّع ← Murabba'i :

Na gina wani ɗaki murabba'i.

بنيت منزلا مربعاً .

Sarki ya ba ni fili murabba'i.

الأمير وهبني قطعة أرض مربعةً .

Tasan nan me ya sa aka yi ta murabba'a ?

هذه الطاسة لماذا صنعت مربعة ؟

## مَرْتَبة ← Martaba :

تعني المنزلة العالية

Jama'a suka yi ta mamaki martabar ruwan Bagaja.

تعجب الناس كثيرا من منزلة الماء الشافي .

Ina da martaba.

لي منزلة عالية .

Mutum mai martaba ne.

رجل له منزلة عالية .

## مرجان ← Murjani :

Ran nan na fita wajen garin shan iska na tsinto wani murjani.

ذات يوم خرجت لأتنسم الهواء خارج المدينة ، فوجدت عقد مرجان .

Aka sato masa murjanin uwargidan sarki.

سرق العقد المرجان من ربة بيت الأمير .

Aka yi ta neman murjani ƙasa da sama ba a gani ba.

بحث عن العقد المرجان في الأرض والسماء فلم يجدوة .



www.alkottob.com

## مَرْحَباً ← Maraba :

Sarki garin ya yi maraba da shi. أمير المدينة رحَّب به .

Suka kewaye shi suna yi masa maraba. أحاطوا به يرحبون به .

Ta yi wuf , ta je , ta sungume ta , tana kuka tana yi mata maraba.

هبت قائمة ، وذهبت وعانقتها ، وهي تبكي وترحب بها .

Ta marabace shi ta kawo masa ruwa ya sha.

رحبت به وأحضرت له الماء فشرب .

Maraba da maigida. مرحباً ياسيدي .

## مارد ← Maridi أو Mariddi :

Nan da nan maridi ya kekketa tsohuwa. في الحال قطَّع المارد المرأة العجوز .

Ka kubutad da mu daga sharrin dan hari mariddi.

لقد انقذتني من شر هذا المغير المتمرد .

Kai lalataccen mariddi barawo. أنت لص فاسد متمرد .

Akwai wadansu maridai masu jiran rijiyoyin nan.

يوجد بعض المردة يحرسون فى هذه الآبار .

Kome ka sara da shi ya karye , kome maridancin aljani.

أي شيء تضربة به ينكسر مهما كان تمرد الجن .

## مُراد ← Muradi :

### وتأتي بمعنى هدف

Abin da na aikata maka ya ƙare muradina kuwa ya biya.

ما فعلته لك أنتهي وقُضِي مرادي .

Ya zama babban muradinsa ne ya bar garinsa da gidansa da dukan abin da ya mallaka. صار هدفة الكبير أن يترك بلدة ومنزلة وكل ما يملك .

Da ya yi gamu da layar muradinsa ya biya ke nan.

عندما لقي التميمة تحقق هدفة .



www.alkottob.com

## مروة ← **Marwa** :

Ya gangaro zuwa Marwa. نزل إلى المروة .

Idan ya iso Marwa zai tsaya a kanta ya yi addu'a.

إذا وصل إلى المروة وقف عليها ودعا .

Na yi sa'ayi tsakanin Safa da Marwa sau bakwai.

سعيت بين الصفا والمروة سبع مرات .

## مزدلفة ← **Muzdalifa** :

Yana sallara magariba da lisha a Muzdalifa. صلى المغرب والعشاء في مزدلفة.

Ya sake bin liman zuwa Muzdalifa inda zasu yi sallar magariba da lisha. تبع الإمام مرة أخرى إلى مزدلفة حيث يصلون المغرب والعشاء .

Kwanan Muzdalifa sunna ce wajiba. المبيت بمزدلفة سنّة واجبة .

## ميزان ← **Mizani** :

Allah ya sa mizanimmu ya yi nauyi da aikin alheri.

اللهم اجعل ميزاننا يثقل بعمل الخير .

Wanda mizaninsa ya yi rinjayi da aikin zunubi ya wulakanta.

من ثقل ميزانة بالذنوب احتُقِرَ .

Ranar kiyama Allah zai sanya mizani. يوم القيامة يقيم الله الميزان .

## مسألة ← **Matsala** أو **Mas'ala** :

تأتي بمعنى الأمر أو المشكلة

Sun sami shiga ba tare da wata babbar matsala ba.

دخلوا بدون مشكلة كبيرة .



www.alkottob.com

Yanzu kuma na fahimci yadda matsalar take.

فهمت الآن كيف يكون الأمر .

Masa'alar ba ta zama mushtarika ba. المسألة ليست مشتركة .

Zamu gani da yawa daga mas'alolin taimama.

سنري كثيرا من مسائل التيمم .

## : Masbuƙi ← مسبوق

Masbuƙi shi ne wanda ya zo daga baya.

المسبوق هو من جاء بعد ذلك .

Idan masbuƙi ya yi rafkannuwa bayan sallamar limaninsa hukuncinsa tamkar mai salla shi kaɗai ne.

إذا المسبوق سها بعد سلام الإمام حكمة مثل المصلي وحده .

## : Tasbaha ← مسبحة

Ko wannensu yana riƙe da doguwar tasbaha yana ja.

كل منهم يمسك مسبحة يشد ــ في حباتها ــ

Da zuwana na sami wata doguwar tasbaha a kan hanya.

عند حضوري وجدت مسبحة طويلة على الطريق .

Suja suka yi ta zuba masa harsashi bai kula ba sai tasbharsa yake ja.

أخذ الجنود يصبون عليه الرصاص فلم يهتم وأخذ يشد حبات مسبحته .

## : Mustahabbi ← مستحب

Yin asuwaki mustahabbi ne. استعمال السواك مستحب .

Wankan idi biyu mustahabbi ne. غُسْل العيدين مستحب .

Mustahabban alwalla su ne , farawa da bismilla yin amfani da asuwaki. مستحبات الوضوء هي ، البدأ بالبسملة والإستفادة من السواك .



www.alkottob.com

## : Masafarta ← مَسْفَر

تعني السوق الكبير الذي يسافر إليه التجار للبيع والشراء أو المسافر أو مكان السفر

Ya sauka a wani babban gari ana kiransa Kano, garin kuwa masafarta ne Ƙwarai.

نزلوا في مدينة كبيرة يقال لها كنو ، والمدينة بها سوق كبير .

Masafarta sun yi asara Ƙwarai da gaske.

المسافرون خسروا كثيرا جدا .

Jos masafarta ta ce.

جوس مكان سفري .

## : Miskini ← مسكين

Miskini shi ne mutumin da bai mallaki abincin kwana guda.

المسكين هو الرجل الذي لا يملك قوت يومة .

Sai ya ciyad da misakinai sittin.

يجب أن يطعم ستين مسكينا .

Zai fanshi kansa da yin azumin kwana uku ko ciyad da miskinai shida.

يفدى نفسة بصيام ثلاثة أيام أو إطعام ستة مساكين .

Kaffararsa ita ce ciyad da musakai sittin.

كفارته إطعام ستين مسكينا .

## : Musulmi ← مسلم

Ga shi musulmi amma zuciyarsa kamar ta kafiri don rashin imani.

ها هو مسلم ولكن قلبه كقلب الكافر لعدم الإيمان .

Abin da aka sani ga ɗan musulmi kowace masiba ta dame shi ya riƘa dangana.

ما يُعرف عن المسلم أن كل مصيبة تصيبة يصبر دائما .

Kafin kwana uku musulmai sun shiga uku.

قبل ثلاثة أيام وقع المسلمون في مشكلة .

Na tsugunta wa wani sarki don ya musuluntad da ni.

جلست إلى أمير لأعلن إسلامي .

Duk na musuluntad da su.

الكل جعلتهم يسلمون .



www.alkottob.com

Nan take muka musulunta. في الحال أسلمنا .

Mu nemi cikawa da imani cikin musulunci.

نسأل الله أن يميتنا على الإيمان والإسلام .

Mun kuwa musulunta mun bi Allah mun bi ka sarkin musulunci.

أسلمنا واتبعنا الله واتبعناك أمير الإسلام .

## : Musinnah ← مُسِنَّةٌ

Musinnah ita ce saniya 'yar shekara huɗu.

المسنة هي البقرة ابنة أربع سنوات .

Idan yawansu ya kai arba'in sa'an nan za'a ba da musinnah.

إذا بلغ عددهم أربعين يُعطى مسنةٌ .

## : Masha'a ← ماشاء

Ba su yin kome sai masha'a. لا يفعل إلا ماشاء .

Ba zai yi masha'a da ita. لا يفعل ماشاء بها .

Masha'a llahu. ماشاء الله .

## : Mushtarika ← مشتركة

Wannan shi ne raban da ake cewa da ita mushtarika.

هذا هو الميراث الذي يقال له مشترك .

Dan'uwa na wajen uba kamar shaƙiƙi ne a wajen rashin shaƙiƙi sai ga mushtaraki kurum. الأخ للأب كالشقيق في عدم الشقيق إلا في المشتركة .

## : Mushiriki ← مُشْرِك

Ba a samu mushiriki a Makka. لا يوجد مشرك بمكة .

Mushiriki ya musulunta. المشرك أسلم .



www.alkottob.com

Ana hana salla wajen binne mushrikai da wuraren ibadarsu.

تحرم الصلاة في مدفن المشركين وأماكن عبادتهم .

## : Masha'ari ← مَشْعَر

Zai tsaya a Masha'aril Harami a wannan rana.

يقف عند المشعر الحرام في هذا اليوم .

Na yi salla a Masha'aril Harami raka'a biyu.

صليت ركعتين عند المشعر الحرام .

In ka zo Masha'aril Harami ka tsaya ka ambaci Allah a guri.

إذا جئت المشعر الحرام قف واذكر الله عنده .

## : Mashaguli ← مشغول

Kar ka zama mashaguli a bisa neman kuɗi ka barAllah.

لا تكن مشغولا بطلب المال وتترك الله .

Malamina ya zama mashaguli a bisa bautar Allah.

أستاذي مشغول بعبادة الله .

Musa yanzu ba mashaguli ba ne tun da ya gama jarrabawa.

موسى الآن ليس مشغولا منذ أنهي الإختبار .

## : Mashahuri ← مشهور

A garin nan dai babu wani mashahuri sai Ahmadu.

في هذه المدينة لا يوجد أحد مشهور إلا أحمد .

Ya ba shi damar zama tare da mashahurin baturen nan ne.

أعطاه فرصة الجلوس مع هذا الأوربي المشهور .

Wannan sana'a ta sa Ingila ta zama mashahuriyar ƙasa a cikin duniya wajen ciniki.

هذه الصناعة جعلت انجلترا تصير بلداً مشهورا في العالم في هذه التجارة .



www.alkottob.com

Su biyu suka zama mashahuran barayi a Ikko da kuma a Ƙetare.

هما الإثنان صارا لصّين مشهورين في ليجوس وما حولها .

: **Masifa** ← مصيبة

تأتي بمعنى مصيبة أو مرض

Allah ya sauƙaƙe musu wannan masifa. خفّف الله عنهم هذه المصيبة .

Babu wata masifar da take samunka a cikin halartar wadannan wurare. لا تصيبك مصيبة في حضور هذه الأماكن .

Masifa ta halakad da sulusin 'ya'yan itacen.

أهلك الوباء ثلث ثمار الأشجار.

Na roƙe Allah ya tsamad da ni daga cikin wadannan masifu.

أدعو الله أن ينقذني من هذه المصائب .

: **Musuhafi** ← مصحف

Babu laifi da azurfa cikin adon takobi da musuhafi.

لا بأس من الفضة في حلية السيف والمصحف .

: **Musafaha** ← مصافحة

Suka yi musafaha da sarki. صاحفوا الأمير .

Musafaha tana ƙara ƙauna a tsakanin jama'a.

المصافحة تزيد الحب بين الناس .

Kar ka yi musafaha da mata. لاتصافح النساء .

: **Masallaci** ← مصلى

Ya gina masallacin juma'a wanda ba kamarsa.

بني مصلى للجمعة لا مثيل له .



www.alkottob.com

Ya tafi babban masallacin garin ya yi addu'a.

ذهب إلى مصلى المدينة الكبير ودعا .

Ya gina masallaci da kyau siffarsa ɗaya da na Zariya.

بني مسجدا جميلا شكلة مثل مسجد زاريا .

Siffar masallatan nan yana da ma'ana ƙwarai.

شكل المساجد هنا له معني كبير .

## مصلحة ← Masalaha :

Ya ƙoƙarin aiki a bisa masalahar musulmi. يجتهد في عمل المصلحة للمسلمين.

Kar ka cuci wani don neman masalahar kanka.

لا تضر أحدا لتنال مصلحة لنفسك .

## مصنع ← Masana'i :

Na gina masana'antar tubali. بنيت مصنعا للطوب .

Masana'antar ɗaya ce a garimmu. مصنع واحد في مدينتنا .

Akwai masana'antar iri uku. توجد ثلاثة مصانع مختلفة .

## مُوضِحَة ← Muliha :

Muliha ita ce abin da ya kwaranye ƙashi. الموضحة ما أوضح العظم .

Ga muliha za a ba da raƙumi biyar. في الموضحة يُعطى خمسة إبل .

## معجزة ← Mu'ujiza :

Labarin shaihu da mu'jizarsa sai mu gaya wa wani ba wani ya gaya mana ba. قصة الشيخ ومعجزته نقولها للناس وليس الناس هم الذي يقولونها لنا .

Tsagewar wata tana daga cikin mu'ujizar Annabi.

انشقاق القمر من معجزات النبي ﷺ .



www.alkottob.com

Mu'ujiza kebantacciya ce ga annabawa kawai. المعجزة خاصة بالأنبياء فقط .

Mu'ujuzojin Annabi suna da yawa. معجزات النبي (ﷺ) كثيرة .

## معروف ← Ma'arufi :

Mahaifina ma'arufi ne a cikin garimmu. والدي معروف في مدينتنا .

Musa malami ne ma'arufi. موسى أستاذ معروف .

Mutumin kirki ba ya mantawa da ma'arufin da ka yi masa.
الإنسان الطيب لا ينسي الذي يُقَدَّم إليه .

## مُعَلِّم ← Malami أو Mu'allim :

تأتي بمعنى عالم أو منجم

Wani malami ya sauka gidana. معلم نزل في بيتي .

Mu je gun malam mai salati a daura auren.
لنذهب إلى عالم صالح ليعقد لنا الزواج .

Da assalatun fari ya aika aka kira masa wani malamin Ƙasa.
في الصباح الباكر بعث ــ من ــ يستدعي له مُنَجِّماً .

Sarki ba abin da yake bukata kamar mashahuran malamai.
الأمير لا يحتاج شيئا مثل العلماء المشهورين .

A lokacin nan yana malanta ne a Katsina. فيهذا الوقتكان يُعَلِّم فيكتسينا.

Ni za'a ba malanta domin duk makircin mutane ba wanda ban sani ba. أنا الذي سأعلِّم لأن كل مكر الناس أعرفة كلة .

Ya mu'allim ina so in yi maka wata 'yar Ƙaramar tambaya.
يامُعلِّم أريد أن أسألك سؤالا بسيطاً .

Na kuwa gode maka ya mu'allimu. أشكر لك يامُعلِّم .



www.alkottob.com

## : Mu'amala ← معاملة

Ban san abin da ya sa kake ma'amala da waɗannan 'yan iska ba ?
لا أعرف لماذا تتعامل مع هؤلاء الفاسدين ؟
Aƙalla dai ba na yin ma'amala da kai. على الأقل لا أتعامل معك .
Ma'amala da majahulin mutum ba ta da daɗi.
التعامل مع الإنسان المجهول ليس مريحاً .

## : Ma'ana ← مَعْنى

Ina ma'anar wannan labari ? مامعنى هذا الخبر ؟
Labarin muke so kawai masu ban dariya da ma'ana.
القصة التي نريدها مضحكة ولها معني فقط .
Ba ka san ma'anar kalmar ba ? ألا تعرف معنى الكلمة ؟
Akwai bambanci a wajen ma'anonin haddodi.
يوجد خلاف حول معاني الحدود .

## : Mu'ayyana ← مُعَيَّن

Daga farillan salla niyyar salla mu'ayyana da kabbarar harama.
من فرائض الصلاة ينة الصلاة المعينة وتكبيرة الإحرام .

## : Magariba ← مَغْرِب

Za'a yi sallar magariba. سيصلي المغرب .
A cikin la'asar ne da magariba sai a taƙaita karatu.
في صلاة العصر والمغرب تُقصَّر القراءة .
Magariba na yi ya tafi masallaci. حان المغرب فذهب إلى المسجد .
Ya zauna nan har magariba na yi. جلس هنا حتى حان المغرب .



www.alkottob.com

## : Muhuti ← مُفْتي

An naɗa ni muhutin garimmu. — عُيِّنْت مفتي مدينتنا .

Muhiti ya zo ya raba mana gadommu. — جاء المفتي ليقسم ميراثنا .

An tuɓe Musa daga aikin muhuti. — خُلِعَ موسى من عمل المفتي .

## : Maƙabarata ← مقبرة

تأتي بمعنى المقابر

Ya tafi maƙabarata ya sami wani sabon kabari , ya tone ya jefa ya mai da ƙasa. — ذهب إلى المقابر وبحث عن قبر جديد ، وحفرة وألقاه وهال التراب .

Ginin masallaci a maƙabarta haramun. — بناء المسجد على المقابر حرام .

Maƙabartammu ta cika. — مقبرتنا امتلأت .

## : Maƙabuli ← مقبول

تعني العائل

Yana da maƙabuli. — لدية عائل .

Wannan yaron ba shi da maƙabuli. — هذا الولد ليس له عائل .

Rashi maƙabuli hasara ce. — فقد العائل خسارة .

## : Muƙabala ← مقابلة

An yi mini muƙabalar shiga jami'a. — أجريت لي مقابلة لدخول الجامعة .

Ranar jummu'a aka yi mini muƙabalar shiga soja.

يوم الجمعة أجريت لي مقابلة لدخول الجيش .



www.alkottob.com

## مِقْدار ← Mikidari :

تأتي بمعنى مقدار أو قَدر

Bai san mikidarin dukiyar da za'a yi iya wa zakka ba.

لم يُعرف المقدار الذي يستطيع أن يدفع الزكاة عنه .

Baban matarka yana da mikidari mai girma a gare ka.

والد زوجتك له قدر كبير عندك .

Im mutum ya yi sata ya karya mikidarinsa. إذا سرق الإنسان نقص قدرة .

## مقرأة ← Makaranta :

تعني المدرسة

Na wuce gaba har muka zo makaranta. سرت حتى وصلنا إلى المدرسة .

Suka tara 'ya'yansu a makaranta. جمعوا أولادهم في المدرسة .

Aka sa shi a makaranta ya yi karatu. أدخل مدرسة ليتعلم .

## مقرّب ← Mukarrabi :

Wani lokaci mukarrabinka shi yake cutarka.

أحيانا المقرب إليك هو الذي يضرك .

In mukarrabinka ya samu alheri, sai ka ce kai ne ka samu.

إذا نال المقرب إليك الخير ، كأنك أنت الذي نلته .

Mukarrabai don razana har suka kaɗe sarki da sarauniya ba su sani ba. المقربون من شدة الخوف داسوا الأمير والأميرة دون أن يعرفوا .

## ميقات ← Mikati :

An yi umurni da shiga Harami daga mikati.

أمر المسلمون أن يحرموا من الميقات .



www.alkottob.com

Mikatin mutanen Sham da Masar shi ne Jahfatu.

ميقات أهل الشام ومصر هو الجحفة .

Ya wajaba a gare shi ya ɗauki harami daga mikatin kasarsu.

وجب عليه أن يُحرم من ميقات بلدة .

## مقص ← Almakashi :

Ya dauki almakashi ya yi masa 'yar hana salla.

أخذ المقص وعمل له علامة في مقدمة شعرة .

Ya ballo almakashi daga ratayensa ya datsi gashin kansa.

أخذ المقص من جرابه وقص شعر رأسة .

## مقصود ← Makasudi :

تعني هدف أو مطلب

Yanda daga makasudin musulunci zaman lafiya.

من أهداف الإسلام الحياة في سلام .

Babban makasudina a wajen Allah shi ne aljanna.

اكبر مطلب لي من الله هو الجنة .

Ba ni da wani makasudi ya wuce neman gafara.

ليس لدي مطلب يتجاوز طلب المغفرة .

## مَقام ← Makami :

Ya sallace raka'a biyu a Makami Ibrahim. صلي ركعتين في مقام إبراهيم .

Makami Ibrahim kusa da dakin Allah ne. مقام إبراهيم قريب من بيت الله .



www.alkottob.com

: **Mukami** ← مُقام

تأتي بمعنى الإقامة أو المنصب أو المركز

Yana da muƙami shekarunsa kamar talatin.

له إقامة تبلغ حوالي ثلاثين عاماً .

Zan yi amfani da muƙamina don nishadi. سأستفيد من إقامتي للهو .

Aka naɗa shi wannan muƙami. عُيِّن في هذا المنصب .

Allah ya kan kai mutum wani muƙami, wanda shi mutum ɗin bai zato zai samu ba. قد يولي الله الإنسان منصبا هو نفسة لا يظن أنه يتولاة .

Sun zama masu muƙami kamar sauran manya manyan gari.

صاروا أصحاب منصب كباقي كبار المدينة .

: **Makka (al-Mukarramah)** ← مكة (المكرمة)

Suka gamu da wani ayari na alhazai zasu Makkah (al-Mularramah).

التقوا بقافلة للحجاج ذاهبة إلى مكة المكرمة .

Na nemi ilmi a cikin Makkah al-Mukarramah. طلبت العلم في مكة المكرمة .

Makka tana da alfarma a wajen musulumai.

مكة المكرمة لها حرمة لدي المسلمين .

: **Makida** ← مكيدة

Ba shi da wata ta'ada sai ta karanta labarun mata da irin makidansu.

ليس له عادة إلا قراءة قصص النساء ومكيدتهن .

Kafirai kullum suna shirya wa musulunci makida.

الكفار دائما يعدون للمسلمين مكيدة .

Kar ka yi wa ɗan 'uwanka musulumi makida. لاتكيد لأخيك المسلم .

: **Makirci** ← مكر

Na sani wannan makircin mahassada ne. عرفت أن هذا مكر الحاسدين .



www.alkottob.com

Muddin ka dogara gare shi wani makirci na mahaluki duk ba ya ba ka tsoro.

طالما أنك تعتمد على الله ، مكر المخلوق لا يخيفك .

Makirin nan sai ya kada kai.

هذا الماكر نكس رأسة .

Wata makira daga cikin sadakun uban ta rubuta masa takarda.

جارية ماكرة من جواري أبية كتبت له رسالة .

## مكسَّر ← Mukassari :

### تعني عاجز أو مشوَّة

Musa ya zama mukasari.

موسى صار عاجزا .

Ni ba mukassari ba ne.

أنا لست عاجزا .

Taimakon mukassari lada ne.

مساعدة العاجز ثواب .

## مكروة ← Makaruhi :

Yin farauta don nishadi makaruhi ne.

الصيد للهو مكروة .

Yawan aikata makaruhi ya kan ja mutum zuwa aikata haramun.

كثرة عمل المكروة تجر الإنسان عادة إلى الحرام .

Aikata makaruhi ba ya sa a rubuta maka zunubi.

العمل المكره عليه لا يكتب لك اثمة .

## مكفوف ← Makafo أو Makaho :

### تعني الأعمي

Bakin makaho ya sami kamar sule biyar sadaka.

الأعمي الأسود نال حوالي خمس شلنات صدقة .

Allah ya maishe ka makaho.

جعلك الله أعمي .

Babu makafi a cikin garin nan.

لا يوجد عميان في المدينة .



www.alkottob.com

## : Makkana ← مكّن

تعني التأكيد أو التثبيت

yawan muzakara zai sa ka sami makkana wajen rubutar jarrabawa.

كثرة المذاكرة تجعلك تتأكد من الإجابة في الاختبار .

Samun nasara shi ya makkanad da shi a cikin makaranta.

الوصول إلى النجاح هو الذي ثبتة في المدرسة .

Mulki ba ya makkana tare da zalunci.

الملك لا يثبت مع الظلم .

## : Mala'ika ← ملائكة

تعني المفرد «ملاك»

Mala'ikan mutuwa zai karbi rayuka da yardar Allah.

مَلَكُ الموت يأخذ الأرواح بإذن الله .

Ya aika mala'ika gare su.

بعث اليهم ملكاً .

Mala'ikan nan ya dawo a cikin siffar mai ƙusumbi.

هذا الملك عاد في شكل أجدب .

Mala'ika ne , aka aiko su jarraba Ilya.

ملائكة بعثوا ليتحتبروا إلياس .

Akwai ga bayi mala'ika masu suna rubuta ayyukansu.

يوجد ملائكة حفظة على العباد يكتبون أعمالهم .

## : Mulki ← مُلْك

تعني المُلك أو الحكم

Na ga zai sa , mu yi rauni , bisa ga sha'anin mulki.

أري أنه نسيسبب لنا الجراح بسبب المُلك .



www.alkottob.com

Ka gaya mana abin da ka sani cikin sha'anin mulƙi.

قل لنا ما تعرف بشأن المُلك .

Ina roƙo a cikin darajar mulkinka , ka bar ni in yi 'yan kwanaki kadan a nan.

أرجو بعظمة ملكك ، أن تتركني أمكث عدة أيام هنا .

Allah ya dawwami mulkinka. أدام الله ملكك .

Suka miƙa har wani ƙato kogo inda zakin nan yake mulki.

ساروا حتى كهف حيث يحكم هذا الأسد .

Ka yi mulkin dabbobi duk da mutane baki daya.

حكمت الحيوانات والناس جميعا .

Sarauniya ce ka mulkinsu. أميرة تحكمهم .

## : Mallaka ← مَلَّك

Ina so a sani na ba dana Ali duk abin da na mallaka.

أحب أن يُعرف أنني اعطيت ابني عليّ كل ما أملك

Annabi Sulaimanu wanda aka ce ya mallaki mutane da aljannu har da tsuntsaye.

النبي سليمان (عليه السلام) الذي يقال أنه حكم الإنس والجن والطير .

Ka bar karuwan nan ta mallaki kome.

تترك هذه المومس تحكم كل شيء .

Ya zama babban muradinsa ne ya bar garinsa da gidansa da dukan abin da ya mallaka. صار هدفه الكبير أن يترك بلده وبيته وكل ما يملك .

Wani bature a lokacin mulkin mallaka ya sayi gidan nan.

رجل أوربي في عهد الإستعمار اشتري هذا المنزل .

## : Maniyyi ← مَنِيّ

Maniyyi ruwa ne mai izan juna , yana fito yayin babban jin daɗi da jima'i. المني ماء دافق ، يخرج عند اللذة الكبرى والجماع .



www.alkottob.com

Maniyyi bai fito masa ba , babu kome gare shi.

إن لم يخرج المني لاشي عليه .

Wanda ya sami maniyyi busasshe a cikin tufansa , sai ya yi wanka.

من وجد منياً جافا في ثيابة ، يجب أن يغتسل .

## : Mina ← مِنَى

Zai fita zuwa Mina a ranar tarwiya. سيخرج إلى منى في يوم التروية .

Kwana a Mina daren ranar Arafa sunna ce. المبيت فيمنىليلة يومعرفة سنّة .

## : Minbari أو Mumbari ← منبر

Limamin jummu'a ya zauna kan minbari. إمام الجمعة جلس على المنبر .

Da ya isa bai zama ba sai gindin mumbari sai ya zuba kuɗinsa.

عندما وصل لم يتوقف إلا تحت المنبر وصب مالة .

Liman ya hau mumbari. الإمام صعد المنبر .

## : Mangwaro ← مانجو

Zaku sami 'ya'yan itatuwa kamar su lemo zaƙi da mangwaro masu gina jiki.

ستجدون ثمار أشجار مثل الليمون الحلو والمانجو التي تبني الجسم .

Na shuka bushiyar mangwaro a gonata. زرعت شجرة مانجو في حقلى .

Wannan mangwaro yana da zaƙi sosai. هذا المانجو حلو جدًا .

## : Manzari ← منظار

تعني النظارة

Kawo mini manzarina. احضر لي نظارتي .



www.alkottob.com

Wannan manzari ya yi mini girma. هذه النظارة كبيرة عَلَيَّ .

Na sayo manzari baƙi daga kasuwa. اشتريت نظارة سوداء من السوق .

## منافق ← Munafuƙi :

Kai dai munafuƙi ne ka cuce ni. أنت منافق غششتني .

Allah ba ya son munafuƙi wanda ba ya aiki sai ya ga idon wanda ya sa shi.

لا يحب الله المنافق الذي لا يعمل إلا إذا رأي من ولاه .

In hau kan munafuka in yi rawa in yi juyi.

لأركب على المنافقة وأرقص واستدير .

Lalle mutanen Sinari akwai munafukai.

لابد أنه يوجد بين رجال سيناري منافقون .

Duk aka ɗauka sallar da yake yi ta munafunci ce a zuciyarsa kafiri ne.

الجميع اعتبر الصلاة التي يؤديها ، صلاة نفاق ، وهو في قلبة كافر .

## منقلة ← Mangala :

تعني الغبيط الذي يُحمل فيه السماد على ظهر الحمار

Sambo ya kama jakuna ya daura musu mangala ya fita.

أمسك سامبو الحمير ووضع لها المنقلة وخروج .

Na sayo ƙasa mangala biyu. اشتريت منقلتين من التراب .

Wannan mangala ƙatuwa ce. هذه المنقلة كبيرة .

Matar ta kama masa , ya sassauka mangalolin.

مسكت له المرأة وانزّل المناقل .

## مُنَقَّلَة ← Munaƙƙila :

A cikin munaƙƙila kuma akwai raƙuma ɗaya bisa goma da rabin daya bisa goma. وفي المنقلة عشرة إبل ونصف عشر .



www.alkottob.com

Munaƙƙila ita ce abin da shunfidarsa na ƙashi ya tashi , amma ba ta isa zuwa ƙwaƙwalwa.

المنقلة هي ماطار فراشها من العظم ولم تصل إلى الدماغ .

## : Munkari ← مُنْكَر

Ya wajaba gare shi ya kiyaye harshensa daga alfahasha da munkari.

وجب عليه أن يحفظ لسانة من الفحشاء والمنكر .

Ka yi hani ga aikin munkari. إنه عن عمل المنكر .

Aikata munkari yana rage darajar mutum. عمل المنكر ينقص قدر الإنسان .

## : Almajiri ← مهاجر

تعني طالب العلم أو المتسول

Muhawara ta shiga tsakanin malami da almajirinsa.

المحاورة بدأت بين الأستاذ وتلميذة .

Alkali ya yi wa almajirin shari'a. القاضي حكم للطالب .

Ya kira wani amintaccen almajiransa ya nuna masa wurin kudin nan.

نادي أحد تلاميذة الأمناء وأراه مكان المال .

Na ba almajirin sadaka. اعطيت السائل صدقة .

Na gina wa almajirai gida. بنيت منزلا للسائلين .

Na yi almajiranci a cikin Makkah. تتلمذت بمكة المكرمة .

## : Mahadi ← مهدي

A ƙarshen duniya Mahadi zai bayyana.

سيظهر المهدي في نهاية العالم .

Na tafi gidan malam Mahadi. ذهبت إلى منزل الأستاذ مهدي .



www.alkottob.com

**: Mahalaka ← مهلك**

تأتي بمعنى الهلال

Ga shi kwadayin nan ya sa , mun kawo kammu a mahalaka.

ها هو الطمع أوصلنا إلى الهلال .

**: Muhimmi ← مهم**

Ba zan sake yi mata wani muhimmin aiki ba.

لن أعمل لها مرة أخرى أي عمل مهم .

Ja'iru ba shi da muhimmin ɗan 'uwa. جائر ليس له أخ مهم .

Yanzu akwai wani muhimmin abu da zamu iya yi maka.

الأن يوجد شيء مهم استطيع أن أعملة لك .

**: Mutu ← موت**

Ta bude baki kamar ta mutu. فتحت فمها كأنها ماتت .

Su duka biyu suka mutu shi ya sa wannan mahawara.

الأثنان كلاهما مات وهو سبب المحاورة .

Na tabbata dai mutuwa zan yi don yunwa.

تأكدت أنني سأموت من الجوع.

Shi bikin nan na mutuwa ya kan zama sanadin yunwa a cikin Ƙasarsu.

حفل الموت هذا ، يسبب عادة المجاعة في بلدهم .

Ka matad da shi a kan musulunci. أمته على الإسلام .

Babu laifi a sawa mamci riga da rawani. لا بأس أن يقمص الميت ويعمم .

Suna zara likkafani daga cikin matattu. ينزعون الكفن من الأموات .

www.alkottob.com



www.alkottob.com

## موافقة ← Muwafaƙa :

تأتي بمعنى الموافق أو المصادفة أو التوفيق

Aka yi muwafaƙa a cikin dare a bakin wani rafi jama'ata sun sauka.

تصادف أن نزلت جماعتي في الليل على شاطيء النهر .

Idan kuwa ka yi muwafaƙa. إذا وفِّقْت .

Allah yi mana muwafaƙa a bisa dukan al'amurrammu.

وفقنا الله في كل أمورنا .

Shugaban jami'a ya yi muwafaƙa a kan a karbe ni a jami'a.

رئيس الجامعة وافق على قبولي بالجامعة .

## مولد ← Maulidi :

A cikin Rabi'u lawwal ake yin maulidi.

في شهر ربيع الأول يقام مولد النبي ﷺ .

Daren watan maulidi yana barci sai ya yi mafarki.

ليلة شهر المولد كان نائما فرأي رؤيا .

***



www.alkottob.com

# النون

## : Na'in ← ناءٍ

Aka samo kan itace ashirin aka haɗa wuta ka'in da na'in.

أحضروا عشرين من فروع الشجر وأشعلوا نارا كبيرة .

Ya ga hadari ya kama ka'in da na'in. رأي العاصفة هبت في كل مكان .

Kogi ya cika ka'in da na'in. امتلأ النهر تماما .

Wasa ya cika ka'in da na'in. امتلأ الملعب تماما .

Abu ya yi ka'in da na'in. صار الأمر خطيرا .

Hadari ya dauro ka'in da na'in. العاصفة حجبت السماء تماما .

## : Annabi ← نَبِيّ

Tsira da aminci su tabbata ga Muhammadu cikamakin Annabawa.

الصلاة والسلام على محمد خاتم النبيين ﷺ .

Ya riƙa kuma koyi da musu bin sunnan Annabi.

يتعلم دائما من المتبعين لسنّة النبي ﷺ .

Allah ya yi tsira bisa ga Annabi da alayensa.

صلى الله على النبي وآله .

Ya cika aike da gargaɗi da annabici da Muhammadu.

خاتم الرسالة والنذارة والنبوة بمحمدﷺ

Yin mafarki na kirki yanki ne daga yankuna arba'in sa shida na annabici.

الرؤيا الصالحة جزء من ستة وأربعين جزء من النّبوة .



www.alkottob.com

## : **Najasa** ← نجاسة

Idan najasa ta bayyana , sai a wanke mahallinta.

إذا ظهرت النجاسة غُسل محلها .

Ba a yin salla da najasa. — لا يُصلي بالنجاسة .

Bai canza da najasa ba. — لم يتغيَّر بنجاسة .

Ya yi wanka da ruwan mai najasa. — اغتسل بماء نجس .

## : **Nahisa** ← نَحْس

Ni dai yau cikin nahisa na fito , daga na kama in taimake shi , sai na ga wutsiyar jaki ta cire.

أنا اليوم خرجت في نحس ، عندما أمسكت ــ ذيل الحمار ــ لأساعده رأيت ذيل الحمار ينخلع ــ في يدي ــ

## : **Nahawu** ← نَحْوُ

علم النحو

Sanin nahawu wajibi ne a kan kowane malamin furu'a.

معرفة النحو واجب على كل علماء الفقة .

Na sayo littafin nahawu. — أشتريت كتاب النحو .

Zan yi ƙoƙari in koyi nahawu sosai. — سأحاول تعلم النحو جيدا .

## : **Nadama** ← ندم

Sharuɗɗan tuban yin nadama a kan abin da aka yi.

شروط التوبة الندم على ما فُعِلَ .

Sa'ada aka ɗaure , ya tuna abin da ya yi wa alƙali ya yi nadama.

عندما سجن تذكر ما فعل للقاضي فندم .



www.alkottob.com

Yana ta nadamar dukan muguntar da ya yi tun yana yaro.

ندم كثيرا على كل مافعل من سيئات وهو صبي .

Me ya sa kake yin wannan nadamar ? ما سبب كل هذا الندم ؟

## : Nasaba ← نسب

Kakannin kakannimmu sun haɗa nasaba da tsuntsayen daji.

أجداد أجدادنا يجمعهم النسب مع طيور الغابة .

Nasabar Annabi nasaba ce mai girma. نسب النبي ﷺ نسب العظيم .

Na haɗu da Musa a cikin nasabata ta wajen kakana na biyar.

اجتمع مع موسى في النسب من ناحية جدنا الخامس .

In zaka aure mace ka bincike nasabarta sosai.

إذا كنت ستتزوج المرأة فابحث عن نسبها جيدا .

## : Nishaɗi ← نشاط

### تأتي بمعنى اللهو

Suka zauna suna ta nasu nishaɗi. عاشوا يلهون لهوهم .

Gara fa mu dan nishaɗi. الأفضل أن نلهو قليلا .

Kudi suka yi masa yawa , suke sa shi nishaɗi haka.

المال كثر فجعلة يلهو هكذا .

Da aka yi wani sarki mai son nishadi. قديما كان يعيش ملك مُحِبّ للهو .

Yin farauta don nishadi makaruhi ne. الصيد للهو مكروة .

## : Nassi ← نص

Nassi yake magana a kanta. النص تحدث عنها .

Giya haramun ce da nassin Alƙur'ani. الخمر محرمة بنص القرآن .

Nassin hadisi ya hana auren jin daɗi. نص الحديث يحرم زواج المتعة .



www.alkottob.com

Nassi ya zo a kan halattar auren bakitabiyya.

جاء نص في تحليل زواج الكتابية .

## : Nasiha ← نصيحة

Yana ta godiya bisa ga wannan nasiha. يشكر كثيرا على هذه النصيحة .

Mutanen suka yi mamakin sarki a kan wannan nasiha.

تعجب الناس من الأمير على هذه النصيحة .

Wanda ya yi nasiha kamar haka , ya kamata a je a gode masa.

من ينصح هذه النصيحة ، يجب أن نذهب ونشكرة .

Na yi masa nasiha ɗaya. نصحته نصيحة واحدة .

## : Nasara ← نَصَرَ

Allah ya ba sarki nasara. نصر الله الأمير .

Mai ƙoƙori kullum shi ke da nasara. المجتهد ينتصر دائما .

Allah ya taimake mu , muka samu nasara bisa ga wannan yaƙi.

اللهم ساعدنا لننال النصر في هذه الحرب .

Ya ci nasara wajen gasar neman sarauta.

انتصر في المنافسة على طلب السلطة .

Yana roƙon Allah ya sa ya sami nasara bisa wannan al'amari.

يسأل الله أن يجعله ينال النصر على هذا الأمر .

## : Nasara ← نصارى

تعني المستعمرين الأوربيين

Na ji ana ce nasara na ci mutane. سمعت أنه يقال أن النصارى يأكلون الناس .

Yaƙin da muka yi da nasara tun suna ƙasa har suka zo kurmi.

الحرب التي خضناها مع النصارى ــ المستعمرين ــ منذ وصلوا البلاد حتى جاءوا إلى الغابات .



www.alkottob.com

## : Nusufi ← نصف

Fiye da nusufin mutanen Nijeria musulumi ne.

أكثر من نصف سكان نيجيريا مسلمون .

Ka kawo nusufin kuɗin mota , in cika maka nusufin don ka sayi mota. أحضر نصف ثمن السيارة ، لأكمل لك النصف ـ الأخر ـ لتشتري السيارة .

## : Anna'ashi ← نعش

Yanzu ba saura sai a ɗauko anna'ashi a kai shi.

الآن لم يبق إلا أن نأخذ النعش ونوصلة .

## : Na'am ← نَعَم

تأتي بمعنى الموافقة

Ya ce «Murjanatu» ta ce «na'am Allah ya daukaki mulkinka».

قال «مرجانة» قالت «نعم رفع الله ملكك» .

Na yi na'am da shi. وافقت عليه .

Na yi haka ne , don in sa dukanku ku uku ku yi na'am da batun auren. فعلت ذلك لأجعلكم كلكم الثلاثة توافقون على مسألة الزواج .

## : Ni'ima ← نعمة

تعني النعمة أو الخير أو الخصب

Ya tuna ni'ima tasa a gare shi. يتذكر نعمته عليه .

Sabo da itatuwa ke bushewa don ba laima , icen nan sa'an nan ke ganye don ni'imar damina ke bisa kanta.

لجفاف الأشجار لعدم الرطوبة ، هذه الشجرة تورق لنعمة الفصل المطير عليها .



www.alkottob.com

Duk ni'imomin duniyan nan da Allah ya ba shi su yi masa bakin ciki.

كل نعيم الدنيا هذه ، التي وهبة الله إياها ، تجعلة حزيناً .

Ba ruwan sama balle wata ni'ima ta samu a wurin.

لا مطر ولا أية نعمة توجد في المكان .

Allah ya kai ta wani gari mai ni'ima ba kowa sai mata.

حملها الله إلى مدينة كثيرة الخير ، لا أحد فيها إلا النساء .

Inda zaku je bakin rijiya ko wani lambu ko wani wuri mai ni'ima sai ku ga ƙudajen zuma.

حيثما تذهبون إلى فوهة بئر أو حديقة أو أي مكان خصب ترون النحل .

## ناعورة ← Na'ura :

تعني ماكينة الطحن

Na yiwo nika a na'urar Musa.

طحنت في طاحونة موسى .

Garba ya sayo na'ura sabuwa.

اشتري ابوبكر ناعورة جديدة .

Na'ura ta fi mutum saurin aiki.

الناعورة فاقت الإنسان في سرعة العمل .

## نفاس ← Nifasi :

Yin wanka daga janaba da jinin haila da nifasi farilla ne.

الغسل من الجنابة ودم الحيض والنفاس فريضة .

In jinin nifasi bai dauke ba mace ba ta salla.

إذا لم ينقطع دم النفاس المرأة لا تصلي .

Mace mai nifasi ba ta shiga masallaci.

المرأة النفساء لاتدخل المسجد .

Nifasi da haila su ne abubuwan da suke hana mata salla.

النفاس والحيض هما اللذان يمنعان النساء من الصلاة .



www.alkottob.com

## : Nafila ← نافلة

Maras lafiya yana yin taimama don yin sallar farilla da nafila.
المريض يتيمم لصلاة الفرض والنافلة .
Ba'a yin sallar nafila bayan sallar subahi. لا تُصلي نافلة بعد صلاة الصبح .
Ya yi nafila da raka'a huɗu. تَنَفَّلَ بأربع ركعات .
Akwai sunnani waɗanda suke ƙarfafa da nafifili. توجد سنن مؤكدة ونوافل

## : Naƙasa ← نقص

تأتي بمعنى النقص أو العيب أو الإساءة

Wannan bayani zai naƙasa kuɗinsa. هذا البيان سينقص ثمنة .
Ya ce sai ya biya shi kuɗin jakinsa tun da ya naƙasa shi haka.
قال يجب أن يدفع له ثمن حمارة طالما عابة هكذا .
Sun naƙasa ni. أساءوا إليَّ .
Ina fa lafiya ? ƙatuwar matarka ta naƙasa ni.
أين هي السلامة ؟ زوجتك الضخمة أساءت إليَّ .
Da ya ke yanzu sun zama naƙasassu a yi unguwar dabam cikin birni.
طالما أنهم صاروا مشوهين ، يُبني لهم حي مختلف في المدينة .

## : Naƙalta ← نقل

نقل كلاما

Na nakalce shi wurin Musa. نقلت الكلام عن موسى .
Can ya nakalci wani abu ya ce «Allah ya kyauta maka».
بعد ذلك نقل كلاما وقال «الله يحسن إليك» .
Ya kuma maƙalta masa abubuwan da zasu yi wa Musa.
وقال له الأشياء التي سيفعلها لموسى .



www.alkottob.com

## : Nukura ← نكر

تأتي بمعنى العداوة والحقد

Yana nukura da ni. — يناصبني العداوة .

Yanzu nukura ta yi kanta a tsakanin mutane. — انتشر الحقد بين الناس .

Kada ka yi wa ɗan 'uwanka musulumi nukura. — لا تحقد على أخيك المسلم .

Nukura mummunar ɗabi'a. — الحقد طبيعة سيئة .

## : Annamima ← نميمة

Ya yi hanin aikata abin ƙi da yin ƙarya da giba da annamima.

حرم عليه عمل المنكر والكذاب والغيبة والنميمة .

Annamimi zai iya haddasa yaƙi tsakanin jama'i.

النمام يمكن أن يوقع الحرب بين الناس .

In ka aure annamimiyar mace sai ta raba ka da danginka.

إذا تزوجت المرأة النمامة تفرق بينك وأهلك .

Annamimanci haramun ne. — النميمة حرام .

## : Nahayu ← نهي

Sai amru da nahayu nake yi. — آمر وأنهي .

Na haye bisa gadon sarautar garin sai amru da nahayu.

أعتليت عرش السلطة في المدينة آمر وأنهي .

## : Nihaya ← نهاية

Gaya wa nihaya. — غاية ونهاية .



www.alkottob.com

## نور ← **Annuri** :

Da ganin baƙon nan , sai an ga mutum mai annuri.

عند رؤية هذا الضيف ، ترى رجلا منير ـ الوجة ـ

In ka lura ka ga annuri ya sake , ba kamar na yadda muka baro ba.

إذا نظرت ترى النور قد تغيَّر ، ليس كما تركناه .

## نوع ← **Nau'i** :

Ba zai yiwu a sayi nau'insa da nau'insa ba , sai fa hanuu da hannu.

لا يجوز بيع النوع بنوعة ، إلا إذا كان يدا بيد .

Dukan abin da aka fitar daga cikin naman duk nau'insa ɗaya ne.

كل ما أخرج من اللحم نوع واحد .

## نية ← **Niyya** :

Faɗa da aiki ba su tabbata sai da niyya. القول والعمل لايكملان إلا بالنية .

Shiga cikin salla da niyyar farilla , shi ma farilla ne.

الدخول في الصلاة بنية الفرض ، هو أيضا فريضة .

Faɗi ko aiki ko niyya duk ba su tabbata sai da katarin sunna.

لا يكمل القول أو العمل أو النية إلا بموافقة السُّنة .

Da farko ku dauri niyya , maza ku zo kafin su shirya.

أولا اعقدوا النية ، وبسرعة أحضروا قبل أن يستعدوا .

Na ɗauki niyya na tuba da sane tun watan jiya.

عقدت النية أن أتوب عن النشل منذ الشهر الماضي .

Na yi niyya na tashi sai wani gari. نويت أن أسافر إلى بلد آخر .

***



www.alkottob.com

# الـهاء

## : Hadaya ← هَدْيٌ

Bai yi samun hadaya ba. لم يستطيع تقديم الهدى .
In ka fid da gashi daga jikinka kana halin mai niyya da hajji hadaya ta wajaba a kanka. إذا اقتعلتشعرة منجسمك وأنت تنويالحج وحب الهدى عليك .
Hadaya ba ta halatta sai a cikin Makka. لايجوز الهدى إلا في مكة المكرمة .
Na yi hadaya da rago. ذبحت الهدى خروفاً .

## : Haka ← هكذا

تأتي بمعنى ذلك

Sun dinga yin haka har kwana bakwai..
استمروا في عمل ذلك حتى سبعة أيام
Matarsa kullum tana fama da shi a kan haka. دائما زوجته تعانيمعة منذلك .
Haka Ƙaddara Allah. هكذا قدر الله .
Da ma ina shakkar haka. لقد كنت أشك في ذلك .

## : Hala ← هَلّا

Hala ba ka san inda ka zo ba ? هلّا عرفت أين جئت ؟
Hala akwai labari mai daɗi. هلّا يوجد خير ممتع ؟
Ya tambayi jakadiya me ya faru halla ta haihu ?
سأل الجارية ماذا حدث هلّا ولدت ؟
Haka ka sami abin da ka cika cikinka ? هلا وجدت ما يملأ بطنك ؟



www.alkottob.com

## : Halaka ← هلك

Alƙur'ani bai zamo halitacce ba balle ya halaka. القرآن ليس مخلوقا فيهلك .
Ya halaka a hannun amini. هلك في يد أمين .
Ya halaka kafin shekara biyu. هلك قبل عامين .
Masifa ta halakad da sulusin 'ya'yan itacen.
المصيبة أهلكت ثلث ثمار الأشجار .
Ka fidda ni daga halaka. أخرجني من الهلاك .
In ka hakala mun halaka mun kuma faɗa a hannun kafirai.
إذا هلكتَ هلكنا ، وسقطنا في يد الكفار .

## : Himma ← همة

تعني الهمة أو النشاط

Idan iyayenka ko malamanka suka aike ka yi himma.
إذا والداك أو أساتذتك أرسلوك فكن نشيطا .
Bera kuma ya sake ta da himma. نشط الفأر مرة أخرى .
Tana yi masa waƙa wai don ya ƙara himma ga aikin da na sa shi.
تغنى له ليزداد همة في العمل الذي كلفته به .
Da mijin ya shigo ya ganta ta himmatu cikin saƙa , amma ba zare ba dalilinsa. عندما دخل الزوج رآها تهمّ في النسج ، ولكن لا خيط ولا أثرة .
Ya ƙara ƙarfafa mana zuciya da himmantuwa. زاد قلبنا قوة وهمة .
Sabo da alherin nan da ka yi mini , shi ya sa na ƙara himmantuwa ga taimakonka. الخير الذي أسدية إليَّ ، هو الذي جعلني ازداد همة في مساعدتك .

## : Hani'an ← هنيئاً

Ya sami dukiyar mahaifinsa yana ci hani'an.
نال ثروة والدة ويستمتع بها هنيئاً .



www.alkottob.com

Im mutum ya ba ka kyautar kuɗi sai ka karɓe su ka ci su hani'an.

إذا أعطاك إنسان هدية من المال فخذها واستمتع بها هنيئاً .

In Allah ya shigar da kai aljanna , zaka ci kome hami'an ba da wahala ba.

إذا أدخلك الله الجنة ستستمتع بكل شيء هنيئا بلا تعب .

## هواء ← Hawa :

Ya ce musu kafin wata guda su gina masa gida cikin hawa.

قال لهم قبل شهر واحد يبنون له بيتا في الهواء .

## هاوية ← Hawiya :

Karuwa ko ta tuba ko ta shiga wutar Hawiya.

المومس إما أن تتوب وإما أن تدخل النار .

Ba mai shiga Hawiya sai wanda Allah ya sa yi masa azaba.

لا يدخل الهاوية إلا من شاء الله له العذاب .

Allah ka nisanta mu daga wutar Hawiya. — اللهم ابعدنا عن النار .

## هيبة ← Haiba :

Sarkin Kano da haiba yake. — أمير كنو له هيبة .

Na aure mata mai haiba. — تزوجت امرأة محترمة .

Zalunci yana rage haibar shugaba. — الظلم ينقص هيبة الرئيس .

★★★



www.alkottob.com

# الـواو

## وتر ← Witiri أو Wutiri :

Wanda ya sallar isha'i sai ya tashi ya yi sallar shafa'i da wutiri.

من صلي العشاء يجب أن يقوم ويصلي الشفع والوتر .

Sai ya sallaci shafa'i da witiri a fili. ثم يصلي الشفع والوتر جهراً .

Ya sallaci witiri raka'a ɗaya. صلي الوتر ركعة واحدة .

Yin wutiri sunna ce wajiba. صلاة الوتر سنَّة واجبة .

## وثيقة ← Wasiƙa :

تأتي بمعنى رسالة

Zan sake rubuto maka wasiƙa. سأكتب لك رسالة أخرى .

Audu ya yi wa Musa wasiƙa biyu. كتب عبده لموسى رسالتين .

Wasiƙa zaki yi , kike neman warƙa ? هل ستكتبين رسالة تطلبين ورقة ؟

Yanzu ba abin da ya fi , sai ka shiga ka yiwo mini 'uar wasiƙa shaida.

الآن ليس أفضل من أن تدخل وتكتب لي وثيقة كشاهد .

Ba kuwa fasinja da 'yan kayansu kawai jirgin sama ke ɗauka ba , har da wasiƙu da jaridu.

ليس المسافرين وأمتعتهم القليلة فقط تحملها الطائرات ، ولكن الرسائل والصحف .

## وجب ← Wajaba :

Abin da ya wajaba ga baligi , shi ne inganta imaninsa.

ما وجب على البالغ هو تصحيح إيمانة .



www.alkottob.com

Ya wajaba gare shi ya kiyaye haddodin Allah.

وجب عليه أن يحافظ على حدود الله .

Ya wajaba a sanasshe su abubuwan da Allah ya faralta daga aiki ko ƙauli.

وجب أن نعلهم ما فرض الله من عمل وقول .

## : Wajibi ← واجب

In ya zama fasiƙi ne , to a nan fa wajibi ne ma a ƙaurace masa.

إن صار فاسقا في هذه الحالة واجب هجرانة .

Wajibi ne a tsettsefe yatsun hannuwa. واجب تخليل أصابع اليد .

Wanda ya yi kokanta a cikin kari , to , wajibi ne ya sake alwalla.

من شك في حدث ، واجب عليه إعادة الوضوء .

## : Wahala ← وحل

تأتي بمعنى مشكلة أو صعوبة أو تعب

Kome wahala , kome hatsari kada ka yanke ƙauna ga Allah.

مهما كانت الصعاب ، ومهما كانت الأخطار لا تقطع الرجاء في الله .

Ga hadari da wahala sa'an nan in koma hannun wofi.

ها الأخطار والصعاب ثم أعود خالي اليد .

Idan ka faɗa mini gaskiya ba ka wahalad da shari'a ba , ba zan ɗaure ka ba. إذا قلت الحقيقة لن تتعب القضاء ، ولن تُسجن .

Kada ki ƙara wahalad da kanki a banza. لا تتبعي نفسك عبثا .

## : Wadiyyi ← ودي

Karuruwa su ne bawali da bayan gida da iska da maziyyi da wadiyyi.

الأحداث هي البول والغائط والريح والمذي والودي .



www.alkottob.com

Wadiyyi shi ruwa ne fari mai kauri yana fita a ƙarshen fitsari.

الودي هو ماء أبيض خاثر يخرج إثر البول .

Abin da ya wajaba ga fitsari , yana wajaba gare wadiyyi.

ما يجب بالنسبة للبول يجب بالنسبة للودي .

## : Warabbuka ← وربك

Musa dai ya suki jikinsa yana zaman tsammanin warabbuka.

اطمأن موسى إلى الاقامة وظن أن الله وهبة كل شيء .

## : Wuridi أو Wurdi ← وِرْد

Ba'a yi bayan sallar alfijiri sai fa wani wurdi.

لا يُؤدي بعد صلاة الفجر إلا الوِرد .

Ya kama wuridi har can da asuba. مسك الورد ـــ قراءة ـــ حتى بعد الصبح .

Ya shiga ya gani wane irin wuridi ya kama har yanzu bai gama ba.

دخل فرأي ورداً فأمسكة حتى الآن لم ينته .

Yana wuridi sai ka ce wani mai rauhani. يقرأ الورد كأنه رجل روحاني .

Na kwana ina wuridi ina roƙon Allah ya taimake mu.

قضيت الليل أقرأ الورد وأسأ الله أن يساعدنا .

Na yi 'yan wurudda na gama na koma gida.

قرأت بعض الأوراد وانتهيت وعدت إلى المنزل .

## : Wardi ← وَرْد

Akwai kwalabar turare wardi a rataye. توجد زجاجة رائحة ورد معلقة .

Ta koke kamar furen wardi wanda tsutsa ta yi wa ta'adi.

حكَّت مثل وردة الورد التي تعدي عليها السوس .

Turaren wardi tsada ne da shi. رائحة الورد غالية .

Matata ta ba ni kyautar turaren wardi. زوجتي أعطتني هدية عطر الورد .



www.alkottob.com

## : Warƙa ← ورقة

'Yar warƙa nake so. أريد ورقة صغيرة .

Wasiƙa zaki yi , kike neman warƙa ? ستكتبين رسالة تطلبين ورقة ؟

Shaihu Mas'ud ya zo da waɗansu takardu warƙa biyu na Alƙur'ani ya ba ni in karanta. الشيخ مسعود جاء ببعض الأوراق ، وورقتين من القرآن لأقرأ .

## : Waziri ← وزير

Waziri ya ce Allah ya ba ka nasara. قال الوزير وهبك الله النصر .

Don ya yi haka sai ya naɗa shi waziri. لأنه فعل ذلك عينة وزيرا .

Waziri ya ce subbana lillahi. قال الوزير سبحان الله .

Ya sa shi ya yi waziricin mutane. جعلة وزيرا للناس .

## : Wusɗa ← وسطى

Sallar asuba ita ce sallar wusda. صلاة الصبح هي الصلاة الوسطى .

## : Wuswasi ← وسواس

Ya halicci mutum , kuma ya san abin da ke wuswasi da shi.
خلق الإنسان ويعلم ما توسوس به نفسه .

In ya zama mai yawan wuswasi ne , to , babu kome a kansa.
إذا صار كثير الوسواس لا شيء عليه .

Ya yi ta wuswasi wannan abu cikin ransa. وسوس بهذا الأمر في نفسة .

## : Wasiyyi ← وِصِيّ

Wasiyyi wasiyyi kamar wasiyyi ne. وصي الوصي كالوصي .



www.alkottob.com

## وصية ← Wasicci أو Wasiyya :

Babu yin wasicci ga mai cin gade. لا وصية لوارث .

Aka yi masa wasicci da shi. عمل له وصية به .

Ya yi wasicci ga mutumin da ba amintacce ba. . عمل وصية لرجل غير أمين

Ya yi kuka mai zafi sabo da rashin samun ikon jin wasiyyar tsohonsa.

بكي بكاء حارا لعدم وجود القدرة لسماع وصية أبية .

Bai bar masa wata wasiyya zuwa ga ubansa ba. لم يترك لهوصية إلىوالدة.

## وضوء ← Alwalla :

Ya ɗauki buta a masallaci, ya yi alwalla ya shigo ya yi salla.

أخذ الإبريق إلى المصلى ، وتوضأ ودخل وصلى .

Ya nemi ruwa ƙasa da bisa , ya yi alwalla ya rasa.

طلب الماء في كل مكان ، ليتوضأ فلم يجد .

Ya tashi ya yi alwalla , ya yi salla , ya ɗauki tasbaharsa , ya shiga salati.

قام وتوضأ ، وصلي ، وأخذ مسبحته ، وبدأ يصلي على النبي ﷺ .

## وطر ← Waɗari :

Abin da muke jira , mu ji kuma mu gani , shi ne irin yadda za'a yi wadari wata rana da ransa.

ما ننتظرة هو أن نسمع ونرى ، كيف ينسج ذات يوم وهو حيٌّ .

## وعد ← Wa'adi :

Zan ɗeban masa wa'adi im bai kawo ba sa'an nan in daure shi.

سأطلب منه وعدا ، إن لم يُحضر ، أسجنة .



www.alkottob.com

Ran nan wa'adin da sarki ya diba wa Musa na kwana hudu ya cika.

اليوم الوعد الذي قطعة الأمير لموسى بأربعة أيام انتهي .

Ba a yin ciniki a kan wa'adin da ba a sani ba.

لا يباع شيء إلى وعد ــ أجل ــ غير معروف .

## وعظ ← Wa'azi :

Ba zai iya yi masa wa'azi ba. لن يستطيع وعظة .

Mu ba mu son wa'azi labarai muke so kawai. لا نريد وعظا ، نريد قصصا فقط .

Ina karantad da su , sai wa'azi da hadisi nake bayarwa safe da rana.

أعلمهم الوعظ والحديث صباحا ونهارا .

Yana wa'azi ga jama'a. يعظ الناس .

Suna bi gari gari suna wa'azi. يطوفون المدن يعظون .

Na tashi ina bin gari , ina wa'azi har safe.

قمت أطوف المدينة أعظ حتى الصباح .

## وِقْف ← Waƙafi :

تعني علامة الوقف في القرآن أو مكان حجز المتهمين

Ya yi ta zuba labaru , ba ya ko waƙafi balle aya.

أخذ يقص القصص لايقف في وقف ولا آية أي باستمرار .

Sarki ya aika aka sallame mutanen nan da ke waƙafi.

بعث الأمير ليُخرج الناس الموقوفون أي المحجوزون .

Ya sa aka kai wanii ƙaton akwati aka ajiye a babban ɗaki a gidan waƙafi. أمر أن يُحمل صندوق كبير ، ويوضع في حجرة كبيرة في بيت الوقف .

Tun da ba su saci kome ba sai a mai da su gidan waƙafi.

طالما لم يسرقوا شيئا يوضعون في الحجز .

Tafi da su gidan waƙafi sai gobe. إذهب بهم إلى الحجز حتى الغد .



www.alkottob.com

### : **Wakili** ← وكيل

Kai ne wakilina a cikin iyali. أنت الوكيل في الأهل .

Da wakilin gari ya ga haka , ya ce in hawo maza in gaya maka.

عندما رأى وكيل المدينة ذلك ، أمرني أن أركب بسرعة وأقول لك .

Ya naɗa ni wakilin gari. عينني وكيلا للمدينة .

Bai zama ko ina ba sai fada , ya kai wa wakili takarda.

لم يتوقف في أي مكان إلا في القصر ، وأوصل إلى الوكيل الرسالة .

### : **Wakilta** ← وَكَّلَ

Yanzu ina so ka wakilce ni a ɗaura aure.

الآن أريد أن توكلني في عقد الزواج .

Ya ce na mayar maka abin da ka wakilta ni a kai.

قال رددت إليك ما وكلتني عليه .

### : **Walicci** ← ولاء

Walicci yana ga wanda ya 'yanta. الولاء لمن أعتق .

Wanda ya 'yanta bawa a mainmakon wani mutum , to , waliccin yana ga mutumin. من أعتق عبدا عن رجل فالولاء للرجل .

### : **Wa'iyazu billahi** ← والعياذ بالله

Sarkin ya ce «wa'iyazu billahi , Allah ya kyashe mu sana'ar sata».

قال الأمير «والعياذ بالله وقانا الله حرفة السرقة».

### : **Wallahi** ← والله

Wallahi tallahi ƙarya ne. والله تالله كَذِبٌ .



www.alkottob.com

Ni wallahi ko da ba ni da allo , na fi shi iyawa.

والله رغم أنني لا أملك لوحاً أفوقة قراءة .

## : Wali ← والي

Suka ɗunguma wajen wali don ya raba musu gardama.

ذهبوا إلى الوالي ليفصل بينهم في النزاع .

An nada Musa walin Kano. — عين موسى والي لكنو .

Wali ya ba ni kyautar doki. — الوالي أعطاني حصانا هدية .

## : Waliyyi ← وَلِيّ

Aure ba zai yiwu ba sai da waliyyi. — الزواج لا يتم إلا بولي .

Ba za'a aurad da mace ba sai tare da izinin waliyyinta.

لا تزوج المرأة إلا بأذن وليّها .

## : Walima ← وليمة

An yi kiranka zuwa wata walima. — دُعيت إلى وليمة .

An kawo abinci mai yawa a wajen walima. — أُحْضِر طعام كثير إلى الوليمة .

An gayyace ni walimar biki. — دُعِيت إلى وليمة عرس .

Ba ni da kuɗin da zan shiryu walima. — ليس لدي المال الذي أعد به وليمة .

★★★



www.alkottob.com

# اليـاء

**:Ya ← يا**

تستعمل أداة للنداء

Ya Allah ka kyashe mu da aikin jahilci. يا الله قنا عمل الجهل .

Ya Allah ka yi mana gafara. يا الله اغفر لنا .

Za'a sa ku aljanna ku duka domin adalacin ka ya sarki.

ستُدْخلون الجنة كلكم بسبب عدالتك يا أمير .

**: Ya'juju ← يأجوج**

Ya'juju wa Ma'juju zasu bayyana a ƙarshen duniya.

يأجوج ومأجوج سيظهران في نهاية العالم .

Ya'juju wa Ma'juju halitta ce wace ba wanda ya taba ganin a cikimmu. يأجوج ومأجوج مخلوقان لم يرهما أحد منّاً .

**: Yasimin ← ياسمين**

Na sayi kwalabar turaren yasimin. اشتريت زجاجة من عطر الياسمين .

In ka shafa turaren yasimin tun da ka nesa za'a ji ƙanshinsa.

إذا تعطرت بعطر الياسمين تُشم رائحة من بعيد .

Yasimin turaren masu mulki. الياسمين عطر الأثرياء .

**: Yau ← يوم**

Yau kyanwa ta mutu duniya ta yi daɗi.

اليوم ماتت القطة وأصبحت الحياة جميلة .



www.alkottob.com

Daga yau kada ka sake barin kaya haka a kan hanya.

بعد اليوم لاتترك مرة أخرى المتاع هكذا على الطريق .

Yau ina ga ta gafarta mini ne.

اليوم أري أنها غفرت لي .

★★★



www.alkottob.com

## صدر للباحث :

١ ــ الإبدال الصوتي في الكلمات العربية في لغة الهوسا ، مجلة مجمع اللغة العربية ، العدد ٤٢ ، القاهرة .
٢ ــ الإلصاق الصوتي في الكلمات العربية المقترضة في لغة الهوسا ، مجلة مجمع اللغة العربية العدد ٤٤ ، القاهرة .
٣ ــ مصادر الإقتراض ، دراسة للكلمات العربية في لغة الهوسا ، مجلة مجمع اللغة العرية ، العدد ٤٦ ، القاهرة .
٤ ــ الحركة الأخيرة ، دراسة للكلمات العربية في لغة الهوسا ، مجلة مجمع اللغة العربية العدد ٤٨ ، القاهرة .
٥ ــ الحذف الصوتي في الكلمات العربية في لغة الهوسا ، مجلة الدراسات الأفريقية ،العدد ٧ ، القاهرة .
٦ ــ أداة التعريف في الكلمات العربية المقترضة في لغة الهوسا ، مجلة الدراسات الأفريقية ،العدد ٨ ، القاهرة .
٧ ــ العبارات العربية المقترضة في لغة الهوسا ، مجلة الدراسات الأفريقية ،العدد ٩ ، القاهرة .
٨ ــ الهوسا لغة وشعبا ، مجلة الفيصل ، العدد ٩١ .
٩ ــ العربية والهوسا ،نظرات تقابلية ، سلسلة دراسات في تعليم اللغة العربية لغير الناطقين بها ، معهد اللغة العربية ، جامعة أم القرى.

**١٠ــ معجم سياقي للكلمات العربية في لغة الهوسا ، سلسلة دراسات في تعليم اللغة العربية لغير الناطقين بها ــ معهد اللغة العربية ــ جامعة أم القرى .**

## تحت النشر :

١ ــ دراسة دلالية للكلمات العربية في لغة الهوسا ، مجلة مجمع اللغة العربية ، القاهرة .
٢ ــ الأثر العربي في الأمثال الهوساوية ، مجلة مجمع اللغة العربية ، القاهرة .
٣ ــ ظواهر صرفية مشتركة بين العربية والهوسا ، مجلة مجمع اللغة العربية ،القاهرة .
٤ ــ دلالات مشتركة بين العربية والهوسا ، مجلة مجمع اللغة العربية ، القاهرة .
٥ ــ معجم الأمثال الهوساوية ، ومقابلها بالعربية .
٦ ــ الأثر العربي في الأدب الهوساوي .



www.alkottob.com